BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM

HAKKIN MALLAKA

©Batul Mamman

November 2019

GODIYA

Dukkan yabo da godiya sun tabbata ga ALLAH SWT Sarkin da Ya bani ikon rubuta wannan labari. Abinda yake mai amfani ina fata Allah Ya bamu ikon aiki da shi. Wanda yake kuskure daga gareni ne kuma ina rokon Allah Ya yafe min. Amin.

GARGADI

Wannan labari da duka abinda ya kunsa mallakar BATUL MAMMAN ne. Ban yarda wani ko wata ya juya min ko da shafi daya ne ba tare da izini ba. Sannan ban yarda a yada wannan labari ta kowace siga ba ta kafofin sada zumunta, bugawa ko karantawa ba. Sabawa hakan zai janyo daukar matakin shari'a akan duk wanda aka samu da laifi. Nagode.

JINJINA

Ga daukacin matan Fikra Writer's Association. Allah Ya kara hada kanmu Ya sada mu da alkhairin zaman tare. Ba zan manta daku ba domin kun cancanci dukkan yabo matan KDM da na SSS baki dayanku ina gaisuwa tare da fatan Allah Ya barmu tare.

GAISUWA TA MUSAMMAN

Duk wadda ta taba karanta littafin Batul Mamman a duk inda take ina mika gaisuwata a gareta tare da fatan alkhairi. Dole na ambaci wasu daga cikinku ba don sauran basu cancanta ba sai dai don kuna da yawa.

Rumanatu Bashir Abubakar

Shafa'atu Aminu

Massouda Moulaye

Sumayya Abdulkadir (Takori)

Anti Salaha A.A Zaria

Aisha Abdu Gusau

Halima Usman (Siyama)

Jamila Ahmad (Meela Adeel)

Zuwaira Sulaiman

Maryam AD Baffa

Zainab Yahaya

Sai kuma wadanda suka bada gudunmawa ta gyara rubutu (editing) Hassana Isma’il Matazu da bada shawarwari game da abinda ya shafi shari’a Hafsa Kamal Ibrahim. Allah Ya saka da alhairi.

Wata mace ce take kai kawo tsakanin falo da ɗaki cike da tashin hankali da fargabar abin da zai faru a yammacin yau ɗin. Yawan tunaninta da matsuwar son jin kyakykyawan labari daga Fanna ya yi mata yawan da ya haddasa mata ciwon kai na bari ɗaya. Kusan wata biyu kenan tana shirin da take fatan yiwuwarsa domin cimma ƙudurinta. Kuma nan da lokaci ƙanƙani ɗayan biyu zai faru, samun biyan buƙatar da zai zama mataki na farko wurin cikar burin nata ko kuma tonuwar asirin da zai janyo lalacewar komai. Tunowa ta yi da cewa Fanna bata da zaɓin da ya wuce yi mata biyayya ta samu kanta da sakin gajeren murmushi wanda ya kasance ɗabi'arta idan ta jiyo ƙamshin nasara. Duk da haka zama ya gagareta saboda rashin nutsuwa ta kalli agogon bango na rantsattsen gwal ɗin da yake ɗaure a tsintsiyar hannunta a karo na barkatai sannan ta sunkuya ta ɗauki wayar landline ɗin da ke kan wani teburin glass a gabanta ta danna wasu lambobi. A take kiran ya shiga kan wayar dake falon gidan. Wata siririyar mata ce ta ɗauki wayar ta kangata a kunnanta a ladabce tamkar tana gaban uwarɗakin nata ta ce,

"Hajiya na shigo ne?”

"Eh"

Kaɗai ta iya cewa ta kife wayar tana jin kamar zuciyarta tana juyin waina a cikin kirjinta. Da hanzari Madam Zainaba ta miƙe domin cika umarni. Cikin sassarfa ta soma bin mattatakalar benen da zai sada ta da ɗaki na uku kuma na ƙarshe a saman. Hannu na rawa ta tura ƙofar ɗakin da tun safe yake a rufe ta shiga. Kamar kullum sassanyan ƙamshin turaren wuta da ya kama ɗakin ta fara shaƙa. Kai a ƙasa ta ƙarasa shiga ta sameta tsaye a jikin taga ta bata baya. Sassauta murya ta yi a ƙoƙarinta na son kwantar mata da hankali da tsoron ɓata mata rai.

"Ki ƙara haƙuri Hajiya kinsan dole ne ta yi abin da kike so ko don gudun kada ki tona mata nata asirin"

Cikin takunta na ƙasaita da isa ta juyo tana murmushi. Tun asalinta mace ce me dakakkiyar zuciya, wadda sanin ainihin abinda yake ƙunshe cikin tunani da zuciyarta abu ne mai matuƙar wahala. Ba domin komai ba sai saboda ƙwarewarta wurin nuna fuskoki mabambanta da suke dacewa da duk

yanayin da ta sami kanta. Tana da tsananin wayo da dabara wurin samun abinda take so.

Haj. Hafsatu Manga Bukarti kenan. Asalinta mutuniyar jihar Borno ce. A kamannin fuska ta ɗebo mahaifiyarta bafillatanar usul amma a ƙirar jiki da kuma launi dangin mahaifinta ta biyo. Tana da tsayi sosai wanda zai bawa me kallonta tabbacin ita ɗin ta raɓu ƙabilar Kanuri. Duk da kasancewarta baƙa yanayin rayuwa ya sanya fatarta gogewa tana sheƙi. Kasancewar ta tashi cikin arziki kuma ta yi aure cikinsa ya sanyata cikin sahun farko na matan da ake kallo a sake kalla saboda kyau da gayu. Zanen fuska da ta gada wurin mahaifinta bai rage komai na kyawunta ba sai ƙarin kwarjini. Tana da tsaga guda ɗaya daga tsakiyar goshi har ƙarshen hancinta sai bibbiyu a kumatu da wasu biyun a gefen kunne sirara.

Mace ce mai kimanin shekaru arba'in gogaggiyar yar boko wadda ta karanci aikin jarida har zuwa matakin degree na biyu wato Masters. Sai dai bata taɓa aikin da ya shafi karatunta ba. Hasalima tana miƙa ragamar ilimin da take da shi ne wajen shirya abubuwa yadda take muradi kuma daidai da buƙatarta.

Madam Zainaba amintacciyar mai aikinta ce, wadda za su yi kai ɗaya ta fanin shekaru saɓanin gogewa. Amma hakan bai hanata yi mata hidima cike da ladabi da biyayya ba. Asalinta mutuniyar Kogi ce yar ƙabilar Igala. Sun haɗu ne a wani asibitin kuɗi a Lagos wanda ya kasance wurin zuwansu indai suna Nigeria kasancewar nan suka zauna da mijinta na fari kafin su dawo Abuja bayan rasuwarsa. Ba wani sabo suka yi ba da farko saboda Madam Zainaba mai shara da wankin banɗaki ce. Wani abu mai girma ne ya zama silar amintarsu har ta kai Haj Manga kamar yadda aka fi saninta ta ɗaukota zuwa gidanta. Bata da matsalar zaman gidan saboda bazawara ce kuma yayanta suna wurin mahaifinsu sai dai ta kai musu ziyara. Tamkar waziriya take ga Haj Manga, ita ce mai sawa da hanawa idan bata kusa.

***

Tashin hankalin da Fanna take ciki bazai faɗu ba a wannan yinin. Tana cikin tsaka mai wuya domin gabaɗaya tun bayan da Haj Manga ta fada mata buƙatarta sannan ta haɗa da tsoratarwa, ta fahimci cewa tana cikin yanayin da bahaushe ke

kira gaba kura baya sayaki. Zaɓi biyu ne rak take dasu, kodai ta tursasa Alh Audi ya saketa ta koma gida mahaifinta ya yi ƙuli-ƙulin kubura da ita ko kuma ta cigaba da zama da shi. Idan har ta yi hakan kamar ta ɗabawa kanta wuƙa ne, domin Haj Manga tana da ƙwaƙƙwarar shaidar da za ta zubar mata da mutumci da ƙima a idon duniya bayan ta kashe mata auren da ƙarfin tsiya.

Duk mai hankali baya buƙatar neman shawara akan wadda ya kamata ya zaɓa, amsar a bayyane take. Sai yanzu ta gasgata zantukan da ta jima tana ji cewa Haj Manga tana da hannu wurin watsa duk wani neme-nemen auran Alh Audi yayan marigayi tsohon mijinta. Kamar yadda jita jitan yake yawo cewa ake yi, tun bayan rasuwar uwargidansa duk lokacin da ya nemi aure sai ta yi kutu-kutu ta shiga ta fita ƙarshe sai dai aji cewa ya fasa auren saboda an sami mishkila daga ɓangaren matar.

Lokacin da nata mahaifin Manaja a reshen kamfanin Alh Audi da yake garin Maiduguri ya gabatar masa da ita akan ya nemi aurenta ko kaɗan basu sami matsala da Haj Manga ba. A takaice ma ita ce ta farko wajen bada gudunmawa ɗari bisa ɗari, ashe talala take yi musu. Aure shekara biyu ga ƙaramar yarinyar da ko yaye bata isa ba amma ana neman raba iyayenta.

Murɗa ƙofar ɗakin nata ta ji anyi cikinta ya bada wani mahaukacin sauti saboda tsabar firgici. Yau ce rana ta ƙarshe da Haj Manga ta bata ko kuma ta tona mata asiri. Sake lafewa ta yi ta runtse idanunta daga kwance tana jin shigowar Alh Audi tsakar ɗakin. Ransa a matuƙar ɓace yake da sabuwar tsirfar Fanna a yan kwanakin nan. Fitsara da rashin kunya kullum sai ta tsiro da sabo gareshi ko girmansa bata gani. Bargon da ta rufa da shi ya yaye da ƙarfi yayi jifa da shi a kasa sannan ya kira sunanta da sigar gargaɗi.

"Fanna"

Ga tsoro a zuci amma haka ta dake ta ta shi cike da tsiwa "sunana kenan!"

Kallon mamaki ya bita da shi. A zahiri faɗa yake son yi mata ko ya kamata ya fyala mata mari sai dai darajar mahaifinta a wurinsa yake dubawa da ƙuruciyarta shi ya sa ya canja akalar maganar da yayi niyyar yi zuwa lallashi.

"Zauna muyi magana"

Ya nuna mata bakin gadon shi kuma yana tsaye ya ɗora ƙafa ɗaya a kan gadon ya ranƙwafo daidai saitin fuskarta. Alh Audi Karam ba shi da tsaho sosai kuma babu kiɓa sai dai ba'a kira shi ramamme ba. Baƙi ne ba wuluk ba mai ƙaton tumbi da sanƙon da ya fara cinye gaban kansa. Fanna ta kawar da kanta gefe saboda tumbin ya matso gaban fuskarta sosai.

"Kaga Alhaji babu sauran magana a tsakaninmu kawai ka sauwaƙe min na kama gabana ko ana aure dole ne?"

"Ni kike faɗawa haka Fanna?"

"Kai waye da baza'a faɗa maka ba? Kuɗi ne dai taƙamarka ni kuma basa gabana"

Ta furta cikin sarƙewar murya, gabanta na dukan uku-uku saboda irin kallon da yake jifanta da shi kamar zai kai hannu ta ji saukar duka.

'Bani da lokacinki' ya ayyana a zuci saboda ya kula abin nata hadda alamun zuga saboda haka ya sauke ƙafarsa ya juya zai bar ɗakin. Tana ganin haka hankalinta ya sake tashi, bata san lokacin da ta danƙaro ƙaryar da take ganin za ta iya zama madafa ga tashin hankalin da ke bibbiyarta

"Alhaji gara ka sakeni tun kafin na tona maka asiri duniya ta san sirrin da kake..."

Maganar bata gama fita ba ta haɗiyeta tsaf saboda wani rikitaccen kallo da ya shiga jefa mata cikin ƙanƙanin lokaci sai ga wuyanta a tsakiyar hannunsa na dama ya kai mata mummunar shaƙa. Bakinsa har wata kumfa yake yi saboda kiɗima da ɓacin rai.

"Me kika ce!? Nace me kika ce!!?Me kika sani!!?"

Ya shiga jero mata tambayoyi bayan tuni ta yi nadamar amfani da tsoratarwar da aka yi mata a kansa. Kakari take yi idanunta sunyo waje saboda azabar riko. Hannuwanta biyu ta saka tana ƙoƙarin cire nasa guda ɗaya amma ta kasa. Alh Audi ya yi fushin da bata taɓa ganin irinsa ba. Idanunsa jajjurr ya sake cewa,

"Me kika sani?"

Fanna tana kakarin wahala domin ya sassauta shaƙar da ya yi mata. Ba abin da ke ta shi sai hucinsa kamar mahaukacin kare. Da alamu jira yake ta yi magana, murya can ƙasa ta ce,

"Wallahi ƙarya nake yi saki na kawai nake so kayi na faɗi hakan"

Sai da ya gama yi mata kallon tuhuma mai cike da zargi sannan ya yasar da ita a ƙasa ya fice daga ɗakin. Ajiyar zuciya ta soma saki da hawaye sai ga shi ya dawo ya jefa mata takarda akan fuskarta.

"Saki kike nema ko? Gashi nan nayi miki uku kuma kafin a kira magariba ki tabbata kin fita daga gidan nan idan ba haka ba sai kin gwammace kiɗa da karatu. Kuma kada ki sake ki ɗaukar min ya ke kaɗai zaki fita shashashar banza."

***

Ko da Alh Audi ya fita jiknsa sai tsuma yake yi, ya kai mari ya kai gauro. Tunani yake yi ya kasa gasgata shin shaci faɗi ta yi ko kuwa da gaske ne ta san wani abu. Sirrinsa a ɓoye yake yana da yaƙinin kuma waɗanda su ka sani harda ubanta Alh Ari basu isa su tona shi ba. A take hankalinsa ya fi kwanciya da gasgata zancenta yana mamakin me ya tunzurata yasa ta neman saki haka? Wata zuciyar ta raya masa bazai wuce yaro sa'anta take burin aure ba tunda dama tana da saurayi aka yi mata fin ƙarfi saboda babanta yana kwaɗayin karin matsayi a wurinsa.

Wayar dake falon farko kafin a shiga katafaren ɗakinsa ya ɗauka da zummar kiran Alh Ari yaci masa mutumci akan sakacinsa da Fanna sai ya ji tana magana daga ɓangarenta kasancewar wayar landline ce, idan wani yana magana a kan ɗaya daga cikin kawunan wayar gidan wani zai iya ji. Wadanda suke ɗakinsa ɗaya tana kama duka gidan, ɗaya kuma lambarsu ɗaya da ta ɗakin Fanna sai kuma cellular da yake amfani dasu kawuna biyu masu masifar tsada. Shiru yayi hadda ɗora hannu ya toshe daidai bakin saboda kada su farga cewa ana sauraronsu. Muryoyinsu tartar ya gane kowa a ciki. Fanna ce take cewa

"Ki fada mata ya bani takardar kuma saki uku ne."

Madam Zainaba ta ce

"kin kyautawa kanki, kada ki manta idan maganar nan ta fita kece zaki kwana a ciki"

A tsorace Fanna ta ƙanƙame wayar daga nata ɓangaren, tana waige kamar wani zai ganta,

"Madam Zainaba ki taimakeni ko nawa ne zan biya ki bani hotunan don Allah"

Siririyar dariya Madam Zainaba ta yi kafin ta ce,

"Hotunan haɗuwarki da tsohon saurayinki a Nicon Nuga Hilton garkuwa ne a wurin Haj Manga. Kamar yadda ta yi alƙawari ba za ta taɓa nunawa kowa ba cewa kina yawonki duk lokacin da Alh Audi baya ƙasar kema ki riƙe bakinki kada wanda ya san cewa da hannunta a mutuwar aurenki."

"Madam Zainaba...",

Sai dai kafin ta ƙarasa isar da muradinta kit Fanna taji shiru an barta da kan waya a hannu sai gumi da yake tsatstsafo mata kamar wadda ta yi tsere. Tana cikin mawuyacin hali a ɓangare ɗaya ga Haj Manga sannan ga mahaifinta sai kuma abinda ya tsaya mata a wuya yaki sauka wato tunanin wane sirri ne Alh Audi yake ɓoyewa wanda ya janyo sauyawarsa lokaci guda?

A nasa ɓangaren kuma sai da ta ajiye wayar sannan shi ma ya ajiye ta hannunsa kansa gabaɗaya ya kulle. Me yasa Haj Manga take shiga tsakaninsa da aure haka? Idan sauran ta kawo kabali da ba'adin halayensu basu da kyau me yasa ta takura Fanna akan neman saki? Sannan ƙarin takaicinsa Fanna tana yawo da igiyar aurensa. Ji ya yi komai ya cakuɗe masa ya tashi ya buɗe firij ɗin ɗakin ya ɗauko kwalbar giyar gulder ya cizge murfin ya shiga kwankwaɗa batare da tunanin zubawa a kofi ba.

***

Washegari Alh Audi Karam da kansa ya kira Haj Manga da Alh Ari ya nemi su zo yana son ganinsu kafin ƙarfe huɗu, saboda tafiya Japan da take gabansa akan harkar kayan wuta yana son buɗe wani sabon reshe mai suna Karam Electronics a ƙarkashin inuwar Karam Holdings Inc. Zuciyarsa ce ta kwana da zurfin tunani akan dalilin da yasa Haj Manga take yi masa haka. Ya sani cewa a halin yanzu babu yadda za ayi a ambaci mutum biyar da su ka fi kowa kuɗi a Nigeria sunansa bai zo a

na biyu ko na uku ba. Shekara uku da yan watanni da rasuwar ƙaninsa Alh Ibrahim Karam amma ya bunƙasa kasuwancin nasu sosai fiye da lokacin da ƙanin nasa yana raye. Ribarsu ta habbaƙa arziƙi ya kama ƙasa. Mata rububinsa suke yi, shekaru ko cikinsa da yake ƙwajaja bai sagar musu da gwiwa ba indai zasu amsa sunan iyalinsa.

Shigowar Tony PA (personal assistant) ɗinsa cikin falon da yake karɓar baƙi ce ta katse masa tunani ya sanar da shi isowar Alh Ari. Umarni ya bayar da ya shigo da shi saboda yana son su zanta kafin isowar Haj Manga, dalilinsa kenan na bada awa guda tsakanin lokacin da ya basu na ganinsa.

Fuskar Alh Ari kamar wanda aka aikowa saƙon mutuwa yana cikin ɓacin rai mai tsanani ko hannun Alh Audi da ya miƙo masa su gaisa yaƙi karɓa. Tony na rufe ƙofar bayan ya jefawa Alhajin wani irin kallo tamkar zai kai masa duka ya soma magana.

"Alh Audi ni za ka wulakanta ka sako min ya saki har uku?" Ya fada yana haki. Alh Audi bai nuna ɓacin rai ba ko kaɗan "ka zauna Alh Ari akwai abinda nake so ka sani"

Baza hannuwan babbar rigarsa yake yi cikin yanayin ko in kula ya ce,

"Babu wata magana tsakaninmu, kai ka san cewa a tafin hannuna kake billahillazi duk ranar da na buɗe wannan bakin" ya ɗora manunin yatsansa yana bubbuga laɓɓansa "sai ka ji inama baka..."

"Kai ARI!"

Alh Audi ya daka masa wata irin tsawa mai firgitarwa. Ba tare da ya jira ya amsa ba ya nunashi da hannunsa, murya a ƙausashe kamar wanda aka yi wa wahayin mutuwa.

"Jiya Fanna ta kalli tsabar idona tana faɗa min cewa ta san sirrina yau kaima kana iƙirarin tona shi? Bani da niyyar tsawaita magana kai ka san waye Audi farin sani. Shiga gonata ba zai yiwa kowa kyau ba saboda haka ina shawartarka da ka rubuta ka ajiye duk ranar da ƙaiƙayin baki ya nemi kwasarka sai na nuna maka wannan Audin yafi wanda ka sani a da."

Jikin Alh Ari sai ya yi sanyi laƙwas ba wai don ɓacin ransa ya sarara masa ba. Zama ya yi rigijif akan kujera ya cire hularsa yana fifita da ita ba don zafi ba sai don rasa abin yi. Daurewa

ya yi kada ya nuna masa tsoron da yake cin zuciyarsa ya soma magana.

"Alh Audi me yasa kayi min haka? Na taimaka maka lokacin da kake buƙatar taimako kuma na iya bakina akan sirrinka. Abu ɗaya na nema shi ne ka auri Fanna domin daga min darajata shi ne kayi mata sakin da babu gyara don ka nuna min iyakata?"

"Ko ɗaya Alh Ari, mutuwar auren nan ba aikin kowa bane sai na Haj Manga" ya faɗa masa duk abinda ya ji a waya tsakanin Madam Zainaba da Fanna a yammacin jiya. Sai da ya sha ruwa rabin tambulan da yake gabansa ya ɗago kai yana kallon Alh Ari da ya zuba masa idanu,

"Abinda ban fahimta ba shi ne dalilinta na hanani aure, kana ganin tana sona ne?" Ya kece da dariyar rashin yarda da abinda ya faɗa shi da kansa. Sai lokacin Alh Ari ya soma samun nutsuwa har ya iya kawo nasa hasashen akan dalilin Haj Manga.

"Baka tunanin ko akan Arƙam ne? Shekara uku fa ba kwana uku bane."

Idan akwai abinda Alh Audi ya ke gudu bai wuce a tayar da maganar Arƙam ba. Hannuwansa biyu yasa ya dafe kansa sannan ya ce,

"Ban taɓa zaton abin alkhairi zai zame min sharri ba Alh Ari, yaron nan anyi neman har an gaji"

Damuwa sosai ce ta bayyana a fuskar Alh Ari,

"Indai haka ne ni ban ga laifin Haj Manga ba. Gani take yi kamar wani abu ka shiryawa ɗan nata ko ya mutu an ɓoye. Ko ni ne fa dole na ɗora alamar tambaya, ta yaya daga kai yaro karatu za a neme shi ko sama ko ƙasa kamar allura?"

Kwafa Alh Audi ya yi yana kaɗa kai,

"Tun ranar da aka bugo waya daga makarantar na nemi kwanciyar hankali na rasa. Ko sati bai yi ba ya gudu, ina raina shi ganin sanyinsa ya yi yawa ashe shaiɗanin kansa ne?"

"To ko dai mutuwa yayi ne ba a ga gawarsa ba?" Cewar Alh Ari, maganarsa kuwa ta ƙara dulmiya Alh Audi cikin tunani wanda alhini ya bayyana ƙarara a fuskarsa. Sun koma tattaunawa akan ɓatan babban ɗan Haj Manga wanda ya kai

wata makaranta a birnin Nottingham da yake Ingila domin ya karasa karatun shekara guda da ya rage masa na babbar sakandire sannan ya nema masa gurbin karatun a jami'ar garin. Lokacin tana takabar mijinta bata cikin nutsuwa da hankalinta ko kaɗan. Kasancewar tsakanin Arkam da ƙaninsa Jamal akwai tazarar shekara bakwai shi ya sa ba a sako shi ba a lissafin tafiyar ba domin ya yi ƙanƙanta. Amma a tsarin tun farko hadda nasa ɗan Shamsu sai shi kuma ya kamu da rashin lafiya yana kwance a asibiti har aka fara karatu da sati ɗaya.

Gudun kada duka suyi latti sai ya fara kai Arƙam dama shi ne babba da alƙawarin Shamsu na samun lafiya zai kawo shi da kansa. Sai dai kuma hakan bata samu ba domin kwana huɗu da dawowarsa Nigeria ya sami waya daga makarantar wai Arƙam ya gudu. A daren ranar ya yi sa'ar samun jirgi suka ta shi da Tony PA sai da ya yi sati biyu ana yawon offishin jakadanci na Nigeria dake ƙasar da na yan sanda neman madafa. Kafin su dawo sai da ya rame cikinsa ya dan ja baya saboda tashin hankali. Bayanai daga airport sun nuna tabbas Arƙam matashi ɗan shekara goma sha bakwai bai bar ƙasar ba amma an kasa samunsa.

Alh Audi ya kira Alh Ari tun a lokacin ya bada umarnin a tsayar da account ɗinsa ta yadda ba zai iya cire kuɗi ba dole wahala ta fito da shi idan ma ɓuya ya yi. Bankin da aka buɗe masa account a ƙasar ma a take yasa aka kulle shi amma har yau shiru babu shi babu labarinsa a idon duniya. Haj Manga tana gama takaba ko ta kan Alh Audi bata bi ba ta ɗauki Jamal suka tafi kaiwa Arƙam ziyara a nan ta haɗu da mummunan labarin da Alh Audi yake ta ɓoye mata. Da ta tashi sai ta kira shi tana tambayarsa yaya sunan makatantar da Arƙam yake shaf ta manta sai da suka je garin ta tuna bata tambaye shi ba. Alh Audi sai ya ɓuge da borin kunya wai tana son nuna masa iyakarsa akan ɗanta shi ya sa ko ta kansa bata bi ba ta tafi ganinsa. Ya gama bambamin faɗansa ya ce kuma ta dawo gida idan ya isa da ita domin ya riga ya canja masa makaranta ma sabanin wadda ya bata ta saka hannu a matsayin uwa. Daga ranar ta ɗora ƙatuwar alamar tambaya akansa na rashin faɗa mata gaskiya. Ta yi kuka ba kaɗan ba a hankali hawan jini ya sarƙeta ga mutuwar miji ga ɓatan ɗa.

Yanzu an shekara uku tana neman Arƙam a gefe shima Alh Audi bai fasa ba kamar yadda makusancinsa Alh Ari da Tony suka sani amma har yau yaƙi faɗa mata gaskiya da bakinsa sai

dai yayi ta hanya-hanya yana zillewa. Ƙarairayin nasa da dabaru tuni sun ƙare ƙarshe ya yi mata jan ido cewa a matsayinsa na wan uba ga Arƙam shi ya soke masa zuwa gida sai ya gama karatunsa gabaɗaya saboda soyayyar da take gwada masa ita ce take sangarta shi ya tashi da sanyi babu hayaniya irin ta matasa sa'anninsa. Wannan kenan.

***

Shawara Alh Ari ya ba shi domin su san manufarta gara ya aureta kawai. Batun Fanna kuma zai yi mata auren kisan wuta da zarar ta gama idda sai a mayar musu da aurensu. Alh Audi yayi na'am ɗari bisa ɗari ko babu komai idan ya nunawa Alh Ari yana son zama da yarsa ya tabbatar sirrinsa zai cigaba da kasancewa a ɓoye. Batun yawon da take yi da saurayinta ta sha ruwa indai buƙatar su biyun za ta biya.

Awarsu guda da rabi Tony ya zo ya sanar da isowar Haj Manga da waziriyarta Madam Zainaba. Ita kaɗai ta shiga falon aka bar Madam Zainaba tare da Tony a wani falon. Sai da ta gyara yanayin fuskarta ta yi alamun damuwa sannan ta shiga falon a firgice. Takun nan na ƙasaita babu shi ta kwantar da kai hadda guntun hawaye ta samu wuri ta zauna.

"Yaya Audi me nake ji haka wai ka saki Fanna?"

Ta ɗan muskuta tana kallon Alh Ari ta wutsiyar ido,

"Kayi hakuri Alh Ari na tabbata kai da Haj. Kolo kuna cikin tashin hankali amma babu komai gara ayi sulhu yanzu ya mayar da ita"

Saroro Alh Ari ya yi yana kallon rainin hankali na Haj Manga shi kuwa Alh Audi murmushi ma ya yi. "Babu sauran aure a tsakaninmu na riga na yiwa Alh Ari bayanin komai kuma shi ma ya fahimta"

Kai kawai Alh Ari ya gyaɗa sannan ya ce "abinda ya faru laifinta ne saboda haka ba zai taɓa zumuncina da Alhaji ba"

"Ni dai banji daɗi ba gaskiya, Yaya Audi saki uku ai sai yara manya masu hankali da zurfin bincike aka sansu"

Magana ta faɗa masa a fakaice daga shi har Alh Ari sun fahimta amma sai suka ƙi nunawa. Ta zauna ta yi ta yabon Fanna da nuna tausayin Kulsum saboda ƙarancin shekaru. Ƙarshe kwabe fuska ta yi ita a dole tana cike da damuwa ta ce,

"Yanzu waye zai kula da ita Kulsum ɗin Yaya Audi?"

Danne ɓacin ransa ya yi ya ƙirƙiro mata murmushi mai nuna alamun kifi na ganinka mai jar koma,

"Ke nake so na barwa wannan amanar idan zaki iya yi min alfarma"

"Kamar yaya?"

Ta tambaya da alamun mamaki duk da cewa tana murna ne ya faɗa tarkonta.

Alh Ari ne ya bata amsa "Haj Manga auren Fanna ga babban mutum kamar Alh Audi kuskure ne daga gareni. Akwai ƙuruciya da zafin kaina tare da ita, Alhaji yana buƙatar mace mai nutsuwa da shekaru kamar naki wadda ta san yau ta san jiya. Yana buƙatar matar da za ta iya riƙe masa gida ta taimaka masa akan harkar kasuwancin nan"

"Sannan ina buƙatar haɗe kan 'ya'yana wuri guda. Ina son Arƙam da Jamal su dawo ƙarƙashin kulawata kema ki taimaka min wurin kula da Shamsu da Kulsum"

Shiru ta yi kanta a ƙasa taki basu amsa sai shesshekar kukanta da suke ji. Alh Ari kamar ya ta shi ya shako wuyanta haka ya daure yana ta bata baki cikin minti goma ta amince da su nemi Baffanta ayi magana. Miƙewa ta yi za ta fita Alh Ari ya dakatar da ita da tsokanar ƙarfi da yaji "haba amaryarmu ki tsaya mana ku ɗan zanta da ango mana"

Kawar da fuska ta yi alamun kunya tana dariya,

"Kada muyi haka da kai don Allah".

Tana fita suka ɗora zancen akan mamakin diramar da ta gama yi musu yanzu duka su biyun sun gaskata lallai neman Arƙam ne yasa take son auren Alh Audi domin ta san inda ɗanta yake. A hanyarsu ta komawa gida tsakanin Haj. Manga da amintaciyarta suka soma tattaunawa cikin magana ƙasa-ƙasa.

"Ban san yadda aka yi ba amma jikina yana bani cewa sun gane akwai hannuna a cikin lamarin nan."

Madam Zainaba ta murmusa "idan kuwa haka ne Hajiya ina tayaki murna domin buƙatarmu ta biya sai dai har yanzu na kasa gane me yasa kike son ya san cewa saboda neman Arƙam kike son auren shi?"

Murmushin gefen baki Haj Manga ta yi, ta datse gefen leßßanta tana kallon titi,

"Saboda neman Arƙam shi ne babban abinda yake gabana amma ba shi kaɗai ne a gaban nawa ba. Karam Holdings zuciyata ke hari, na kuma rasa dalilin faruwar hakan a gareni."

Ta faɗa tana dunƙule hannu haɗe da kai wa iska wawwan naushi, kamar ita ta kashe zomon.

Idanu Madam Zainaba ta ƙwalalo cike da mamaki "Hajiya kina nufin kamfanin gabaɗaya?"

"Ko kina ganin bazan iya bane?" Ta kafeta da idanuwanta masu tsuma zuciyar mutane musamman na ƙasa da ita. Fahimtar cewa taso yin katoßara yasata saurin gyaɗa kai kamar ƙadangaruwa cike da hanzari "ko kadan Hajiya, gani nayi abin ba na yau ko gobe bane"

Murmushi ta yi mai cike da ma'anonin da ita kaɗai tasan manufarsu a ƙasan ranta,

"Daɗina dake saurin fahimta Zainaba. Tabbas mallakar Karam Holding ba abu bane da zan iya yi yau ko gobe, aiki ne da zai ɗauki lokaci shiyasa ma na tura kaina jikin Alh Audi. Don ta Arƙam ko ban aure shi ba dole ne ya fito min da ɗana idan yana son kwanciyar hankali"

***

Abu kamar wasa wata uku bayan sakin Fanna maganar auren Alh. Audi da Haj. Hafsatu Manga ta karaɗe lungu da saƙo na Najeriya. Wannan yamaɗiɗin ya faru ne ba don komai ba sai don kasancewar dama can ana raɗe-raɗin tana shiga ta fita ta hana shi aure a matsayinta na matar ƙaninsa da ya rasu. Kan kace mene ne wannan labarai kala-kala sun soma yawo ana tono rayuwarsu ta baya. Babban abin da ya fi ɗaukar hankalin mutane kuwa shi ne rasuwar Alh. Ibrahim mijinta da Tsaiba matar Alh. Audi a cikin shekara guda, a taƙaice ma dai tsiransu wata biyar ne da yan kwanaki. Shiyasa masu ƙarfin hali suka ɗora musu alamar tambaya ana ganin kamar akwai wata a ƙasa. Tun daga wannan lokacin kuma ita Haj. Manga ta fito da maitarta a fili take hana shi aure ga shi yanzu a cewar yan bani na iya sun gaji da ƙumbiya-ƙumbiya zasu yi auren. A wata majiyar ma cewa ake yi dama suna neman juna, wasu kuma sun tafi akan cewa kuɗi ne yake ruɗarta. To ko ma mene ne

dai magana ba ta fitowa a jiki shiyasa ko a jikinta wai an mintsini kakkausa.

Ta ɓangaren Alh. Audi shiri yake yi sosai saboda yana ganin wannan karon dai idan ya yi auren ya yi shi Kenan. Ko wane irin abu Haj Manga take tunanin shigowa da shi gidansa ya sani cewa ya fi ƙarfinta kuma aure ne za su yi babu yaji bare saki. Danƙarreran gida yasa aka gina masa na gani na faɗa irin wanda duk girman Abuja a wannan lokacin na shekarar 1999 babu kamarsa. Har tururuwar zuwa ganinsa ake yi, mutane da dama basu taɓa ganin gida mai kyau da tsarin Karam Mansion ba. Domin ba ƙaramin kuɗi ya narka ba kamar bai san ciwonsu ba, duk a ƙoƙarinsa na son ganin gidansa ya doke na mutumin da yake riƙe da ragamar lamba ɗaya a kuɗi a ƙasar.

Karam Mansion katon gida ne wanda aka zube ƙarshen basira wurin gina shi. Mutumin da ya zana gidan har yau bai yi aikin da ya sama masa maƙudan kuɗaɗe kamar zane da tsara wannan gini ba. Katafaren fili ne da aka yi gine-gine a cikinsa. Banda ainihin gidan da yake daga ɓangare ɗaya akwai wani daga jikinsa, ta gefen swimming pool (wajen wanka) madaidaicin flat mai ƙofofi uku kusa da juna da su ke fuskantar ruwan. Kowace ƙofa idan an shiga ƙaton falo ne da ƙaramin kitchen sai ƙofar ɗaki da banɗaki a cikinsa. Ɗakunan anyi su ne domin yan mazan gidan, wato Arƙam Ibrahim Karam, Shamsu Audi Karam da kuma ƙaramin cikinsu Jamaluddeen Ibrahim Karam. Shamsu da Jamal ne kaɗai zasu amfana da nasu, tunda ba a san inda Arƙam yake ba har yanzu. Haka ma ɗiyarsa Kulsum duk da ƙuruciyarta ita ma an ƙawata mata nata ɗakin a sama, kafin a ƙarasa sashin da ɗakunan iyayan suke.

Bayan ɓangaren samarin a can gefe kusa da katanga wani ginin ne guda biyu iri ɗaya, amma sun juyawa juna baya. Basu kai sauran gidan kyau ba amma suma sun tsaru daidai gwargwardo. Kai tsaye za a iya fasalta sashin da na masu aikin gidan, duba da yadda aka tsarashi ɗaki bayan ɗaki kuma kowane da makewayi cikinsa. Sashin farko na masu aikin cikin gidane, kama daga wanke-wanke da shara da kuma goge-goge. Ɗayan kuma na masu aikin waje wato masu gadi, direbobi, mai wanki da guga, mai sharar farfajiyar gidan da kula da shuke-shuke da aka ƙawata gidan dasu da kuma ƙaton ni'imtacen garden (lambu). Sai kuma wani ginin hawa biyu da aka yi musamman domin baƙi. Har ila yau akwai keɓantaccen wuri

da aka ajiye namun daji irinsu barewa, jimina, ɗawisu da birai. Sai da aka gama komai na gidan aka zuba kayan more rayuwa kamar anzo duniyar kenan sannan Alh Audi ya je Maiduguri bisa jagorancin Alh Ari da wasu abokansu su biyu su ma masu kuɗi da faɗa a ji suka yi masa rakiyar neman aure.

Kai tsaye suka nufi gidan Justice Umaru wanda dangi suke kira da Baffa Alƙali, shi ne kawun Haj Manga wanda ya riƙeta tun bayan rasuwar iyayenta. Alƙali ne a kotun (ɗaukaka ƙara) court of appeal. Yana daga cikin masu kuɗin da Jihar Barno take ji dasu. Dattijo ne kaifi ɗaya kusan halayensa kaf Haj Manga ta ɗebo tamkar ya yi kakinta ya tofar ta wannan fanin. Idan suna yi da kai to fa ka ciri tutar gata da soyayya amma muddin ka shiga bakin littafinsu to sai ta Allah. Wayau ne dasu da dabarar iya ƙulli, shi Alƙali ita kuma karatun aikin jarida saboda haka ake gwaren ideas (fikra). Yawancin duk abinda take yi yanzu na hana Alh Audi aure shi ne yake kitsa mata tare suke shirya komai. Allah bai ba shi yaya mata ba sai ita kaɗai tilon yar ƙaninsa shiyasa yake matuƙar ji da ita. Dansa na uku Kashim shi ne sa’anta. Sauran akwai Ali, Babagana, Kachalla da Bukar. A rayuwarsa indai Hafsatu zata ce wash to Baffa Alƙali ya dinga tambayarta kenan,

"Manga me ya sameki? Manga me ki ke so?"

Cikin wannan gata ta tashi bata da uwa da uba amma Baffa Alƙali bango ne madogara a gareta. Bayan gajeriyar tattaunawa da su Alh Audi ya ce ya ba shi aurenta sai su faɗi lokacin da suke ganin ya yi musu a zo a ɗaura aure. Alh Ari ne ya yi uwa ya yi makarɓiya shi yake bada amsa akan komai tamkar babu wata ɓaraka tsakaninsu. Hankalinsa a kwance yake, ya riga ya daidaita da wani yaronsa zai aura masa Fanna sati ɗaya bayan ta gama idda. Amma da sharaɗin zai sakota bayan wata uku. Ya gama lissafa komai a cikin ransa sai jiran lokaci. Sun kammala komai suna shirin tafiya Baffa Alƙali ya sako zancen Arƙam cikin wasa.

"Wane course yake karantawa ne ɗan naka?"

Alh Audi da bai fahimci inda ya dosa ba ya yi murmushi a zatonsa tambayar akan Shamsu ne,

"Business Admin".

"Amma shi da ya yi science (kimiya) me ya kai shi karatun Business (kasuwanci? Kodayake na ji ance karatun turai babu tsauri kamar namu, suna iya canja masa idan ya sauya ra'ayi"

Gaban Alh Audi sai da ya faɗi da ya gane da wa ake. Sunkuyar da kai ya yi yana ƙaƙalo murmushin jin kunya ya yi saurin gyara zancen,

"Shamsu ne ya fara level one wannan shekarar, Arƙam yana level two ne dayake ya wuce shi da shekara ɗaya."

Kallon ido cikin ido Baffa ya yi masa fuskarsa a tamke tamau,

"A wace makaranta Shamsun yake?"

Cikin Alh Audi ya tsirga, indai ba yana hauka ba ga kowa ya saka masa ido akan rashin sanin ina Arƙam yake yaushe zai sake tura wani ɗan kasar waje.

"Gwagwalada yake, University of Abuja."

Babu wani ɓoye-ɓoye Baffa ya ce,

"Shi nawa jikan ne ka kai wata ƙasar har yanzu ka kasa kawo mana shi mu ganshi? Duk karfin dangin uba fa Alh Audi ka sani cewa uwa ma tana da nata haƙƙin." Ya gyara zaman gilashin idonsa sannan ya cigaba da cewa "Magana ce ta aure a tsakaninku shiyasa nake mai baka shawara, da ka fitowa Manga a mutum sak ka bata ɗanta ko da rai ko a mace. Na san ba kasafai ake so mutum ya dinga karewa yayansa ba amma magana ta gaskiya ta yi haƙuri na ban mamaki akan yaron nan."

Yana kaiwa nan ya tashi abinsa ya shige ciki ya barsu su huɗu zaune kamar ruwa ya cinyesu. Ɗaya daga cikin abokan nasa da suka zo tare mai suna Haji Lawalli ne ya soma magana bayan ya dena jin alamun tafiyar Baffa. Kai tsaye ya aje kallonsa a saitin Alh Ari sakammakon sanin duk cikinsu ya fi su kusancinsu da Alh Audi.

"Kaga maganata ta jiya ta fito ko?"

"Wace magana kenan?" Cewar Alh Audi yana bin su da idanu ɗaya bayan ɗaya.

"Alhaji gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, INA ARƘAM yake?"

Haji Lawalli ya jefa masa tambayar da ya riga ya gaji da jinta. Bai jira amsarsa ba ya ɗora a zafaffe da cewa,

"Ko da bani da masaniya akan komai amma ina da yaƙinin babban abin da yasa Haj. Manga amincewa aurenka bazai wuce saboda rashin sanin ina ɗanta yake ba. Mu ɗin ma idan mun tambayeka sai dai kayi ta kauce-kauce. Saboda Allah jama'a an taɓa haka?" Ya yi tambayar yana raba idanu tsakaninsu.

Abin mamaki garesu duka bai wuce hawayen da suke zarya a kumatun Alh Audi ba. Abin da zai girgiza wannan mutumin ya wuce raini amma yau akan ɗan ƙaninsa yake hawaye gidan surukai? Zubar hawayensa nasa ya tayar da hankulan sauran abokan nasa biyu amma Haji Lawalli tsaki ya doka saboda takaici. Wannan tsakin ne ya ƙular da Alh Ari har ya shiga yi wa Haji Lawalli tonon silili a wurin.

"Haji Lawalli idan dai da gaske ka damu kai kanka ka sani ba nan ne muhallin kawo maganar nan ba amma saboda baƙin cikin Haj. Manga bata karɓi tayinka ba shi ne kake neman kunyata abokinka a gidan surukansa."

Ai fa an taka jelar miciji ran Haji Lawalli ya sake dugunzuma ya tashi a fusace ganin Alh Audi da Alh Hadi suna kallonsa da mamakin jin wannan magana.

"Ko da aure ko babu ni mai kulawa da Haj Manga da yayanta ne domin amintarmu da Ibrahim ta wuce duk inda kuke tunani."

"Don Allah ku tashi mu tafi, wane irin abu ne haka da girmanku a gida irin wannan kuke mana tashin hankali?" Cewar Alh Hadi ya mike tsaya yana jira su tashi. Haji Lawalli ne akan gaba ya fice ko sake kallonsu bai yi ba. Alh Audi kuwa sai da Alh Ari ya taimaka masa ya iya miƙewa jiki a saɓule. Gidansu na garin su ka wuce wanda aka gina shi tun bayan auren Ibrahim da Hafsatu Manga kasancewar suna zuwa garin akai-akai shi kuma da kuɗinsa bai yarda da zuwa hotel ba kodayaushe ko zaman gidan surukai. Suna isa kowa ya sauka banda Haji Lawalli ya ƙwame a bayan mota yace airport za a kaishi ba zai kwana a garin ba. Duk yadda suka kaɗa suka raya ya dage yace bazai zauna ba, yana da abin yi. Bayan ya tafi sun shiga gidan masu aiki suna ta karakaina ana ƙoƙarin haɗa

musu abinci su Alh Ari suka dinga bawa Alh Audi haƙuri. Alh Hadi ya ce,

"Kada ka manta Haji Lawalli tare suka girma da marigayi saboda haka yana ganin kamar yafi kowa kusanci da cancanta ya auri Haj Manga ya riƙe mata yaya shiyasa"

Alh Ari uban kauɗi ya yi saurin tarewa amininsa,

"Idan yana taƙamar abota shi kuma Alh Audi da suke jini ɗaya fa? Har akwai wani kusanci sama da na ka haɗa uba da mutum? Kawai ka yarda kishi ne yake ɗawainiya da shi" sai kuma ya dan kwantar da kai ya rage murya "amma Alhaji wai da gaske ba za ka dawo da yaron nan gaban uwarsa ba ko don ka kubuta daga zargi ba?"

Jiki ba kwari Alh Audi ya sake labarta musu abinda ya faru domin Alh Hadi bai san komai ba.

"Har yanzu da nake muku maganar nan neman yaron nan ake yi ban taɓa hutawa ba. Kuna tunanin da gangan zan boye shi na janyowa kaina zargi da zagi ne?"

Cikin ƙunar rai yake magana idanunsa sun sake ƙanƙancewa,

"da na san cewa haka zata faru ko don kuɓuta daga fushin Dada da maganganun da ake jifana dasu da tuni ko ba shi da rai na kawo gawarsa na huta" kwalbar giya ya ɗauko ya shiga ɗaɗɗaka sai da ta kusa ƙarewa ya direta yana cije leɓe ya nisa a tunani. Daga ƙofar falon Tony PA ne ya gama sauraron hirarrakinsu ya murmusa "hmm dama ni ku ka kama da kun daɗe da mantawa da Arƙam ya taɓa ɓata."

Wayarsa ya lalubo ya rubuta sakon SMS da turanci wanda fassararsa take nufin (Ina buƙatar ƙarin kuɗi saboda ya soma tayar min da hankali cewa yana son dawowa gida). Sai dare amsarsa ta shigo inda aka rubutu masa (Ok) kawai.

***

Saukarsu Haj Manga kenan a birnin Dabo, Kano ko da me kazo an fika. Cikin shigar da aka fi gani a jikinta kodayaushe ta lafayya. Atamfa ce super exclusive a jikinta mai adon fari da koren ganye ta naɗe jikinta da lafayya ruwan madara mai adon bakin leshi. Yatsun hannuwanta sun sha jan lalle, wanda ya soma baƙi ga zabban gwal reras. Kafarta kuwa irin jan lallen nan ne wanda ake saka salatif ayi ado daga samansa, ya yi

mata kyau sosai. Kunshi a wurinta wani ne yake tarar da wani ta riga ta saba. Sassayan ƙamshin turarukan humra da ya jima da kama jikinta ke ta shi fuskarta babu wata kwalliya sama da hoda da kwalli sai mai a leɓenta amma ta yi wani irin kyau.

A gefenta yaro ne ɗan shekara goma sha uku cikin ɗinkin tazarce da hula. Babu ta inda ya ɗebo mahaifiyar tasa a kamanni domin kuwa shi fari ne mai ƙaramin jiki idan an kwatanta da yanayin nata jikin. Kai tsaye motar da take jiran ƙarasowarsu ta nufa an riga an buɗe mata ta shiga ta zauna Madam Zainaba ta zaga ɗaya ɓarin riƙe da jakar Hajiyar. Shi kuma Jamal ya shiga gaba. Wani ma aikacin filin jirgin kuma ya ɗauko akwatunan kayansu ya saka a booth (bayan mota). Madam Zainaba ce ta biya shi ya dinga zuba godiya kamar ya ari baki har su ka isa unguwar Yakasai gidan Dada mahaifiyar marigayi Ibrahim. Sai da suka yi sallah da cin abinci sannan Dada ta zauna tare da Haj Manga.

Farar dattijuwa ce mai ɗan ƙaramin jiki alamu sun nuna a wurinta Jamal ya yi gado. Girmanta ya yi kyau domin da hankalinta sannan tana da ƙwari don har yanzu bata ranƙwafa ba. Idan ka cire yan ciwake-ciwaken da kan kama masu shekaru irin nata bata da wata matsala sai ta raunin idanu shiyasa take amfani da gilashin ido. Hira take yi da jikan nata yana ta zuba mata surutun wai saboda tace ya yi kyau ya sako manyan kaya.

"Ai kuwa kayi kyau wannan auren namu ya kamata na sake biyan sadaki saboda ya ƙara ƙarko."

Jamal ya kwashe da dariya, "Dada maza ne suke biyan sadaki fa ko Nanna?" Ya tambayi Haj Manga da take shirin zama akan wata dadduma ruwan zuma. Murmushi ta yi kawai ta kaɗa shi waje saboda amsa kiran Dada. Yana fita kuwa Dada ta haɗe fuskarta tamkar ba ita ta gama wasa da dariya da jikanta ba. Maganar ɗaya ce ta sani dama shi yasa bata ji mamakin fitowarta daga bakin Dadan ba.

"Audi ya zo nan shekaranjiya ya faɗa min zasu je neman aurenki."

Sunkuyar da kai ta yi batare da ta amsa ba. Dada ta ji wani abu ya taɓa mata zuciya sai dai kuma bata da hurumin hanata aure don ta taɓa auren ɗanta.

"A matsayin ya na ɗaukeki Hafsatu ba don lamarin Arƙam ba babu yadda za'ayi na zuba miki ido kiyi ta zama babu aure." Ta numfasa sannan ta cigaba da magana "Audi ma ɗana ne idan kun haɗa kanku bani da abin cewa sama da yi muku addu'a da fatan alkhairi."

Kai a sunkuye Haj Manga ta ce,

"Dada nagode."

"Idan kin gode Hafsatu to ku fito min da jikana."

Dada ta ce lokaci guda tana fashewa da kuka mai tsanani. Dam! Haj Manga ta ji zuciyarta ta buga da ganin hawayen Dada. Kwarai tana jin tausayinta amma zuciyarta ta riga ta bushe ta yadda kukan ma sam ta kasa yi sai haƙuri da take ta bata. Sai bayan kimanin minti goma Dada ta sami nutsuwa, amma muryarta ta yi rauni sosai tana rawa ta kama hannuwan Haj Manga ta riƙe gam,

"Kamar yadda na roƙi Audi kema ina roƙonki don Allah kada na mutu ban sake saka yaron nan a idona ba. Idan mutuwa ya yi ku faɗa min, na iya haƙura da iyayena, kakansa da mahaifinsa ma me zai hana ni haƙura idan shi ma ya koma ga Mahaliccinmu?"

"Dada wallahi..."

Girgiza kai Dada ta shiga yi "uhmm uhmm na gaji da rantsuwarku daga ke har Audi. Ba don mutuwa ta ɗauke min Ibrahim ba baku isa ku gwada min iko akan yayansa ba."

"Ba haka bane Dada" Haj Manga ta sake jin wata muguwar tsanar Alh Audi zuciyarta ta cigaba da saƙa mata yadda za ta mayar da rayuwarsa abar kwatance idan ya kasa bayyana mata Arƙam, a raye!

Washegari ta koma Abuja tare da Madam Zainaba, ta bar Jamal a wurin Dada. Sai dai gaba ɗaya tafiyar bata yi mata daɗi ba, bayan artabun da suka sha da Dada nan ma bata sake zani ba. Wata yar ƙanin Dada ce ta zo gidan ta sauke mata kwandunan rashin mutumci kala-kala. Ɗan uwanta daya kasance bangon jinginarsu take tayawa kishi ga zargin ta haɗa baki da Alh Audi sun ɓatar da Arƙam. Bata tanka mata ba ko sau ɗaya, sai ma Dada ce ta dinga ƙoƙarin tsawatarwa, ga kuma Madam Zainaba dake ƙoƙarin kare mata abin dai ya so ya koma rigima sosai. Tana daga gefe tana sakin murmushi, sai

dai kowane furuci na matar tana ajiyeshi a mizanin da ya dace kafin ta waiwaye shi. Koda wasa bata bada ƙofar da za a fahimci maganganun sun taɓa ba, sai ma ƙoƙarin maida abin wasa da dinga yi. Sosai hakan ya ƙara mata martaba da ƙima a idon surukarta ta.

***

Duk wani abu da ya kamata a shirya anyi an gama. Wata biyu bayan zuwa tambaya Maiduguri, su Alh Audi suka koma aka ɗaura aurensa da Haj Hafsatu Manga, akan sadaki mai tsada wanda ya biya da sulallan gwal. Taron ya sami halartar manya manyan ƙusoshin gwamnati, yan kasuwa da masu faɗa a ji a Najeriya da kewaye. Cikin kwana huɗu aka gama komai amarya ta tare a sabon gidanta dake unguwar Asokoro a birnin tarayya Abuja.

Wata shidan farko Haj Manga ta sauke duka makaman yaƙinta ta nunawa Alh Audi kulawar da ta dace da ango irinsa. Shi kuma wannan kulawar ita ta susuta shi ya sami kansa da yi mata soyayya da zuciya ɗaya. Da yake abin da take so kenan sai ta ƙara bada himma wurin tattalinsa da na yayansa. Akwai mai reno da aka ɗauko musamman domin Kulsum, amma duk da haka kusan komai ita take yi mata. Tun yana zargin akwai ranar da zai kama ta da laifin cuzgunawa yarinyar a bayan idonsa har ya haƙura ya aminta da ita. Matsalarta guda ɗaya ce Shamsu idan ya zo hutun ƙarshen mako daga Gwagwalada.

Kishi yake gwada mata na fitar hankali akan mahaifinsa. Shi ma kuma uban sai ta kula da takunsa, yana matuƙar gudun ɓacin ran ɗan nasa. Wannan abu bai ɓata mata rai ba ko kaɗan sai ma dariya da take yi a gefe. Wato shi da nasa ɗan suna son juna, ita da nata da aka rabasu ko su mutu ko suyi rai saboda kewa ba damuwarsa bace? Ta wannan fannin sai ta tattarasu ta watsar ta rungumi Jamal ɗinta. Makarantar kwana mai kyau ta maza ta samar masa saboda tana buƙatar nutsuwar aiwatar da abubuwan dake gabanta.

Wata safiyar Asabar lokacin tana da wata bakwai a gidan ta fito ɓangaren dakunan samarin gidan. Abu take son tambayar Madam Zainaba dake ɗakin Jamal tana gyarawa saboda washegari za a basu hutu. Sanye take da wani lace ruwan madara mara nauyi anyi mata ɗinkin riga da skirt da suka yi

wa jikinta kyau matuƙa. Haj Manga haɗaɗɗiyar mace ce wadda take bawa jikinta da suturunta mahimmanci kamar sauran al'amuran rayuwarta.

Sassanyar iska ke busawa a hanyar saboda swimming pool da yake wurin tare da manyan bishiyun da suke gefe suna kaɗawa. Ɗakin Arƙam ne na farko idan an fito ƙofar ɓangaren nasu sai na Shamsu a tsakiya sannan na Jamal a ƙarshe. Cikin nutsuwa take tafiya har ta iso ƙofar ɗakin Shamsu, ba nufinta ta tsaya a wurin ba sai dai tashin muryoyin da take jiyowa yasa ta dawo da baya ta kara kunne. Alh Audi ne da ta yi tsammanin ya fita mintuna talatin da suka wuce da Shamsu suke sa'insa. Cike da zakuwa ta kalli hagu da damanta ta tabbatar babu kowa sai kawai ta buɗe ƙofar a hankali ta danna kai. Tana sanya ƙafa a cikin falon wata irin iska mara daɗi ta doki hancinta ba arziki tasa hannu ta toshe shi. Alh Audi da Shamsu suna daga cikin uwar ɗakin basu ji shigowarta ba ta lallaɓa ta raɓe daga bakin ƙofa yadda za ta jiyo su sosai. Daga yadda Shamsu yake magana za ka gane yana cikin fushi da ɓacin rai.

"Kai fa ka ce min wannan maganin zai yi"

Alh Audi ya miƙa hannu zai taba shi ya ja da baya, idanunsa sunyi ja sosai. Bai yi fushi ba ya sake miƙa hannu sai da ya riƙo hannun Shamsun na dama ya rufe shi da nasa biyu.

"Kayi haƙuri, idan wannan bai yi ba zan sake neman wani."

Dogon tsaki Shamsu ya ja Haj Manga a ranta ta ce 'ashe ba ni kaɗai ake yi wa ba?' Tana ji yana magana yana cin magani irin na marasa kunya "ni dai na gaji, saboda matsalar nan fa na yarda da karatu a kasar nan. Sannan duk yadda nake da abokai na amma na kasa barin kowa ya kwana a apartment ɗina. Wasu ma sun fara jin haushina ko ina wulakantasu ne saboda na rainasu"

"Ka ƙara haƙuri Shamsu zan yi magana da Dr Madaki, idan maganin asibiti yaƙi sai mu koma na hausa" Alh Audi ya ce cikin rarrashi kamar yana tsoronsa. Wani tsaki ya sake ja zai yi magana Haj Manga ta tura ƙofar tana murmushi. So take idanunta su gane mata irin lalurar da ake ɓoyewa tsakanin uba da ɗan. Da murmushi a fuskarta ta dinga kallonsu tana ƙarewa ɗakin kallo.

"Ashe kuna ciki ina ta sallama ba a amsa ba?"

Rai a ɓace Alh Audi ya ce "mene ne ya shigo dake?"

Shamsu kuwa fargaba ce ƙarara ta bayyana akan fuskarsa ya yi tsuru-tsuru dashi. Cikin halin ko in kula kamar bata ga sauyin yanayinsu ba ta bawa Alh Audi amsa,

"Wani bashi-bashi nake ji daga waje shi ne na shigo in gani idan ɗakin ne babu gyara na turo Mercy"

Ganin ƙofar rufawa kansu asiri ta bayyana gareshi ya yi saurin canja muhallin fushinsa zuwa ga Shamsu,

"Kaga abinda nake faɗa maka ko? Saboda kawai kana taƙamar akwai masu aiki sai ka mayar da kanka ƙazamin ƙarfi da ya ji" ya shiga nuna kayayyakin da suke a yashe a tsakar ɗakin a wuraren da basu kamata ba.

"Kinga fa yadda yake zubar da kaya kamar wani ƙanƙanin yaro."

Dariya ce ta taho mata ta gimtseta da ƙyar. 'Wai ni zaku rainawa wayo' ta ce a zuci tana bin Shamsu da kallon ƙurilla. Sai da ta farga kamar su ɗin ma kallon da suke yi mata kenan ta yi saurin canja yanayinta zuwa na mai lallashi.

"Kayi haƙuri Alhaji haka samarin suke yanzu. Zan turo Mercy ɗin ta gyara, sai ka fito."

Ta juya tana aje takunta akan diga-diganta cike da ƙasaita. Ajiyar zuciya suka saki duka su biyun, hankalinsu ya soma kwanciya da Allah Yasa bata ga abinda basa so ta gani ba. Sai dai kafin su ankare ta kuma waigowa. Daga Alhaji har Shamsu sai da gabansu ya faɗi da inda ta kalla. Bata kula da yadda suka yi ba ta ce,

"Uhmm! Alhaji, na ce fita kayi ka dawo ne ko kuwa tun sallamarmu ta ɗazu dama kana nan?"

Haɗa kalmomi ya soma yi cikin gargadar harshe irin na marasa gaskiya "ni ko? Au ashe fa ban faɗa miki ba cewa naji labarin result ɗinsu ya fito shi ne nazo dubawa"

Ta san sarai ƙwai ya saki sai ta dawo tana murmushi su kuwa gaba na faɗuwa "Shamsu ɗauko mu gani nasa albarka".

Kawar da kansa ya yi gefe yana ƙunƙuni "shi ma Baban na faɗa masa bai fito ba."

Dama bata sa a ka ba don ta san cewa ya dai faɗa ne domin kawar da hankalinta. Murmushi ta sake yi musu sannan ta kama hanyar fita tana jin muryar Alhaji yana sake nanatawa Shamsu wai ya dinga tsafta. Abinda ya fito da ita bata iya yi ba sai komawa da ta yi ciki tana tunanin me suke ɓoyewa? Wannan tunanin shi ya ɗauke mata hankali musamman ganin Shamsu ya bar gidan ranar da yamma maimakon Litinin da ya saba komawa makaranta.

Maganar dawo da Fanna tana nan daram, Alh Ari ba da wasa yake yi ba. Ya aurar da ita har anyi sakin ta soma idda. Shi da Alh Audi suna ta ɓoyon shirinsu daga gareta sai gashi mahaifiyar Fanna ta tona. Haɗuwa suka yi a wani biki, irin abin nan na mata sai da ta bari wurin da mutane sosai ciki kuwa harda Haj Manga ta kada baki ta ce.

"Daga wannan bikin kuma sai na komen Fanna fa. Ina gayyatar masoya, maƙiya da mahassada kowa yazo ya ga inda ake bikin yar gata."

Matar wani minista sai ta kalli Haj. Kolo ta kalli Haj Manga cike da mamaki ta soma magana.

"Aka ce saki uku ya yi mata har ta sake aure."

"Inji wane sarkin maƙaryatan? Saki ɗaya ne jal!" Haj. Kolo ta bata amsa.

Mata an sami abin da ake so cikin ƙanƙanin lokaci an kasa Alh Audi a faifai kowa tana tofa albarkacin bakinta. Babu wadda ta iya goyon bayan Haj. Kolo akan idon Haj Manga. To ai ido ba mudu ba ya san ƙima, laffayar jikinta kaɗai sai ta sayi suturar jikin wasu cikinsu harda jaka da takalmi duk da kuɗin mazajensu. Gefen bakinta ne kaɗai ya motsa ta yi murmushin nan nata sannan da ido ta yi wa Madam Zainaba alama. Sai da ta tabbatar ta fahimceta ta tafi isar da saƙo sannan ta ce da matan,

"Ai mutuwar aure babu daɗi bare ga ƙaramar yarinya kamar Fanna. Shi ya sa saboda Kulsum na matsantawa Alhajina ya dawo da ita."

Yabo ta soma sha daga matan nan aka bar Haj. Kolo da cizon yatsa. Takaicinta bai ƙaru ba sai da Madam Zainaba ta shigo da Kulsum a hannu. Bacci take yi a bayan mai rainonta ta karɓota tana kuka. Idanunta na sauka akan Haj Manga ta

soma kokawar ƙwacewa daga hannun Madam Zainaba cikin gwarancinta take mika hannu.

"Nanna za ta"

Haj Manga ta tashi daga kan kujerarta ana binta da kallon burgewa, ta karɓota tana sumbatar kumatunta "waye ya saka babyn Nanna kuka?"

Haj. Kolo dai tamkar ta hadɗiyi zuciya saboda cin fuskar da taso yiwa Haj Manga kanta ya dawo. Ana ta fadɗin maganganun da zasu yi mata ciwo kamar bata wurin.

***

Saɓanin yadda ta nuna dakiya da halin ko in kula game da jin komen Fanna da Alh Audi ya dawo kuka ya sameta tana yi. Hankalinsa kuwa in ya yi dubu ya tashi ya yi juyin duniya ta sanar dashi damuwarta taƙi. Fita ya yi ya tura aka kira masa Madam Zainaba ta fadɗa masa ƙarya da gaskiya. Nuna masa ta yi bayan Haj. Kolo ta yi maganar zai mayar da yarta sai aka hadɗewa Haj Manga kai ana ta zaginta a bainar jama'a.

Fuskarsa tuni ta kadɗa ta koma abin tsoro, a haka ya ɗauki waya ya kira Alh Ari ya sauke masa fushinsa tare da dogon gargadi. Ba don girman sirrin da Alh Arin ya sani ba da babu abinda zaisa ya sake auren Fanna. Duk abinda zai sosa ran Haj Manga baya ƙaunarsa. Burinsa ta kwantar da ranta su gina rayuwa mai dadɗi fiye da wadda tayi da ƙaninsa. Idan zai sami haka babu abinda zai hana shi sake bada ƙaimi da jajircewa wurin nemo mata ɗan banzan yaron nan da ya jefa shi cikin zargin mutane.

Ranar kwana ya yi yana lallashi tare da manyan alƙawarrurukana yadda zai fifita ta akan Fanna. Sai da ta yi nadamar fushin ƙaryar da ta tsira kuwa saboda yadda ta tsani ya dinga bibiyarta yana yi mata surutai. Da safe bayan ya fita ta kira Baffa Alƙali ta fadɗa masa zancen auren da nuna rashin yarda da ta yi. Yana zaune a ofishinsa lokacin shi kadɗai ya yi murmushi,

"Dama na fadɗa miki akwai wata a ƙasa tsakaninsa da wannan Alh Ari, idan ba haka ba ban ga dalilinsa na goyon bayan aurenki bayan an sakar masa tasa yar ba."

"To yanzu Baffa me ya kamata nayi?"

"Kin yanke shawarar irin kasuwancin da zaki iya yi? Ko har yanzu kina tunanin cewa zaki iya tunkarar Alh Audi baki da kuɗi a hannunki?"

Shiru ta yi bata amsa ba ya cigaba da cewa "Hafsatu da kuɗi ake neman kuɗi, you need power to face Alh Audi. Ki bar ganin ke da yaranki kuna da shares a Karam Holdings, wannan ba zai sauƙaƙa mana raba shi da kamfanin ba domin rama ɗaukan Arƙam."

Har yanzu bai ji ta ce komai ba ya dan murmusa "Hafsatu kuka? Haba don Allah ki dena. Alh Audi ya yi kuskuren taɓa min jika har ya saka ki zubar hawaye. Amma a yadda lamura suke yanzu ko gawar Arƙam aka ɗauko a ɗakinsa ina mai tabbatar miki da cewa babu inda shari'ar za ta je bare a kai ga ƙwatar mana haƙƙinmu."

Hawayen da take yi mara sauti ta goge da bayan hannunta tare da sake ƙanƙame wayar "Baffa lokaci ƙara ja yake yi..."

"Kuma zai ƙara ja muddin baki sakawa zuciyarki haƙuri ba. Wallahi tunda aka kai yanzu Audi bai dawo da Arƙam ba kuma bai faɗi inda yake ba na tabbata ba za mu sami ganinsa nan kusa ba. You need to be strong Manga."

Zuciyarta ke suya da ɓacin rai da tsanar Alh Audi, da ya zaɓi mutuwar mijinta a matsayin lokacin da zai rabata da ɗan da mijin nata yafi so sama da komai a duniya. Datse tunanin da ta san zai raunana mata zuciya ta yi ta tambayi Baffa matakin da za ta ɗauka yanzu. Cikin nutsuwa ya warware mata duka abinda ya tsara ta ajiye wayar tana murmushi.

Alh Audi ya dawo da yamma ya sameta yadda ya barta a ɗakinsa. Babu wanka bare alamun ta fita ko wani ya shigo. Idanunta sunyi jawur ta yi kalar tausayi. Auren gabaɗaya yaji ya fice masa daga rai, ya saki briefcase ɗinsa a ƙasa ya tayar da ita daga kan gadon yana taɓa wuyanta ko akwai zazzaɓi. Bai ji komai ba don kuwa banda rashin wanka ƙalau take, abinci mai rai da lafiya ta take cikinta da shi tunda niyyarta idan ya dawo ko ruwa ba za ta sha ba.

Ya shiga damuwa sosai da ganin yanayinta. Sai yanzu zuciyarsa take ƙara gaskata cewa hadda soyayyarsa ta hana ta aure ba saboda Arƙam kaɗai ba. Yafi kowa sanin abubuwan da suke gabansa masu girma amma tabbas mallakar zuciyar Haj

Manga tana cikin sahun gaba. A wurinsa baki ya yi kaɗan ya kwatanta ta saboda duk inda ake tunanin mace ta wuce.

"Tashi ki yi wanka zan kira Dr. Madaki yazo ya min duba ke"

Tabe baki tayi tana ture hannunsa "ni ka kyaleni idan ma sonka da kishi zasu kasheni ai baka da asara."

"Haba Hafsa me ya kawo zancen mutuwa kuma?" Ya ce a gigice. Hafsan da ya kirata da shi ya sake bata haushi. Duniya Ibrahim kaɗai yake kiranta Hafsatu sai ko Baffanta. Ba ta son jin sunan a bakin Alh Audi ko kaɗan. Fashe masa da kuka ta yi don ta sake ɗaga masa hankali. Tun yana lalashi da baki har ya gaji ya ɗauko cheque book ɗinsa. Zaman dirshan ya yi a gabanta a ƙasa cikin nan nasa shima ya samu wuri ya yi balance.

"Nawa kike so na baki kiyi abinda kike so dabshi?"

Fuskarsa ta kalla zuciyarta fal murna kafin ta nemi kuɗin da Baffa ya ce shi ya bata da kansa. Amma sai ta nuna kamar ya yi mata laifi da yake tunanin kwantar mata da hankali da kuɗi.

"Ba kuɗinka nake so ba kaima ka sani."

"Na sani to faɗi abinda ki ke buƙata" ya ɗauke littafin zai ɗora akan centre table ta yi saurin dakatar da shi. Wani irin kallo ya shiga jefa mata tamkar mai son karanto cikin zuciyarta. Yanayin kallon nasa sai ya takurata ta gane ta kusa bada kanta. Ba shiri ta wayance tana yi masa hararar wasa.

"Ku maza yanzu haka ku ke yi ne? Idan kuna neman aure sai kuyi ta yiwa ta gida kyautar babu gaira babu dalili"

Dariya ta bashi yadda ta yi da fuska ya ce "Ku ɗin ne sai ana lallaɓaku." Ɗan littafin ya sake buɗewa "blank cheque zan rubuta miki na san ba za ki rubuta abinda zai gurgunta ni ba"

"Da gaske kake Alhaji?"

Bai ce komai ba sai takardar da ya sakawa hannu ya yago ya miƙa mata. Karɓa ta yi tana masa godiya da ƙorafin kada ya ga ta karɓa ya yi murna. Tayi ne kawai saboda ta san cewa itama Fanna yana kashe mata kuɗi.

"Mata sarakan kishi, tashi kiyi wanka mu ci abinci Hafsatuna"

'Wai Hafsatunsa? Allah Ya isa!' ta ce a zuci. A zahiri ta sakar masa kyakkyawan murmushi sannan ta mike zuwa banɗaki. Ita kanta yau taji babu daɗi saboda ta wuni ba wanka.

***

Kwanaki sunyi ta tafiya har lokacin da Fanna ta sake dawowa a matsayin matar Alh Audi. Ta sha huɗubar zama da Haj Manga a wurin iyayenta saboda haka da shirinta ta zo gidan. Abu ɗaya ne yake damunta shi ne waɗannan hotuna da Haj Manga ta yi mata barazana dasu. Kwananta ɗaya a gidan ta sallami mai rainon Kulsum aka kawo mata wata daga gidansu. Bayan sati ɗaya kuma aka sallami sauran masu aikin gidan gabaɗayansu aka zuba wasu. Madam Zainaba dai bata taɓuwa duk da ita Alh Audi yafi tsana saboda mugun kusancinta da Haj Manga.

Sannu a hankali Haj Manga ta kula cewa, idan ta sakasu aiki basa yi sai Fanna ta basu izini. Wannan mulkin mallakar sai ya zame mata sabon jari, inda ta yi katari aka yi irin haka akan idon Alh Audi. Ranar Fanna tasha faɗa kamar zai cinyeta ɗanya. Haj Manga kuma domin ya kwantar mata da zuciya, ya ce ta kawo cheque ɗin da ya bata kwanaki saboda ya kula bata yi amfani da shi ba. Wannan kuma huɗubar Baffa ce da ya ce kada ta nuna zalama akan kuɗin. Tana kawowa ya rubuta mata maƙudan kuɗade da ya san cewa idan it ace za ta cike ba za ta dauki rabinsu ba.

Ba ƙaramin girgizata kuɗin suka yi ba, saboda bata san darajar Karam Holdings har ta kai ayi kyautar zunzurutun kuɗi irin waɗannan ba batare da asusu ya girgiza ba. Bata yi ƙasa a gwuiwa ba ta nemi izininsa akan fara kasuwanci ya kuma amince mata. A satin suka tafi Lagos ita da Madam Zainaba. Wani tsohon yaron da suke harkar filaye ta nema akan ya samo mata katon fili a unguwa mai tarin jama'a kuma bakin titi. Harka ta kuɗi sati bai zagayo ba ya kaita wata unguwa Ikoyi. Filin ya yi mata ta kira Baffa Alƙali suka gama tsarin komai sannan ya turo mata hotunan tsarin gini irin na plaza kala goma. Wanda yafi kyau da tsari ta zaɓa ta saki kuɗi aka fara gini.

Mr Bankole yaron da ya nemo filin ne yake kula mata da komai, kafin isowar Kashim sa'anta ɗan gidan Baffan. Su ta sakarwa ragamar ita da Madam Zainaba suka wuce China. Da yake da shirinta dama, shi ya sa basu ɓata lokaci ba. Cikin wata guda aka gama haɗa mata order na kayan gado, kujeru,

kayan yara, kayan ado da ƙyale-ƙyalen mata da kuma kayan wuta na kitchen. Duk wannan abu ba wai ta yi wa Alh Audi dogon bayani bane. Iya abinda ya sani shi ne za ta fara kasuwanci, kuma ta tafi sayen kaya. Amma sauran bayanai ta nuna masa cewa ya jira ta gama, domin tana son ta ba shi mamaki ne. Bai matsa mata ba ya ƙyaleta. Kafin ta baro Chinan ma ya je ya yi sati guda ya dawo.

Rashinta a gidan da kuma rashin bayani daga Alh Audi ya ɗagawa Fanna hankali sosai. Bata san me yake faruwa ba, amma zuciyarta tana raya mata cewa ko mene ne ba alkhairi bane gareta. Kasa haƙuri ta yi ta sanar da Alh Ari shi kuma ya yi amfani da matsayinsa kafin su dawo daga China ya tura canjin masu aiki a gidan Lagos ɗin. Da suka dawo taga sababbin fuskoki bata damu ba. Kwanansu uku suka wuce Abuja.

Fanna ta matsu ta san me Haj Manga take yi wanda ya sa bata damuwa da duk wani hari da take kawo mata na kishi. Harkokin gabanta kawai take yi sai zuwa ziyartar Jamal a makaranta.

Watanin da suka gabata Haj Manga bata hutawa ko kaɗan. Baffa yana Maiduguri yana faɗa mata abubuwan da za ta yi. An gama gini cikin nasara ga kayanta sun iso daga China suna warehouse. Plaza ɗinta kuwa tun kafin a buɗe zancenta ya zaga garin saboda girma da haɗuwa. Hawa shida ne ginin anyi masa ado da gilas. Shaguna biyar ne a sama da ƙasa, bakwai a hawa na huɗu da na biyu sai goma a biyun tsakiya. Yanayin ginin ya bada fasalin ficika mafi karancin coin kafin a dena amfani dasu gabaɗaya. A shaguna goma take son zuba kayanta sauran kuma ta bayar haya. Tun kafin a kammala mutane da dama sun cike form na neman shagon haya a wurin. Duk abinda ya kamata ayi anyi har an saka ranar bikin bude A & J Palace kamar yadda ta saka masa suna da farkon sunan yayanta.

Ana sauran kwana biyu su tafi Lagos bikin Alh Ari ya je ofishin Alh Audi. Sun jima suna tattaunawa wanda duk Alh Ari ne yake ƙoƙarin ankarar da shi manufar fara wannan gagarumin kasuwanci na Haj Manga.

"Idan baka manta ba kwanaki na nemi izininka akan canja ma'aikatan gidanku na Lagos. Ba wani abu ya janyo haka ba sai zargin cewa akwai wata maƙarƙashiya da Haj Manga take

ƙulla maka" Katse shi Alh Audi ya yi ta hanyar ɗaga masa hannu,

"Dakata malam! wai ni mene ne gaminka da iyalina ne? Ina ce Fanna ka ke so na aura kuma na aureta to kuma sa idon na mene ne?"

Ransa ne ya soma baci shima, "ka tsaya na dire kafin ka tari numfashina mana."

"Kai nake sauraro"

Matsowa Alh Ari ya yi ya ranƙwafo kusa da kujerar da Alh Audi yake zaune sosai.

"Yarinyar da na tura mai girki ita na bawa aikin saka ido akan duk wani motsin Haj Manga a cikin gidan. Direbanta shima ni yake yi wa aiki".

"Ba ka ganin kana wuce gona da iri akan lamarin gidana Alh Ari? Ba fa tsoronka nake ji ba don ka san sirrina, na rantse maka abu ne mai sauƙi a wayi gari a nemeka a rasa" Alh Audi ya ce rai a matuƙar ɓace ya tashi ya juya masa baya, "kana iya tafiya ko ma mene ne bani da buƙatar ji. Abu ɗaya nake so da kai, ka ɗauke ido daga duk abinda ya shafi matata".

Zuciya ce ta ciwo Alh Ari ya tashi shima "kudi da ka ke taƙama dasu na fa san tushensu saboda haka kai ba kowan kowa bane Audi."

Kofar ofishin Alh Audi ya kalla da sauri ya juyo a fusace "kana hauka ne? Idan wani ya shigo fa?"

Dariyar ban haushi Alh Ari ya yi, "sai su san kallon kitse suke yiwa lalataccen rogo"

Motsi Alh Audi ya ji saboda tsoro ya tafi da sauri ya buɗe ƙofar. Wurin zaman sakatariyarsa ya kalla ya sauke ajiyar zuciya domin ba ta wurin. Dawowa ya yi ya gwara ƙofar ya koma ya zauna, yana huci kamar wani matashin ɓauna,

"Me Haj Mangan ta yi?"

Sai da Alh Ari ya yi murmushi sannan ya zauna shi ma ya soma faɗa masa maganganun da masu aikin suka kawo masa rahoto. A ciki akwai yawan wayarta da wani Baffa wanda su biyun sun san waye shi a wurinta. Akwai kuma batun idan kasuwa ta buɗe a hankali ta sa Alh Audi ya ƙara mata kuɗi ta buɗe wasu

rassan. Karshen jawabin dai shi ne cewa duk abinda take yi tana yinsa ne domin ta samu ƙofar mallakar ko da rabin Karam Holdings ne sannan ta shigar da ƙara akan ɗanta da ya ɗauka da sunan zai kai shi makaranta.

"Idanunka sun makance da soyayyar ƙarya da take nuna maka. Matar nan bayanka take son gani. Ka taimaka ka faɗa min inda yaron nan yake a bata abinta kowa ya huta."

Alh Audi ya tashi daga kujerar da yake kai ya tunkuɗata baya sai da ta kifa. Zuciyarsa sai tafarfasa take da ɓacin rai ba akan kowa ba kowa sai Arƙam. Datse haƙoransa ya yi yana magana da ƙyar.

"Wannan tsinannen yaro idan bai riga ya mutu ba ni zanyi ajalinsa. Wace irin masifa ce wannan yake neman janyo min. Me zan ci da shi da har ake zargin ni ne na ɓoye shi? Abinda yafi bakanta min rai bai wuce na rashin samun damar aiwatar da nawa kudurin a kansa ba. To ko wannan ne abinda Oga ya gargade ni a kansa?"

Alh Ari yaji daɗi haƙansa ya cimma ruwa ran Alh Audi ya ɓaci. Gyara zamansa ya yi ya ɗora ƙafa ɗaya kan ɗaya tare da kunna sigari yana dariya.

"Ba wannan bane kaɗai matsalarka mutumina, wato na ji daga majiyar da bata ƙarya cewa Haji Lawalli yana ingiza Dada su ma su shigar da ƙara akan yaron nan dai." Ya tashi ya daidaita hannuwan babbar rigarsa, "Ni nayi nan sai mun haɗu."

***

Cikin rashin sanin kwaɓarta ta yi ruwa Haj Manga ta cigaba da shirye shiryenta. Da kanta taje makarantarsu Jamal ta dauko shi saboda shi take so ya buɗe wurin a madadin kansa da yayansa. Duka gidan a safiyar Asabar suka wuce Lagos. Abin da ya bata mamaki bai wuce haɗuwa da iyaye da yan uwan Fanna ba a airport. Daga Maiduguri ma Baffa Alƙali da matarsa Umma sun wuce Lagos ɗin tare da dukkan yayansa su biyar da matansu. Cikin dangin Innar Haj Manga mutum shida aka tura su wakilcesu domin tayata murna.

A can gidansu matan suka sauka gabaɗaya mazan kuma aka kama musu masauki. Bayan sun yi sallah ko abinci bata iya ci ba ta kira Madam Zainaba zasu je taga decoration da aka yi wa babban ɗakin taron da yake hawa na uku a ginin inda za su yi

event ɗinsu washegari. Ɗakin Alh Audi taje ta ƙwanƙwasa masa ƙofa, saboda tana tunanin ko Fanna tana ciki. Ilai kuwa ita ta buɗe tana ta yatsina da karairaya. Daga ciki Alh Audi ya ce ta shigo tare da sallamar Fanna.

"Alhaji sauri nake yi, kaga gobe ne gashi ban je na duba shirin da aka yi ba" ta faɗa daga bakin ƙofar bayan fitar Fanna.

A tsanake ya zo ya ja hannunta cikin ɗakin "ke da fita sai gobe, kinga yadda ki ka soma yin ɗan wuya kuwa? Kullum kina fama kusan shekara baki da nutsuwa. Idan baki huta ba yau goben ba lallai ki moro a wurin ba."

"Don Allah kada ka hanani zuwa, aski ya zo gaban goshi ka haƙura a ƙarasa. Gobe so nake idan kaga abinda nayi ka yaba."

"Ko a haka ma na san cewa na tsinci dami a kala. Masu shirin nan experts ne saboda haka ki kwantar da hankalinki zasu yi abinda ya dace."

Gani ta yi kamar da gaske baya son ta fita ta nuna bata san zance ba, shima kawai sai ya haɗe rai ya soma faɗa. A babu yadda zata yi ta haƙura. Da safe ma ta so ko yaya ta leƙa ya hana dole ta haƙura zuwa ƙarfe huɗu da rabi da zasu tafi.

***

A limousine din Alh Audi zasu tafi wurin taron da matansa. Ya fito sanye da suit ruwan ƙasa wadda ya gagara balle maɓalli saboda tudun cikinsa. A gefensa Fanna ce ta ci ado da wani rantsattsan leshi an zuba gwal sama da ƙasa ana ta firirita. Sai da suka zauna da minti goma ƙwarara sannan Haj Manga ta fito. Atampar aura ce a jikinta wadda ba a gani sosai domin ta lullubeta da haɗaɗɗiiyar laffayar da tasa aka yi mata musamman daga Dubai.

A babarbariyarta sak ta fito duk ƙyashi da hassadar mutum ya san ta wuce sa a. Mutum uku ke kokawar buɗe mata ƙofar ɓangaren dama na motar Jamal ɗinta ya riga su. Ya ƙara tsayi da kyau kamanninsa da mahaifinsa kullum ƙaruwa suke yi. Shekarunsa goma sha shida a lokacin ya soma tara siririn gashin baki. Hannu ya ɗora a kafaɗarta ya miƙawa Madam Zainaba digital camera ɗinsa.

"Daukemu da Nanna kafin ta shiga taro ganinta ya yi min wahala. Kinsanta da sabga ganinta sai an cike form."

"Kaniyarka"

Haj Manga ta ce tana rungumo shi jikinta tare da dariyar wai har yanzu ta kere shi a tsayi. Shamsu da ya ke tsaye a gefe ya yi sana'arsa, wato tsaki ya shige motar da zasu bi. Su ma ana yin hoton kowa ya shiga mota suka mika zuwa mall ɗin.

Yan jarida da mutane sunyi tururuwar cika wurin anata hayaniya, da ƙyar yan sanda su ka zagaye iyalin suka sami damar wucewa cikin gate ɗin. Nan suka yi ta zagayawa gaisawa da manyan baƙi sannan aka taru a gaban wani ƙyalle mai kyau da ya zagaye farfajiyar wurin. Haj Manga ta matso riƙe da hannun Jamal domin karɓar almakashin yanke ƙyallen ya zamana an buɗe wurin sai Alh Audi ya rigata ƙarasawa.

Karɓar almakashin ya yi ya miƙawa Shamsu sannan ya karɓi Kulsum da tasha ado sosai ya ce,

"Ɗauketa ku yanke tare."

Tamkar saukar aradu maganar da shiga kunnuwan Haj Manga domin dena ji ta yi na taƙaitaccen lokaci ma. Ta ɗaga ƙafa kenan cikin wani irin ɓacin rai mara misaltuwa ta ji anyi mata ƙaƙƙarfan riƙo. Juyawa ta yi da niyyar zagin uwa da uban koma waye idanunta suka sauka a cikin na Baffa Alƙali. Kai ya girgiza mata yana mata nuni da ta tsaya a inda take. Kamar wata mai ciwon wuya ta juya da ƙyar tana kallon Shamsu ya saka almakashin a cikin hannun Kulsum sannan ya yanke ƙyallen ya faɗi a ƙasa aka ɗauki sowa da tafi.

Mai gabatarwar ya nuna musu wani ƙaton abu da aka lullube. Alh Audi ya gyaɗawa Shamsu kai bayan ya karɓi loudspeaker ɗin. Shamsu na yaye lulluɓin wurin rubutun da yake ƙarƙashi ya soma walƙiya. Alh Audi ya ce,

"Welcome to S & K Palace, kyauta ce ga yayana Shamsuddeen da Kulsum wanda matata abar alfaharina Haj Hafsatu Manga Bukarti ta taimaka min wurin assasa komai."

Kuka mai tahowa daga ƙasan zuci shi ne ya tasowa Haj Manga, amma duk faɗin wurin Baffanta kaɗai ta yarda yaga rauninta. Saboda wannan dalilin ta maye ɓacin ranta da murmushi a lokacin da Alh Ari ya tako gabanta yana mata godiyar ɗaukar dawainiyar kula da koma na ginin tun daga farko har ƙarshe.

"Tabbas na yarda idan mutum ya yi dacen mace ta gari irinki sai dai ya yi fatan cikawa da imani" ya ce da murmushin

mugunta a fuskarsa. Murmushi itama ta yi sannan ta ja hannun Jamal "muje ka taya yan uwanka murna".

Jikinsa ya yi mugun sanyi saboda ya fahimci me ya faru a wurin. Murya na rawa ya ce "Nanna are you ok?" Bata ce masa komai ba sai ƙarfin riƙon hannunsa da yaji ya sake ƙarfi. Can cikin zuciyarsa ya ce 'Arƙam kana ina?'

***

FGGC Bajoga Gombe State.

"Susu. Ke Suwaida Musa fito fito da sauri" cewar wata yar siririyar matashiyar budurwa a bakin ƙofar hostel ɗinsu. Cornflakes wadda aka kira Susu take sha a lokacin ta miƙawa ɗaya ƙawar tasu da suke group tare su uku ta fito tana murmushi.

"Minasco ta samu ne?"

Hannunta Minasco ta damƙo ta kuma buɗe murya domin dayar ta ji "Aisha ke ba za ki fito ba?"

Aisha din tafi alamun nutsuwa da salihanci cikinsu. Tasowa ta yi ta fito bakin ƙofar ɗakinsu ta samu har sun ɗan yi nisa suna uban shewa da karaɗi irin na yan matan da ke tashen girma. Ware ƙafa ta yi ta cimmasu lokacin da Minasco take cewa.

"Kun manta ma mun ce muna shiga senoir class zamu yi school daughter? Wallahi na hango yan kyawawa a sababbin nan muyi sauri kafin a rigamu."

Ai fa sai murna kowacce tana faɗin yadda za ta ɗinga kulawa da school daughter ɗinta, yadda yaran ba za su dinga ƙyuyar yi musu aiki ko zuwa aike ba. Jin kawunansu su ke yi a sama an gama junior class su ma yanzu manya ne a makaranta. Sun doso wurin da sababbin ɗaliban yan JSS 1 su ke sai su ka tsaya, daga gefe suna jiran Senior Mistress ta gama yi musu magana ga prefects da zasu tafi dasu zuwa hostels da aka basu. Fuskokin yan matan da yawa babu fara'a wasu ma da gani sun ci kukan rabuwa da iyayensu.

Su Minasco yanke shawarar komawa harabar hostel ɗinsu suka yi, idan ya so cikin waɗanda aka turo nan sai su nema saboda sauƙin mu'amala. Basu daɗe ba da komawa sai ga Labour Prefect da yara suna biye da ita. Wasu cikin yan

manyan aji musamman jss2 sune masu taya yaran ɗauko kayansu.

Hannun Minasco Susu ta ji a kafaɗarta tana cewa "ke ce mai son yan kyawawa Susu kallo gefen famfon can ki ga wadda na gano miki."

Aisha murmushi ta yi "kuna da matsala ni zan koma na kwanta kafin a sakani ɗaukar kayan kowa na fasa daughter din."

Babu wadda ta amsa mata tsakanin Minasco da Susu, domin kuwa hankalinsu yana gun wata yar kyakkyawar yarinya mai ɗan jiki da kumatu. Kallo ɗaya za ka yi mata ta burge mutum. Uniform ɗinta ya yi mata kyau saɓanin sauran ɗaliban ita sai washe baki take yi tana yiwa wata yar js2 magana.

"Ke Minasco gano min waccan banzar uwar shisshigi da neman s." Cewar Susu a zafafe.

Minasco itama ta hangota ta yi gaba Susu na biye da ita zuwa gaban yaran, ransu a haɗe kamar waɗanda aka yi wa wani abu.

"Ke Shalewa waye ya baki damar kula school daughter ɗin Susu?" Cewar Minasco yar kanzagin Suwaida da gurɓataccen turancinta saboda ba wani isarta ya yi ba. Shalewa ɗan ja da baya ta yi a tsorace. Susu da kawayenta basu da sauƙi don tasha wahalarsu suna js3 ta shigo js1 kawai saboda yarenta suka kafa mata kahon zuƙa. Tana tsoron yin magana kada su saka ta aikin wahala da ta tambayi yaushe ta zama daughter ɗinta yarinyar da shigowarta kenan makarantar.

"Sorry Senior Amina" ta ce da Minasco tare da taɓa kafaɗar yarinyar "greet them."

Ɗan murmushi yarinyar ta yi ta ce "good evening"

Susu sai kai ya yi wani gingirim, daɗi ya kamata saboda muryar yarinyar da salon turancinta ya burgeta sosai.

"What is your name?"

"Tauhidat"

Minasco ta dara "Susu kin dace wallahi, ke kinji wani rantsattsen suna irin na yan gayu. Kila ma fa yar masu..."

Harara Susu ta jefa mata kada ta zubar musu da aji, ta kama hannun yarinyar har ƙasan zuciyarta tana fatan kada Allah Ya

kawo wata cikin yan ss2 ko ss3 su ƙwace mata daughter. Hanyar shiga hostel su ka nufa Minasco ta kwaso kayan nata tana cewa Shalewa ta tafi tunda ba hostel ɗinsu bane. Tsayuwar dole ce ta kama Susu ba shiri, lokacin da sabuwar daughter ɗinta ta ɗagawa Shalewa hannu.

"Odabo sister mi"

Wani horrified look ta wurga mata "na shiga uku kema yar gidan su oloshi ce?"

Minasco ta zubar da kayan a ƙasa ta ruga gabansu "wai kina nufin bayerabiya ce?"

"Baki ji me ta ce ba? Ke ya sunanki na gaskiya?" Susu ta ce da Hausa.

"Oluwatosin Tauhidat Abayomi amma Tosin ake kirana a gida."

"Kan babban bala'i. Susu kinji wani uban suna? Wato da fakewa zaki yi da hausa ki liƙe mana ko? Sarakan gulma a ɗiba a kaiwa yan uwa" ta dungure kan Tosin.

Rikicewa ta yi ta kasa fahimtar laifinta, ta kalli Shalewa wadda ta yi tsuru itama. Ita kuma mai yi mata murmushi ɗazu yanzu kallon ƙyama take yi mata. Duk da ba wai ta gane hakan bane amma ta fuskanci cewa basa sonta kuma kamar yadda su ka nuna da farko. Tana wannan tunanin Susu ta talle mata ƙeya sai da ta hantsila ƙasa fararen kayanta su ka dame da tabon da yake wurin inda ruwan sama ya kwanta a wani ɗan rami.

Kuka Tosin ta saka Shalewa ta tafi domin taimaka mata, Susu da Minasco kuma su ka nemi hanyar gudu ashe health prefect Ganiyat Saliu ta ga abin da ya faru duk da bata alaƙanta abin da bambancin yare ba. Ita dai kawai abinda ta yi tunani cin zali ne da nuna iko tunda sun shiga senior class abinda makaranta take ƙoƙarin daoilewa saboda ƙorafin iyaye.

"Kneel down there" ta ce da ƙarfi tana tahowa wurin da bulalarta a hannu saboda yau ita ce da duty. Susu da Minasco sun mugun tsanarta saboda itama bayerabiyar ce. Aƙida mara tushe su ka ɗorawa kawunansu saboda yanayin yadda garuruwan ƙasarmu su kan nuna naka-naka ne sauran ƙabilun ƙasar ba mutanen kirki bane.

Da kanta ta ɗago Tauhidat daga cikin taɓon, sannan ta nemi jin ba'asi. Tashin farko Susu sai cewa ta yi bata kula bane ta tureta.

"Karya kike yi, saboda naga lokacin da kika daketa" cewar prefect ɗin sannan ta ɗaga hannu ta yafito Shalewa "ku je ta cire kayan ki kawo min su nan yanzu in bata ta wanke" ta ƙarasa furucin tana nuna Susu. Jin haka yasa ta ɓata rai, ta soma magana ciki-ciki tana murguɗa baki da juya idanu irin na tsagerun makaranta "tabɗi, ni zan wanke mata kaya? To wallahi gara ma ki min bulala na yi tafiyata akan na taɓa ƙazaman kayanta."

Daga nesa kaɗan dasu Head girl Alawiyya ta hango abin da Susu take yi, ranta ya ɓacci kuwa. Da ita Suwaida take taƙama a matsayin yayarta saboda kasancewar iyayensu mata ya da ƙanwa ne. Sai dai kuma halinsu ya sha bambam, har ta kai Alawiyya lokuta da dama ta kan ji kunyar ace su yan uwa ne ma. Rashin kunya da gadara kamar yar wani hamshaƙin maikuɗi. Tahowa ta yi wurin gadan-gadan Susu ciki ya soma hautsinewa saboda Alawiyya bata da sauƙi akan bada horo ga masu laifi. Tana zuwa kuwa ta tambayi Ganiyat ta faɗa mata abinda idonta ya gani. Shalewa ma ta faɗa duk da mugun kallon da su ke watsa mata na zamu gamu dake.

Alawiyya sai ta kama hannun Tauhidat ta saki fuska ita ma a zatonta bahaushiya ce ta ce "maza ki ciro kayan a wanke, kina da wasu ko?"

Murmushin da ya bayyana kyakkyawar wushiryarta ta yi, har ta manta da abinda aka yi mata saboda yarinya ce mai saurin sabo da sakewa da mutane "eh guda uku Papa ya ɗinka min, kuma hadda wasu ance sai babu class in saka. Suna akwatina."

Dariya Minasco ta yi a hankali a daidai kunnen Susu ta ce "mun sami story teller fa, irin wannan zubo zance daga tambaya daya?"

Sunanta Alawiyya ta tambayeta ta faɗa har lokacin da murmushin nan a fuskarta ba ta ɓoye mamakinta ba kuwa ta ce mata "ashe yarenku ɗaya da Ganiyat amma kin fita iya hausa sosai". Suka yi dariya ita da Ganiyat ɗin.

Kai ta gyaɗa cike da jindaɗi ta ce "Broda Shaheed ya fini iyawa, ni kuma na fishi iya yarbanci."

Har zuciyarta Alawiyya sai ta ji yarinyar ta bata sha'awa. Ita da Ganiyat suka haɗata da Shalewa ta je ta cire kayan da su ka ɓaci. Susu kuwa kamar ta mangareta duk wannan murmushin da take yi har tana ayyanawa ko akwai taɓin hankali a tare da ita, idan ba haka ba babu wani alamun fushi akan tureta da ta yi sai sakin baki take tana faman zuba surutu.

A ɓangaren Tauhidat tahowarta makaranta abu ne da ta daɗe tana mafarki. Kullum idan yayanta Shaheed zai koma makaranta yan kayan provision da ake haɗa masa sune suke tsole mata ido saboda akwaita da son zaƘi. Sai dai kuma duk soyayyarta da tafiya bodin ranar tahowa makaranta anyi daru da ita kamar me, taci kuka ta gode Allah. Tunda take bata taɓa barin mamanta ba kullum suna tare. Aunty Bimbo mai abinci kamar yadda yan unguwarsu ke kiranta ta yi ta fama da haihuwa yaran har uku na mutuwa tsakanin Shaheed da Tosin shiyasa ta ke shagwaɓata son rai tana yi mata gata. Sunanta ma Oluwatosin yana nufin kyautar Allah sai dai a gida kaɗai ake kiranta da sunan, a waje musamman makaranta Tauhidat ake kiranta. Duk abinda Bimbo ta samu burinta ta fito da Tosin dinta ta yi kyau, shiyasa ta ke tsaf da ita.

Asalinsu mutanen Abeokuta ne ta jihar Ogun zama ne da neman arziƘi ya kawo iyayen Abayomi mahaifinta Gombe har aka haifeshi da ƙannensa. Lokacin da su ka tashi komawa gida shi kaɗai ne yake aikin direba a gidan wani Sanata sai yaƙi binsu. Ga shi anyi masa aure da Bimbo yar garinsu tana fama da tsohon ciki. A hankali ita ma ta saba da zaman. Bayan Sanata ya sauka ƙuncin rayuwa ya fara dukansa sai ya sallami da yawa cikin ma'aikatansa, azal ta faɗawa Abayomi hadashi. Da yake Aunty Bimbo akwai zafin nema sai ta buɗe gidan abinci a bakin titin unguwarsu.

Tana yin ƙosai mai daɗi da safe da rana zuwa biyar na yamma kuma ta yi amala, tuwon semo, sakwara, teba da miyoyinsu kala-kala na ganye, kuɓewa, ogbono ta saka kifi ko nama da ganda. A gefen shagon Abayomi ya samu yake yin faci da buga iska sannan shi yake zagayawa bayan shagon ya daka mata sakwara. Da Shaheed ya kawo ƙarfi shi ya karɓi dakan. Tauhidat a shagon nan ta buɗi ido tun ƙananan shekaru ta goge sosai da irin girke-girkensu. Yarinya ce kyakkyawa wankan tawarɗa ga ɗan jiki irin wanda turawa ke kira chubby. Bakinta ɗauke yake da wushirya wadda da wuya take ɓuya saboda tsabar murmushi da yawan fara'arta. Idan ka ga

fushinta to lallai abu ya yi tsamari. Bata da gashi sosai amma a cike yake ga wahalar gyara. Wannan dalilin yasa Aunty Bimbo ta yi masa kwas-kwas da za ta taho makaranta. Askewa mata kai ba komai bane a wurin cikakken bayerabe.

Bayan ta cire kayan Ganiyat ta bawa Susu wankinsu, Minasco kuma Alawiyya ta haɗata da masu dawowa makaranta a makare aikin nome ciyayi. Wannan lamari shi ne matakin farko na assasa ƙiyayyar Susu ga Tauhidat. A ganinta ci baya ne da raini a saka ta wankin kayan yar jss1 kuma mutane da yawa sun sani.

***

Kwanaki huɗu kenan da Alh Audi ya juya akalar ƙudirin Haj Manga ta hanyar yi mata bazata ya ƙwace plazar da ta wahala wurin ganin kafuwarta. A ranar da aka yi taron kafin a tashi taji kirjinta yana suya ga wani azababben ciwon kai ya far mata lokaci guda. Bata nemi kowa ba domin gabaɗaya duniya gani take babu wanda kuma ya cancanci ta amince da shi ɗari bisa ɗari sai yayaan cikinta. Jamal ta tura ya samo musu taxi drop zuwa airport. Shi ma ɗin ƙuruciya bata rufe masa ido ya kasa fuskantar cin zarafin da aka yi wa mahaifiyarsa ba. Ya so yiwa Baffa Alƙali magana kafin su tafi amma ta hana.

Sun daki gurbi kuwa domin basu sami jirgi ba, aka sanar dasu jirage masu zuwa Abuja sun gama tashi a ranar sai washegari.

A yadda Haj Manga take jin jikinta ya ɗauki zafi sake kwana a Lagos ba zai yiwu ba. Tasha ta umarci Jamal ya samo mota ta kaisu ya shiga roƙonta da ta yi haƙuri sai gobe. Cikin fushi ta hau shi da faɗa, dolensa ya bi umarninta awa guda basu rufa ba suka ɗauki hanyar Abuja a wata peugeot da ta yi musu shata su kaɗai. A baya ta zauna ta zurfafa a tunani har bata san lokacin da hawaye ya dinga ambaliya akan fuskarta ba. Rabonta da kuka irin wannan tun daren ranar da ta kudiri niyyar auren Alh Audi. Sai yanzu ma take ƙara godewa Allah da bata gayyato kowa daga Kano ba. Ta yi haka ne domin gujewa magana akan Arkam, amma da a gabansu aka yi mata wannan dibar albarkar bata san inda za ta saka kanta ba kuma.

Tafiyar gabansu ba ta wasa bace, domin ba su suka isa Abuja ba sai ƙarfe biyar saura na asuba. Tana saka ƙafarta a cikin gidan da gudu-gudu ta hau sama zuwa ɗakinta. Ko takalmi

bata cire ba ta tafi ta durƙusa a gaban wakekiyar wardrobe ɗinta. Wani akwati ɗan ƙarami ta janyo daga ƙasan ta buɗe cikin sauri. Gabanta ya yi mummunar faɗuwa kuwa, envelop ɗin da take ganin zai zame mata garkuwa wurin juyar da abinda Alh Audi ya yi mata babu shi babu dalilinsa. Zazzage akwatin ta shiga yi tamkar mahaukaciya tana barbaza sauran takardun. Komai nata yana nan, envelop ɗin mai ɗauke da takardun shaidar mallakar fili, takardar izinin ginin da ma ta rigistar sunan wurin a matsayin wurin kasuwanci shi kaɗai ne babu. A take zafin ƙirjinta ya ƙaru ta yi zaman yan bori tare da tuge ɗankwalinta, ƙananun kitson barebarinta suka bazu a gefen fuskarta. A hankali wani irin sanyi ya shiga ratsata ta sulale a wurin a sume.

A can Lagos kuma ko minti biyar basu yi da barin wurin ba Madam Zainaba ta fara nemansu. Ta yi ta kiran wayoyinsu ita da Jamal duka a kashe sai hankalinta ya tashi. Tunaninta bai kawo mata komai ba sama da sun koma gida. Cike da tausayin uwarɗakin nata ta dinga kutsa kai tsakanin mutane zuwa inda ta hango Baffa Alƙali yana magana da yayansa. A ladabce ta faɗa masa Haj Manga ta tafi. Shi ma wayar ya kira yaji shiru ya cewa yayan nasa su zo su tafi wurinta. Suna zuwa tun a bakin gate ya tambayi masu gadi aka sanar da shi babu wanda ya shigo gidan tun bayan fitarsu ɗazu. Nan fa hankalinsu ya ta shi kafin magariba kowa ya san ba a gansu ba.

Ana kiran isha sai ga motocin yan sanda sun shigo gida. Alh Ari ne ya ɗaukosu wai ana zargin an sacesu ne a wurin taro. Baffa sai ji ya yi Alh Audi yana musu bayani.

Fuskarsa ta nuna damuwa sosai kana ganinsa duk ya firgice da alamun alhini ya ce "kwanaki uku kenan tana faɗa min idan ta fita tana jin kamar ana bin bayanta." Ya ja hanci harda kaki ya tofar da majina a gefe sanna ya cigaba "na ɗauki abin wasa har ina cewa ta fiye tsoro ashe gaske ne. Officer ko nawa ku ke bukata zan bayar ni dai kawai a nemo min matata da ɗana."

Ana haka Alh Ari ya amsa waya ya fita, bai jima ba ya dawo tare da ma'aikatan gidajen talabijin na NTA, AIT da DBN sun zo neman rahoto game da sace matar Alh Audi Karam. Abin ma sai ya bawa Baffa Alƙali dariya. Zuciyarsa tuni ta ba shi komai lafiya sai dai ɓacin rai yasa ta yi nisa da gida. Ya tabbatar hakan ba dabara bace domin kuwa Alh Audi amfani zai yi da wannan damar ya turbuɗe fuskarta da ƙasa. Hakan ce

kuwa ta faru aka saito kemara da loudspeaker daidai fuskarsa idanunsa jazur yana amsa tambayoyin yan jarida.

Tambayar farko daga wata mace cikin masu ɗaukan rahoton ita ce "Sir, me za ka iya cewa game da ßatan matarka Haj Hafsatu Manga Bukarti?"

Daga shi sai yar ciki da dogon wando ya cire coat ɗin ya kalli kemarar yanayinsa abin tausayi yana sadda kai ƙasa ya ce, "ɗazu na yi tunanin ko wani mugun abu ne ya faru amma yanzu na fahimce kamar ba haka bane, ina zargin kaina da ßata mata rai har ta yi fushi."

Baffa Alƙali zama ya yi don ba shi da ƙarfin jure tsayuwa yana kallon ikon Allah. Da wani namji ya tambayi Alh Audi da ya yi musu fashin baƙi akan abinda ya ce sai ya duƙar da kai yana magana.

"Kamar yadda ku ka sami labari yau ake bikin buɗe plaza da na gina da sunan yayana. Alal haƙiƙa komai na ginin nan kama daga sayen fili zuwa kammaluwar abinda kuke gani Haj Manga ce ta yi. A yadda na tsara komai zamu mallakawa yayanmu wurin ne."

"Yallaßai wadanne yaya kenan? Naka ko nata? Mun san cewa yaranta biyu na ƙaninka ne."

Alamun ßacin rai Alh Audi ya nuna kafin ya bada amsa.

"Yayan ƙanina ba nawa bane? Ni idan ina ƙirgen yayana huɗu nake cewa. Duk da cewa nawa biyu ne ita ma nata biyu. Kamar yadda nake muku bayani niyyata na mallaka musu wurin su huɗun. Sai aka sami akasi wanda aka bawa kwangilar yin banner ɗin sunan wurin jin ance yayana sai ya saka farkon sunan Shamsu da Kulsum. Mun riga mun saba aiki da shi, cewa na yi kawai ya saka farkon harufan sunayensu."

Katse shi aka yi daga gidan TV na DBN inda mutumin ya ce "amma kowa ya ji lokacin da ka ce S & K palace na yayanka ne."

Ko ɗar bai ji ba ya ba shi amsa da cewa "nima ba ƙaramin mamaki na yi ba da Shamsu ya buɗe naga harufan basu cika ba. To amma abu na mutane da yawa ga ku yan jarida da na nuna kuskuren daga gareni ne ban sa an duba banner ɗin ba an tabbatar komai daidai kafin a fara taron sai ace Alh Audi is careless..." ya yi wata siririyar dariya. "Gudun haka yasa na

gabatar da shi da sunan da yake jiki tare da niyyar gyarawa idan an gama. Na san dole ta ji haushi tunda tun farko na faɗa mata harda nata yaran. Kun san matan nan ba dai kishi ba, gani za ta yi kamar na ware nata" ya kuma yin dariya a zuwan wasa yake yi.

"Haɗin gwiwa kenan ku ka yi na kuɗin da aka yi komai dasu?" Wani ya sake tambaya.

Murmushi ya yi wannan karon, irin murmushin nan da yake nuni da mutum bai ɗauki kansa komai ba.

"Ko kaɗan, kuɗi dai nine na bata domin kyautatawa da kuma ganin ita ce uwargida sai na bar mata ragamar a hannunta."

Mutanen da suke wurin cikin yan uwansu Fanna da abokansu suka soma ƙananun maganganu. Alh Audi ya ƙare jawabinsa da ban haƙuri ga uwaigida sarautar mata. Jama'a sun jinjina masa yayin da yan jaridar duka suka matsa gefe domin ƙarƙare rahoton ta hanyar jawabin ƙarshe. Dukkaninsu sun ƙare bayanansu da nuna cewa Haj Manga bata kyauta ba saboda ta yi hukunci cikin fushi. Za su cigaba da bibiyar binciken yan sanda har zuwa lokacin da za a ganta. Bayan tafiyarsu Alh Audi ya ƙarasa inda Baffa Alƙali yake zaune ya durƙusa a ƙasa yana ba shi haƙuri. Takarda Tony PA ya miƙo masa ya warware a gabansa sannan ya nuna masa.

Kallo ɗaya Baffa ya yi mata ya ƙaƙalo murmushin ƙarfin hali ya ajiye a saitinsa. "Allah Ya tayasu riƙo, haɗasu su huɗun zai ƙara musu zumunci ai."

Daga haka bai ƙara magana ba ya ta shi su ka tafi masaukinsu shi da su Ali. Kafin gari ya waye duk wanda ya kalli AIT ko NTA a ranar da wahala idan zuciyarsa bata cika da tausayin Alh. Audi da jin haushin Haj. Manga ba. Da yawa kallon mace mai kishi da son kai suke mata. Saboda anyi kuskuren cire sunan nata yayan shi ne ta gudu daga wurin taro don baƙinciki.

***

Wuraren takwas na safe ta buɗe ido ta ganta kwance akan gadonta, an ɗaura mata drip a hannu ga Jamal yana ta gyangyaɗi daga zaune akan gadon saitin kanta. Ciwon kan nata ya yi sauƙi sai nauyin jiki.

Tambayar Jamal take shirin yi me ya sameta ya ta shi ya fita. Bai daɗe ba suka dawo tare da Dr. Samson Madaki da ɗaya daga cikin masu aikin gidan. Da taimakon Jamal ta zauna bayanta jingine da pillow.

"Jamal bamu wuri ko..."

Dr. Madaki ya ce da shi. Fita ya yi yana kallon mai aikin da nufin ta fito itama. Likitan sai ya girgiza kai ya nuna ba sai ta fita ba.

"Doctor me ya sameni?" Haj. Manga ta tambaya a raunane.

"Hajiya kina wasa da lafiyarki gashi cikin jikinki yana gab da zubewa."

Wannan ita ce amsar da ya bayar wadda ta girgizata. Yana lura da yadda mai aikin tasu ta wangale idanu da baki don mamaki da gulma. Ita kuwa tamkar an watsa mata ruwan zafi ta ce,

"Ciki ne dani? Garin ...."

Bai barta ta ƙarasa ba ya katseta da sauri, "na sani muna iya ƙoƙarinmu domin ganin cikin nan ya zauna. Amma laifina ne, da na san cewa ba kya gari ba zan kiraki ba. An bani tabbacin cewa maganin yana taimakawa matan da ciki yake musu barazanar fita shi ya sa nace ki taho asibitin saboda aiki ya yi min yawa."

Mamaki kasheni in ban mutu ba ta ce da kanta a zuci. Gabaɗaya maganganun Dr. Madaki babu wadda ta yi ma'ana bare ta fahimta. Mai aikin bata kula da ruɗanin da ya bayyana akan fuskarta ba ta fita bayan likitan ya bata umarnin taje ta kawo mata farfesu. Da azama don kada a ci gaba da bayani bata ji ba ta ce,

"Akwai na kaza yanzu na gama dama."

Dakatar da ita ya yi,

"Ba shi ya kamata ta sha ba."

Ta murmusa,

"Akwai na kayan ciki dana kifi duka da safen nan muka yi saboda ance su Alhaji zasu iso da wuri."

Sai da ya nemi wanda bata ce akwai ba ta ce, "Na kashin rago take buƙata. Kiyi sauri kinji, sannan ki tabbatar ya dahu sosai."

Suna jin guntun tsakin da ta saki ta fita rai a ɓace. Ita ce babba cikin sababbin masu aikin gidan, saboda haka ita kaɗai ke da damar shiga dakunan matan gidan. Tana fita Dr. Madaki ya soma yiwa Haj. Manga bayanin da Baffa Alƙali ya yi masa tun daren jiya. Baki ta buɗe cike da tsantsakar mamakin ƙarfin halin Alh. Audi. Wato juya komai ya yi kanta don ya ɓata mata suna bayan rashin adalcin da ya yi mata? Da ya kula cewa ta shiga tashin hankali sai ya fara faɗa mata shawarar da suka yanke da Baffanta.

"A labaran NTA naga komai lokacin kuna hanya ba sani zaki yi ba. Ki kwantar da hankali mun riga mun ɗinke duk wata ɓaraka da tahowar taki ta janyo. Abu ɗaya za ki riƙe shi ne cewa kina da ciki kuma yana baki matsala. Ni kaɗai na san da shi saboda kina gudun kada Alhaji ya ƙwallafa rai kuma ya zube. A jiya na kiraki na faɗa miki an kawo min maganin da nace zai taimaka miki wurin zaunar da cikin..."

"Amma Doctor ka rasa abin cewa sai ciki? Da shekaruna ga kuma history na matsalar da na dinga samu bayan Jamal na rashin zaman ciki, gaskiya wannan shawarar babu mai karɓa." Ta ce tana girgiza kai.

Ɗan dattijon likitan murmushi ya yi mata "waye yace miki mata basa haihuwa da shekaru arba'in da biyu? Ina da magani da aka kawo last week na matsala irin wannan. Ke dai kawai ki tabbatar kinyi abinda ya kamata a gaban yan jarida."

Tana jin ya ce yan jarida ta yaye bargon da aka rufeta ta miƙe. Fita ya yi daga ɗakin tayi wanka da sauri ta yi sallolin da ake binta bashi. Bayan ta gama shiryawa ta kunna wayarta ta kira Baffa da Alh Audi wayarsu bata shiga, ashe suna jirgi sun taho. Saƙon text ɗin Baffan ta gani wanda yake yi mata bayanin shirinsu da Dr. Madaki. Abin sai ya ɗaure mata kai saboda a iya saninta likitan Alh. Audi ne kowa ya sani. Yaushe suka haɗa kai da Baffa da yake Maiduguri bata sani ba? Shaɗaya na safe gida ya cika. Alh Audi da muƙarraban Alh Ari sai su Baffa da wakilan NTA guda uku da aka turo domin jin ta bakin Haj. Manga. Fanna tana gefe tana cika tana batsewa tuni labari ya risketa cewa ciki ne da Haj Manga. Harara ta dinga jefawa ɓangaren da take zaune akan kujera sanye da jallabiya ta yafa babban mayafi ga fuska fayau. Tambayarta reporter ɗin ya yi dalilin biyo motar haya da yamma daga Lagos zuwa Abuja ba tare da sanin mijinta ba. Kallon fuskar Alh Audi ta yi ya kafeta

da idanu babu fara'a ko kaɗan a tare dashi. Wani irin juya idanu ta yi ta murmusa kafin ta soma magana.

"Jiya babbar rana ce a garemu da duka masu ƙaunarmu. Bayan shafe lokaci ina ta kai kawo wurin ganin komai ya tafi daidai kaga ba zan so saboda raina ni ɗaya taron ya lalace ba. Na tabbatar da na faɗawa Alhaji wayar da Dr. Madaki ya yi min shi ma ba zai zauna a wurin ba, ga baki mun tara daga wurare daban-daban. Tsoron da naji ni kaina bai wuce jinin da nake zubarwa ba sakamakon rashin hutun da aikin ya jawo min."

Reporter ɗin ya ce "idan na fahimceki dai rashin fahimta ce ta jawo aka yi tunanin wani abu ne ya sameki jiya. To amma me ya hanaki sanar dasu a waya ko ki faɗawa PA dinki Madam Zainab sunanta ko?"

Murmushin da yafi na ɗazu ta saki "Madam Zainaba tana da ruɗewa, idan na faɗa mata kana ganin ba za ta sanar da Alhaji ba? Wayata da ta Jamal duka ni na kashe. Kai namiji ne ba za ka fahimta sosai ba amma ga mace ta san cewa babu irin wahalar da bama jurewa domin kula da ciki da yayanmu."

"Ko kina da saƙo na ƙarashe ga mutanen da suka shiga tashin hankali a daren jiya?"

"Kwarai kuwa, nagode musu Allah Ya saka da alkhairi. Ina kuma roƙon afuwarsu saboda naso kaina batare da bayar da gamsashshen bayani ba na kamo hanya. Saboda kada na bata taron shiyasa ko direba ban nema daga gidan ba. Ka san idan mace ta daɗe bata haihu ba sam bata ji bata gani." Ta share yar ƙwallarta tana yamutsa fuska kamar wadda take cikin ciwo "ban san da cikin da wuri bane ina ta faɗi tashi akan aikin nan da zan kula da jikina yadda ya kamata."

Kafin a ɗauke kyamarar daga kanta ta riƙe ciki tana jujjuya idanu. Dr Madaki ya taho da sauri yasa aka kamata.Yan jarida dai hankalinsu a tashe suna biye da motar da aka sakata zuwa asibiti. Alh Audi da Alh Ari basu da zaɓin da ya wuce bin bayansu. Su duka biyun an rasa me yin ko tari a motar saboda mamakin da suke ciki. Wannan shi ake cewa reshe ya juye da mujiya.

Zaman rabin awa suka yi sannan Dr Madaki ya fito ya sanar dasu cewa, sai dai ayi haƙuri ta yi ɓarin cikin wata uku na yan biyu. Zuwa yanzu yan jarida sun ƙaru ana ta yabawa jarumta irin ta Haj Manga. Tana cikin wannan yanayi amma saboda

kada ta ɓatawa mijinta shirinsa ta yi ta dauriya gashi cikin da take ta wahala a kansa ya zube.

To yanzu kwanaki huɗu kenan ƙura ta lafa. Takardun plaza har yanzu babu su babu dalilinsu. Baffa ma ya koma Maiduguri bayan dogon jan kunne gareta akan ta kiyaye daga nuna wani canji ko yaya a fuskarta. Ya kuma ƙara mata da ta dena komai ta yi zaman jinyar barin karyar da ta yi kafin ya san me ya kamata su yi a gaba. Game da alaƙarsa da Dr. Madaki kuwa ya sanar da ita cewa ta kwantar da hankalinta. Duk abinda yake da yaƙinin zai yi mata wuya, zai tsaya mata akansa. Ya ƙara tabbatar mata kada ta manta, tana da uban da zai yi komai domin ganin walwalarta.

Maimakon hakan ya kwantar mata da hankali sai ta sami kanta da yawan tunani. A iya saninta babu wanda ya san inda ta ajiye takardun nan sai Madam Zainaba, idan kuwa haka ne kenan da ita aka haɗa baki wurin cutar da ita. Sai dai kuma silar haɗuwarsu tun farko ta sanya mata wasiwasin anya kuwa za ta cuceta? Da abin ya isheta bayan yan kwanaki sai ta yi mata izinin zuwa garinsu ganin yayanta da yan uwa. Da yake bata nuna mata cewar maganar ɓarin ƙarya bane sai ta so kin tafiya a cewarta za ta buƙace ta. Haj Manga sai da ta yi da gaske wurin nuna mata cewa ta warke ta bata sati uku taje ta zaga dangi.

Ranar tafiyar bayan Madam Zainaba ta gama shiryawa ta sauko wani ni'imtaccen falo a ƙasa inda Haj Manga take zaune. Sallama tazo suyi Haj Manga ta ce ta koma ɗakinta akwai atampopi a wata leda ta ɗauko. Tana hawa saman ta janyo jakarta ta ɗauke mata waya ta mayar da ita inda ta ɗauka sannan ta kashe wayar. Da ta dawo sai ta bata guda uku a ciki ta kaiwa yan uwanta mata. Godiya Madam Zainaba ta yi sosai saboda irin shatara ta arzikin da ta haɗa mata.

A hanya ta farga da rashin wayar tana isa gidansu ta karɓi wayar babbar yarta ta kira Haj Manga. Bayan sun gaisa take faɗa mata an sace mata waya.

"Wani tsinanne ne ƙila ya ɗaukar min a mota. Yara za su yi ta gwadawa ko zamu same shi" ta ce cike da takaici.

Tsinuwar nan har zuciyar Haj Manga sai cewa take ba dai ni ba. Haƙuri ta bata da alƙawarin saya mata sabuwa idan ta dawo. Cikin aminci suka yi sallama. Da daddare misalin

shabiyu da rabi ta tashi ta kunna wayar ta shiga dube-duben sakonnin da suke ciki. Idan ka cire nata sauran yawanci daga yaranta ne. Duka nambobin Alh Audi da ta Alh Ari ta saka a wayar ta gwada kira amma suna bai bayyana ba. Alamu sun nuna babu hannun Madam Zainaba, to waye kuma yake bibiyarta?

Gari na wayewa Alh Audi ya shigo kamar yadda ya soma tunda aka ce ta yi bari wai ya zo dubiya. Kadaran-kadahan ta amsa ya tashi ya fita yana yi yana waigenta. Gabaɗaya ta zame masa abar tsoro tunda ta iya mummurɗa magana yanzu har yi ake dashi wai ya yi amfani da ita kuma don wulakanci aka saka sunayen nasa yayan kaɗai. Sai da ya tafi ta sauka ƙasa sanye da riga da zani na atampa ta yi ɗaurin ture ka ga tsiya. Fanna tana zaune da Kulsum amma ganinta yasa ta tashi da yarta tana buga tsaki.

"Ba kya gabana ƙaramar alhaki."

Haj Manga ta ce bayan ta zauna a falon ta ɗora ƙafa ɗaya kan ɗaya tana karkaɗata. Kana ganinta tamkar wata jinin sarauta tana riƙe da waya a hannu. Minti biyar bai cika ba da fitar Fanna taji motsi kamar mutum yazo bayan ƙofar falon. A hankali gefen bakinta ya motsa ta murmusa sannan ta ɗauki waya ta ɗora a kunne a zuwan da Madam Zainaba take yi. Doguwar hira ta rinka yi ita kaɗai kafin daga bisani ta ce,

"Yauwa maganar file ɗin nan na takardun filaye a ina ki ka ajiye min ne?"

Jim ta yi kamar tana sauraron amsa sannan ta sake cewa,

"Okay suna cikin akwatin nan ko? Nagode Zainaba." Ta sake yin shiru na ɗan lokaci ta kuma ɗorawa "kada ki damu har yau ko Jamal bai san inda nake ajiye akwatin ba. Alhaji kuma zan bashi mamaki tunda suna hannuna dasu zan yi amfani wurin kwato plaza ɗin."

Rifkatu mai aiki ta naɗe komai ta garzaya ɗakin Fanna ta kai mata rahoto. Gigicewa ta yi tunda ta san sun ɗauke takardun plaza ɗin. Idan akwai wasu Alh Ari sai ya ci mata mutumci yace bata aiki da nutsuwa.

"Maza jeki ki ɗauko min akwatin da sauri kafin ta hawo."

Da Rifkatu ta tafi kai gulma Haj Manga ta koma ɗakinta. Banɗaki ta shiga ta ɗan buɗe ƙofar kaɗan, yadda za ta hango

cikin ɗakin. Can sai gata ta shigo kai tsaye alamun ba yau farau ba ta nufi gaban wardrobe din ta durƙusa. Sai da ta janyo akwatin sannan Haj Manga ta fito gadan-gadan ta yi kanta.

Idanu a waje, ciki ya ƙulle kamar ta saki zawo, ta tashi jiki na rawa za ta gudu. Kafin ta yi taku uku Haj Manga ta damko wuyan rigarta ta juyo da ita ji kake tas, tatas...tas tana surfa mata lafiyayyun maruka. A gigice take kurma ihu saboda azaba sai ga Fanna ta shigo dama tana kusa. Idanun Haj Manga da ta gani ita kanta sai da nata cikin ya tsirga kafin ta fara tambayar me ya faru. Cikin ƙaraji Haj Manga ta haɗasu da Rifkatun ta ƙare musu tanadi.

"Kun ajiye ɓarayi a gida ba dama na yi ajiya sai an ɗauka. Wannan wace irin masifa ce?"

Rifkatu ta rufe bakinta da yake zugin mari a tsorace ta nuna Fanna "Maman Kull..."

Caraf Fanna ta kama yatsan da yake nunota ta hanata ƙarasa magana "dan ubanki ashe kece barauniyar gidan nan ban sani ba? Ina awarwarona da nake ta nema?"

Haj Manga sai da ta yi dariya duk yadda taso daurewa. Da gaske Fanna take jibgar Rifkatu kada ta tona musu asiri. Kyalesu ta yi sai dare da Alh Audi ya dawo ta tayar da zancen bayan tasa an kira sauran masu aikin. Nuna su ta yi ɗaya bayan daya "Alhaji ina so yau a gaban kowa ka shata mana layi ni da duka masu aikin nan kada wadda ta sake kusanto ɗakina."

Kamar bai sami labari daga wurin Fanna ba ya ce tayi masa bayanin laifin me suke yi mata. Rifkatu mai fasasshen baki da kumburarren ido sakamakon dukan da Fanna ta yi mata ta nuna masa da baki "ita na kama a ɗakina taje yi min sata kamar yadda ta saba."

"Me? To ba dai a gidan nan ba, Fanna ki sallameta ta kama gabanta" ya ce yana kumfar baka.

"Ni ban ce a koresu ba sai dai ni ma zan ɗauko nawa da kaina. Zan sa a nemo min direba da mai girki da yi min shara. Kafin su zo bana buƙatar ganin kowa a hanyar ɗakina."

Tashi ta yi sai kuma ta koma ta zauna ta sallami masu aikin ta gyara zama.

"Abu na gaba shi ne ina so a biyani duk abinda Rifkatu ta ɗauka zan baka list tunda matarka ce ta kawo su sai ka ɗauke mata nauyin biyan. Sannan ta sanar dani wanda ta kai wa takardun plaza, satar ashe mai lasisi take yi."

Tana kaiwa nan ta tashi ta barsu. Alh Audi ya buɗe baki ya fi sau biyar amma ya rasa abin cewa. Anya baiyi kuskuren auren Hafsatu Manga ba kuwa?

***

Tauhidat ta sha wahala sosai a hannun Susu. Tun bata jin komai har ta koma ko muryarta taji sai ta kusa sakin fitsari. A haka aka gama zangon farko ranar hutu murna a wurinta ba'a cewa komai. Ta fito da yan kawayenta suna ta hira kowacce da kayanta a gefe tana jiran azo a ɗauketa.

Suna tsaye ta hango Susu ta nufosu tana murmushin mugunta ita da Minasco. Aisha ta gaji da hanasu cin zalin Tauhidat ta zuba musu ido kawai. Jikinta ne ya hau ɓari da ta ganta sai Allah Ya taimaketa kamar daga sama taji muryar mamanta.

"Oluwatosin" ta ce cikin murna tana dariya. Wani irin ihu ta saka ta kwasa a guje ta rungume Aunty Bimbo.

"Maami" ta ce tana ta murna da mamakin zuwanta. Ta yi zaton babanta ne zai zo. Sai da su ka gama rungumar juna ta durƙusa ƙasa ta gaisheta ita kuma tana tambayarta karatu. Duk hirarsu da yarbanci su ke yi Shaheed yana gefe yana yi musu dariya saboda ƙorafin Maami ɗinsu wai yarta ta rame. Duk abinda su ke yi a idon Susu da yar korarta don Aisha ko kai bata ɗaga ba. Dariyar shaƙiyanci su ka hau yi suna kallon daurin zanin Aunty Bimbo da ta yi iya ƙwauri bisa al'adar yarabawa. Minasco ce ta fara nuna mata,

"Mutuniyas ba za ki je kwasar gaisuwa ba wurin babarku?"

Kafaɗarta Susu ta kaiwa duka da ƙarfi "amma kin cuceni, me zai kaini gaishe da dangin Oduduwa masu ɗagaggen ɗaurin zani?"

Maganganun da ɗan ƙarfi su ke yi da gayya tunda sun san cewa Tauhidat tana ji. Hankalinta bai kai garesu ba sai da taji suna binsu a baya duk takun Aunty Bimbo ɗaya sai Susu ta ce,

"Tsingil..."

Minasco kuma ta ce, "zanin babarku" suna dariya harda tafawa.

Karaf a kunnenta kuma ta san da wa su ke duk da ƙuruciyarta don lokacin shekarunta goma sha ɗaya. Amma hakan bai hanata fahimtar munin a yiwa mahaifiyarka dariya ba. Kwace hannunta ta yi daga cikin na Aunty Bimbo ta dumbuji ƙasa hannun hagu da dama ta yi kan Susu kamar wata zakanya. Kafin mutane su gane me yake faruwa ta bangajeta duk tsayinta sai da ta kai ƙasa saboda abin yazo mata a bazata. Tauhidat ta haye ruwan cikinta ta soma tula mata kasa a baki da fuska tana ihu cikin yarabanci tana cewa kada su sake zagin mahaifiyarta.

Aunty Bimbo da Shaheed da sauran mutanen wurin da su ka haɗa da prefects, iyayen yara da malamai aka soma kici-kicin rabasu amma Tauhidat taƙi tashi. Minasco da ta kawowa aminiyarta agaji ma tunkuɗeta ta yi ta faɗi ta fasa baki. Nan da nan wurin ya rikice aka samu aka kwashesu sai ofishin shugabar makarantar.

Idanun Tauhidat a soye Aunty Bimbo tana yi mata faɗa amma ko gezau sai ajiyar zuciya da take yi. Principal tana tare da wasu malamai da prefects aka tambayi me ya faru Tauhidat ta labarta musu harda kwatanta muryoyinsu. Nan fa malamai da prefects su ka shiga kare mata domin kuwa zuwa yanzu da yawansu sun san irin cin zalin da Suwaida take yi mata. Amma duk da haka sai ta ƙaryata.

"Idan ƙarya nake yi mata a rufeni ni kaɗai a makaranta kada naje hutu" cewar Tauhidat hawaye na zubo mata.

Principal ta janyota "babu mai rufe mana Tauhidat a makaranta amma ranar da aka dawo za kiyi aikin wanke toilet saboda kinyi laifin dukan babba, gashi har kin jiwa Amina ciwo" ta nuna Minasco. Godiya sosai Aunty Bimbo ta yi mata tana jaddada cewa za ta ƙara jan kunnen Tauhidat idan sun je gida. Bayan fitarsu Susu da take tsaye jiki duk ƙasa da Minasco mai kumburarren lebe takarda aka basu su zo da iyayensu ranar da za'a dawo makaranta idan ba haka ba kada su dawo gabaɗaya ta gaji da ƙararsu da ake kawowa.

Zumbura baki Susu ta yi ta karɓi takardar a wulakance. Displine master na gani kuwa ya hau jibgarta da dorina amma da yake tsagera ce idonta babu ko ɗigon hawaye bare ta bada

haƙuri. Haka ta dawo harabar makarantar har mahaifinta yazo ɗaukarsu ita da Aisha da Minasco da yake unguwarsu ɗaya a cikin Gombe.

Iyayen Suwaida yan Gombe ne gaba da baya. Su biyar ne a gidansu ita kaɗai ta biyun ƙarshe ce mace. Babban yayansu sunansa Salihu sai Imam, Ridwan, Suwaida da kuma Habibu. Mahaifiyarsu Talatu mutuniyar kirki ce ba sawa ba fitarwa. Babansu tsohon ma'aikacin gwamnatin tarayya ne daga baya ya dawo gida yake aiki da hukumar zabe ta ƙasa reshen jiharsu. Suna da rufin asiri bakin gwargwado basu rasa kuɗin ɗauke buƙatun yau da kullum ba.

Suwaida yarinya ce mai son a yaba mata tun ƙuruciya, ɗabi'ar da ta samo asali daga yawan kambamata da kakarsu Iyalle take yi. Komai sai ta ce Suwaida tafi kowa, kama daga kyau, ƙoƙari ko hankali shiyasa bata ganin girman yayyenta ko kaɗan. Idan ta yi abu aka yabeta gobe dan uwanta ya yi aka yaba sai ta kusa kwana tana kuka. Wannan halayyar tana ɓatawa Talatuwa rai ta yi ta faɗa amma Iyalle da take gidan sai ta hana. Duk wata tsiyar Suwaida da sa hannun kakarta. Ta tashi da son ganin a komai ita ce ta yi zarra shiyasa ƙawaye ma sai da ta duba a unguwarsu waɗanda nata iyayen su ka fi nasu kuɗi, ta fisu kyawun fuska da ƙoƙarin karatu saboda ko kwatance za'ayi a ambaceta da matsayin tana gaba dasu.

Ta sami yadda take so kuwa bayan haɗuwarta da Aisha da Amina (Minasco), sai da suka koma yan koranta saboda suna cin arziƙinta. Minasco tafi Aisha kwantar da kai tamkar wata baiwa sai abinda Suwaida ta ce, Aisha kuwa kafin tafiyar ta yi nisa tana soma wayo ta fuskanci inda ƙawancen yasa gaba sai ta soma ja baya dasu. Kasancewar nata mahaifin yafi na sauran ƙaramin ƙarfi bai sa ta amince da ƙawancen mulkin mallaka ba, sa'arta ta dinga juyata kamar waina. Idan ka ga sunyi wani abu tare harda ita to tabbas tasa kanta ne ba wai son burge Suwaida kamar Minasco ba. Ajinsu ɗaya tun firamare har zuwa yanzu komai nasu tare ne.

A hanyarsu ta komawa gida Susu kamar yadda ta mayar da sunanta, tana gaban mota tana kuka saboda faɗan da Alh Musa yake yi musu akan abinda su ka yi a makaranta. Minasco da Aisha suna baya sunyi shiru. Maimakon faƊan ya yi tasirin sanyaya mata zuciya sai ya zamana cikin hutun nan bata da aiki sai tsara yadda za ta kaya tsakaninta da Tauhidat idan an

koma makaranta. Da anyi magana kowa sai ya kare mata harda Principal, ƙudurin hanata jindaɗin karatun tayi idan ya so a koreta bayan buƙatarta ta biya.

***

Gidan Abayomi sun sha hutunsu cike da ƙaunar juna da haɗin kai. Idan ba ka nufin kowa da sharri, sai Allah Ya buɗa maka a inda kake Ya yi ta sanya maka albarka. Hutu ya ƙare Aunty Bimbo ta kashe ɗan abin hannunta wurin yiwa Tosin ɗinta siyayyar komawa makaranta. Sai dai babu abinda yake birgeta saboda kusantowar kwanakin haɗuwa da Susu. Aunty Bimbo tana lura da ita ta kirata ɗaki ana gobe zasu koma, ta bata shawara akan haƙuri sannan idan anyi mata ba daidai ba ta sanar da malamai. Da kuka su ka rabu washegari Tauhidat ta shige banɗaki ta rufe kanta. Aunty Bimbo sai da ta yi ta rarrashi ƙarshe ma dai goyata ta yi har bakin motar da Abayomi ya yi musu shata. Shaheed ya gama karatu lokacin sai zaman gida kafin a sami kuɗin tura shi Unilag ya fara karatun jami'a.

"Maami bana son komawa a sakani a day" ta ce tana sharce hawaye.

"Ki gama js1 in dai har lokacin ba kya so In sha Allahu zan mayar dake day kinji Oluwatosin ɗina" ta shafa kanta sannan ta soma kwararo mata addu'a su na cewa "Amin" ita da Shaheed da babansu.

Satinsu ɗaya da komawa har ta soma sakewa, saboda Susu ɗauke kai take yi idan sun hadu. Wata Asabar da safe ta gama wankin kayanta ta shanya sai ga Minasco an turo ta kirata. Tun a hanya jikinta yake rawa Minasco ta soma dariya.

"Yau Susu sai ta yi kilishi dake a makarantar nan."

A gaban gadonta ta sami Susu ta ɗora akwatin Tauhidat ɗin akan gadonta ɗakin babu mutane yawancin ɗalibai sun fice. Fuska a murtuke ta nuna mata akwatin.

"Bude ki bani duka madarar da take ciki"

Kai a sunkuye ta ce "senior Susu bani da madara."

Minasco ta yi saurin cewa "Ke, ashe rainin wayon naki ya kai Susu ta saka ki abu ki ki yi saboda kina taƙama da malamai

ko? To bari kiji na faɗa miki ko sau nawa zaki kai ƙararmu sai mun ci moza mun ci faza dinki ehen."

Rantsuwa ta fara cewa babu basu ankara ba Susu ta ɗaga tsohon akwatin ta buga shi da ƙasa sai da ya tsage tana hararta "malama bude ki bani ina da abinyi."

"Eh, eh a buɗe a bamu ko mu ƙarasa shi" cewar Minasco. Durƙusawa Tauhidat ta yi tana duba inda ya tsage sannan ta ce "ni bana shan madara tana saka ni amai shiyasa Maami bata sako min ba"

"Da me ki ke shan cornflakes?"

"Ban iya sha ba, kin gani ma" ta buɗe musu akwatin nata tana zubar kwalla. Susu bata haƙura ba ta dinga dungure mata kai tana lakace mata hanci "yar matsiyata akwatin ma babu wani abin arziki ashe?"

Minasco tana ganin samu da rashi domin kuwa akwatin makare yake da provision ta kasa haƙuri "Susu ga sadin (sirdine) fa. Ki ɗaukar mana da gesha ko gwangwani bibbiyu ne mu raba."

Ita ma hararar ta samu daga Susu, "jiya ban baki gesha ɗin ba?"

Shiru Minasco tayi ita kuma ta mayar da hankalinta ga Tauhidat, "rufe akwatin ki zo kwanata."

Suna tafiya ta fashe da kuka amma ta san zuwa ya zame mata dole. Da jan ƙafa ta isa kwanar tasu ta yi kneel down tun kafin a saka ta. Aisha tana kwance tana karanta littafin Wedlock of the Gods da aka basu assignment na literature ta ganta ta tashi zaune.

"Ke kuma lafiya?" Ta kalli ƙawayenta sai suka ɗauke kai.

"Tunda baki da madara shiga nan kiyi min ƙwai shi nake son ci" Susu ta nunawa mata ƙarƙashin gadonta.

Aisha da sauri ta tashi daga kwanciyar da tayi "Susu me yarinyar nan ta yi miki kuma? Har kin manta me ya faru ranar hutu?"

"Wallahi Aisha baki da kirki, Susu tayi miki komai amma duk motsinta sai kin saka ido kin nuna ba daidai ta yi ba. Idan baki da niyyar tayata ki ɗauke kai mana" inji Minasco mai ƙarin

neman fada. Aisha sai kallon ikon Allah tana gani suka tura Tauhidat ƙarƙashin gadon Susu wai ba za ta fito ba sai ta yi mata ƙwai guda biyu. Da kuka ta shiga suna mata faɗan idan wani ya ji gobe a store zasu kulleta. Store ɗin da kowa yake tsoro dole ta kama bakinta sai ajiyar zuciya. Bayan kimanin minti goma Aisha ta ce su fitar da ita Susu ta hau ta da faɗa ta kuma ƙwace littafin don dama nata ne wai za ta ga da yadda Aishan za ta yi assignment ɗin. Wannan bai bata haushi ba kamar gorin da su ke yi mata da Minasco. Cikin ɓacin rai ta fita daga hostel ɗin gabaɗaya ta barsu. Ba daɗewa aka kaɗa ƙararrawar cin abincin rana suka ce kada ta kuskura ta fito.

Tana takure a kasan gado taci kuka ta ƙoshi fuska ta dame da hawaye da majina har suka dawo. Suwaida ta manta da ita saboda sun rufe gefen gadon da zanin gado da bargo. Minasco kuma tana tsoron magana ta kwaɓe mata kamar yadda aka yi da Aisha ɗazu. Tun shaɗaya da rabi na safe har akayi la'asar tana ƙasan gadon baccin wahala ya kwasheta, jiki kuma ya yi tsami.

***

Kwana biyu kafin ranar da Susu ta tura Tauhidat ƙarƙashin gadonta Aunty Bimbo ta tafi Abeokuta matar ƙaninta ta haihu. Da tunanin Tauhidat ta kwana ta tashi, gari na wayewa ta bawa Abayomi dubu goma wai yaje makarantar ya biya kuɗi a rabata da wannan yarinyar da su ka yi faɗa.

Kin karbar kuɗin ya yi yana murmushi "Abimbola kina da saka abu a rai, irin wannan ke saka yara su goge da zaman duniya fa."

Damuwa ce kwance a fuskarta ta girgiza kai "ni dai zan fi jindaɗi idan aka raba musu ɗaki. Please Papa Shaheed ka je."

Domin ya kwantar mata da hankali ya amince "zani amma ki riƙe kuɗin nima akwai a wurina. Sannan ki fara mana addu'a kinsan Malam Sani ɗinnan direba mai zuwa shagonmu cin abinci?"

"Eh, na gidan Haj Lami da ake bikin yarta ko?"

"Shi fa, wai aikin direba ya yi min tayi a gidan Karam" gani ya yi tayi masa wani irin kallo na rashin fahimta ya soma dariya "gidan Alh Audi Karam."

Idanu Aunty Bimbo ta zaro "Karam fa kace? Papa Shaheed masu kuɗi ne sosai, ance da dollar ake biyan masu aikinsu. Da gaske zai samar maka aiki?"

Abayomi ya dinga dariya saboda yadda ta ruɗe, burinta mijinta ya sami wani aikin saboda yadda yake yawan damuwa kusan ita ke riƙe da gidan.

"Matar Alhajin ce take neman direba da kuma mace mai girki. Ya ce min ta hanyar kamfaninsu su ke ɗaukar masu aikin gidan amma wai ita tana neman mace mai hankali wadda za ta iya yarda da ita. Ban gama gane zancen ba amma na faɗa masa muna so. Ya yi min alƙawarin idan ki ka amince Hajiyar za ta bani aiki a gidan saboda ta fi son masu aure ma."

Aunty Bimbo sarkin addu'a nan ta shiga jero yabo ga Allah tana yi musu addu'ar dacewa da aikin nan. Sai shaɗaya ta tafi tasha bayan sun haɗu da Mal Sani sun nemi alfarmar ya faɗawa Haj. Manga cewa suna son aikin kuma za ta same su da rikon amana. Suna tafiya ya kira Haj Lami yar kanwar mahaifiyar Haj Manga ya faɗa mata. Dama ita ta baiwa cigiyar masu aikin ita kuma ta faɗawa direbansu saboda yana da mutane. Washegari za ta iso Gomben bikin yar Lamin.

To da yake kana naka Allah na nasa kuma ta Allah ita ce daidai. Aunty Bimbo ta tafi da farincikin samun aiki da zai ƙara musu samu ta yadda rayuwar yayanta sanyin idaniyarta zata inganta, har tana hango Shaheed ya tafi makarantar da yake mutuwar so wato Unilag ya fara karatu. Oluwatosin ɗinta kuwa jeka ka dawo za ta nema mata a kusa da gidan aikin nasu a Abuja sai hankalinta yafi kwanciya. Mijinta Abayomi zai ware ya dena yawan damuwa. Ko yaya garin Abuja yake? Ta dinga rayawa a ranta tana murmushi da yawan cewa "Alhamdulillah".

Sun kusa shiga gari bayan awanni a motar wani abu ya soma ƙauri daga gaban bonnet direban ya tafi ya duba. Yana buɗewa daidai da yin bindigar motar gabaɗaya ta kama da wuta. Da shi direban da fasinjojinsa babu wanda ya tsira dukkansu sun ƙone sai fatan Allah Ya jiƙan musulmi baki ɗaya. Abayomi yana ta jiran wayar Aunty Bimbo saboda basu daɗe ba da ta ce sun kusa isa idan ta je gida nan da awa ɗaya za ta kira shi. Shiru babu wayarta sai ya soma gwadawa amma ya kasa samu kuma cajinsa ya yi kasa sosai. Sai ya soma danganta shirun nata da hayaniyar yan uwa ƙila bata sami zama ba. Abu kamar wasa

awa biyu ta wuce a lokacin da yake tsammanin kiran nata sai ya ɗauko wayar da niyyar kiran yayanta aka yi rashin sa'a cajinsa ya ƙare. Zuciyarsa ke matsanancin bugu hankalinsa ya kasa kwanciya ya tada Shaheed suka tafi shagon wani mai renting din CD ya roƙi alfarmar a jona masa chajin amma mutumin ya ce tashi zai yi sai dai ya kawo da safe.

A gidansu Aunty Bimbo su ma hankali ya tashi wayarsu ta karshe ta ce sun kusa shigowa gari. Yayanta ne yake ta kiranta yana kuma kiran Abayomi basa samunsa. Daga baya su ka sami labarin mota kirar J5 ta ƙone a hanya. Tashin hankalinsu bazai faɗu ba yan uwa aka tafi wurin yan sanda domin bincike. Da numbar motar aka kira tashar da ta taso cikin dare ƙarfe ɗaya lokacin an gama kwashe abinda ya yi saura a motar. Ma'aikatan union na tashar sun bada shaidar tabbas wannan mota mai lambar da aka faɗa daga wurinsu ta taso. Wadanda 'yan uwansu ke tsumayin isowarsu su ka nemi a duba sunaye sai gashi a ciki an sami Abimbola Hafsat Abdulwasiu.

Abayomi ya manta rabon da ya raba dare bai runtsa ba sai a wannan ranar. Aunty Bimbo ta kan tsokane shi cewa da ya ɗora kansa a pillow yake fara minshari, sai gashi yau yadda ya ga rana haka ya ga dare saboda rashin samunta. Zuciyarsa a cunkushe tunaninsa ya tsaya cak. Gabanin asuba wani irin bacci mai nauyi ya ɗauke shi ba shi ya farka ba sai goma na safe da matsananincin ciwon kai kamar zai rabe biyu. A kiɗime ya tashi ya fara danna wayarsa da ya bari a jikin caja ko an kawo wuta bai sani ba amma taki kunnuwa. Jiki babu ƙwari ya yi sallar da ta kubuce masa ta asuba sannan ya yi wanka. Ƙaramin falonsu ya duba ya sami bread da flask ɗin tea wanda Shaheed ya ajiye masa. Tunda ya ji gidan shiru ya san ya tafi wurin facinsu a bakin titi. Ko ruwa bai iya kurɓa ba ya fita. Allah cikin ikonSa lokacin Mal Sani ya karyo kwanar layin kenan ya ɗauko Haj Manga daga airport na Bauchi saboda rashinsa a Gombe a wancan lokacin. Rage gudun motar ya yi ya sauke glass ɗin domin su gaisa ya kare da tambaya da fatan Aunty Bimbo ta isa gida lafiya. Cikin hausarsa mai saurin tona masa asiri a gane ba asalin yarensa bane ya ce,

"Mallam Sanni tun jiya na kasa samunta ga rashin caji, ka taimaka min na saka sim card ɗina a wayarka na kirata" damuwa ƙarara a fuskarsa, abinda bai sani ba yana fara maganar hawaye ya soma sauka akan kuncinsa. Wani irin

yanayi yake ciki mara daɗin fasaltawa shiyasa yake ta ambaton Tawakkaltu Alallah a zuci.

Alamar juyawar Mal Sani bayan motar inda Haj Manga ke duba wasu takardu cikin nutsuwa ta ji. Yana son neman izinin tsayawa ya saka sim ɗin da Abayomi ya riga ya miƙo masa amma yana gudun ɓacin ranta. Madam Zainaba da ke zaune a gefe ita ma kallonta take yi. Tana jin idanuwansu a kanta tayi murmushin gefen baki ba tare da ta ɗago kai ba.

"Ashe har yanzu ana soyayya a duniya? bashi ya kira ko hankalinsa zai kwanta."

Muryar da Abayomi ya ji ne ya fargar dashi cewa akwai mutum a bayan motar. Dan duƙawa ya yi duk da ba ya hango komai ta duhun gilashin ya gaishesu sannan hannu na rawa ya karɓi wayar. Tashin farko matarsa ya kira sau biyu shiru sai ya kira yayanta wanda dama gidansa ne za ta je. Yadda yanayin fuskarsa ke sauyawa Haj Manga ta ke karanta tana girgiza kai ta zurfafa cikin tunanin lamuranta da Alh Audi sai ji suka yi Abayomi ya ce,

"(Kana hauka ne)?" da yarensa da babu wanda ya fahimta a cikinsu.

Wata maganar ya kuma saurara daga ɗaya ɓangaren lokaci guda ya faɗi ƙasa kansa ya bugu da mudubin gefen direba. Cikin sauri Mal Sani ya fito haka ma Madam Zainaba, Haj Manga bata motsa ba amma gabanta ya yi mugun faɗuwa. Mutanen kusa dasu sun fara tahowa Mal Sani ya kara wayar a kunnensa. Da yarbanci mutumin ya soma yi masa magana ya yi saurin sanar da shi halin da Abayomi yake ciki da turanci. Muryar yayan Aunty Bimbo dama rawa take yi jin haka ya kama kuka ya faɗa masa halin da ake ciki.

"Innalillahi wa inna ilaihi raji'un."

Mutane su ka ji Mal Sani ya faɗa. Sai aka fara tambayarsa ko Abayomi ne ya cika. Fuskar Aunty Bimbo yake hangowa mai yawan murmushi a kwanakin da ya haɗu da ita da jiya, da ƙyar ya iya haɗa kalmomin da ya ce, "Matarsa ce da ta tafi gida jiya motarsu ta ƙone a hanya ta rasu."

Zance ya riga ya kai bakin titi cewa Abayomi ya suma saboda haka a kunnen Shaheed ya faɗi wannan magana. Yaro ya faɗa kan mahaifinsa yana kuka yayin da ake kokarin samun

farfaɗowarsa. Alhinin mutuwar ya ratsa jama'a, kusan duk waɗanda su ke wurin idan ka cire Haj Manga da Madam Zainaba babu wanda bai san Aunty Bimbo ba. Da aka samu Abayomi ya farfaɗo tashi ya yi yana hawaye mutane suna masa ta'aziyya amma ya kasa cewa komai sai Shaheed ya yiwa nuni da gidansu ya umarce shi da ya hada musu kaya su wuce Abeokuta.

Bayan an rirriƙe shi zuwa gidansa Mal Sani ya koma mota yana yiwa Haj Manga bayani.

"Ita ce mai girkin da na samo miki...Allah mai iko, jiya mun rabu tana ta murnar samun aikinsu ita da mijin ashe ko haɗuwa babu rabo tsakaninku."

Wani irin sanyi ne ya ratsa Haj Manga da jin wannan batu. Hankalinta ya tashi matuƙa ta ji tausayin mutumin ya yi mata wani irin kamu a zuci. Cikin rabin awa Abayomi da ɗansa su ka fito ƙofar gidan jama'a sunyi dafifi ana ta gaisuwa. Wani maƙocinsu ne ya ɗaukesu a babur ɗinsa zuwa tasha su ka ɗauki hanyar Abeokuta uba da ɗan suna hawaye.

***

A ranar da gidan Abayomi su ka tashi da wannan tashin hankali ne kuma Susu ta tura Taihidat ƙarƙashin gadonta ta ce ta yi mata ƙwai. Har akayi la'asar sun manta da yar mutane sai bayan magariba ɗalibai da yawa sun dawo daga cin abincin dare ta farka. Bata sani ba bacci ne ta yi ko suma na tsayin lokacin nan amma da ƙyar ta iya buɗe idanuwanta da su ka yi nauyi. Miƙe takurarren jikinta ta so yi amma babu wata gaba da ta bata haɗin kai sai ma wata irin azaba mai raɗaɗi da take bin sassan jikinta. Mahaifiyarta kawai take buƙata a wannan lokaci shiyasa cikin wata irin dasasshiyar murya da bata fita sosai ta soma kuka tana magana da yarensu.

"Maami kizo, Maami ki kawo musu ƙwai su fito dani, Maaamiiiii."

Kamar wasa wasu yan mata huɗu suna yar hayaniyarsu daga ßangaren daman gadon wata ta dan daga hannu ta ɗora akan laßßanta.

"Shhhhh."

Ta kusa da ita ta firfito da idanu a tsorace "gardi ne?"

"Maaammmiiiii"

Sai akayi sa'a akwai wata yarinya da ake kira Mami a wurin. Idanuwa kanta su ka dawo jikinsu duka a sanyaye.

"Mami kamar fa ke ake kira."

Rai a ɓace cike da tsoro ta ce "inji uban wa? Ance muku sunan gaskiya ne Mami ɗin?"

Wata da cikinta ya kaɗa don tsoro baki na rawa ta ce "amma dai kowa a ɗakin nan ya san sunanki ne. Wallahi ki ɗaga hannu idan aka sake kiran."

Mami sai ta soma ja da baya da baya tana neman hanyar gudu kada a sake kiran sunan sauran su miƙa ta.

"Maaamiii" Tauhidat ta sake kira a wahale.

Da su ka tabbatar dai magana su ke ji kamar daga ƙarƙashin kasa da murya can ƙasa ba bata lokaci su ka soma rige-rigen fita daga ɗakin wasu na faɗuwa wasu na take su. Gudun kafa me naci ban baki ba ake yi cikin kiɗima ana kiran aljanu ne a hostel ɗin su na neman Mami. Susu da su Minasco suna bakin ƙofa dama tare dasu ake gudun gabaɗaya sun manta da wata Tauhidat.

Ƙawayenta guda biyu ne ma rashin ganinta ya dame su tun a wurin shanya. Abinka da ƙuruciya sunyi tunanin aiki seniors ko prefects su ka bata shiyasa basu nemeta ba kada a haɗa dasu. Da aka kaɗa ƙararrawar zuwa cin abincin rana har aka gama basu ganta ba sai su ka fara nema. Sun wahala sosai ga rashin wayo sai ƙarfe shida na yamma ɗaya ta takura akan su faɗawa prefect ko rijiya ta faɗa wurin ɗebo ruwa. Tun kafin su faɗa ɗin su ke kuka, sai da suka yi mai isarsu sannan zancen ya kai kunnen dinning prefect ita kuma ta faɗawa malamar da take da duty ranar aka fara nemanta.

Duk inda ake tunanin ganinta an duba amma babu alamunta. Malamar nan hankalinta yayi mugun tashi bata san me za ta faɗawa Principal ba sai gashi ta hango ɗalibai yuya guda anzo faɗa mata akwai aljanu a hostel dinsu. Salati ta yi yau sai godiyar Allah daga wannan sai wancan. Ɗaya daga cikin masu gadin da ta sa aka kira ta cewa ya nemo masu aikin rijiya a duba ko ta faɗa sannan tabi yaran saboda dare ya soma yi ina za ta kaisu.

Cincirindon ɗalibai ne a bakin hostel ɗin an kasa shiga. Yan manyan aji sun tabbatar mata da cewa tabbas akwai aljana tana kiran Mami, ga kuma Mami a gefe tana kuka kamar ranta zai fita don tsoro. Malamin Qur'ani da yake limanci ta sa aka kira da wasu malamai biyu su ka shiga ɗakin ana addu'a da karatu. Tauhidat ta galabaita ƙarshe ɗan motsin da take iya yi ta ƙasa. Muryar Liman ta ji yana karatu sannan ya ce,

"Su waye ku? Me ku ke nema?"

Da ƙyar ta dan ɗaga murya "Sir nice Tauhidat ku fito dani don Allah."

Sai kallon kallo tsakanin malaman da metron ɗin hostel.

"Kina ina ne?" Ya tambaya jikinsa na bashi mutum ce.

"Kasan gado, Senior Susu ta ce na yi mata ƙwai ne" ta ja ƙarshen tana fashewa da kuka.

Malamar nan mai duty jikinta har tsuma yake yi ta ruga waje ta kira Suwaida saboda ita ta sani mai wannan sunan. Hankalinta a tashe ta biyota za ta ja Minasco ta kwace hannunta ta yi baya. Gaba na faɗuwa ta shiga ɗakin sauran malaman suna tambayar malamar da ta kirawota dalilin kiran ba'a gano matsalar ba. Bata amsa musu ba sai fatan yarinyar da take ta nema ta kasance a wurin. Ɓangaren gadonsu mai hawa biyu ta nuna mata.

"Daga min bedsheet din gadonki."

Dammmm! Ta ji zuciyarta na barazanar fasa mata ƙirji. Sai yanzu ta tuna abinda ta yiwa Tauhidat tun kafin azahar.

"Na shiga uku na" ta ce murya a sarƙe.

Zargin malamar ya tabbata ta haɗe rai,

"Za ki shiga dai mutuniyar banza, daga min nace!"

Hannunta yana rawa ta yaye zanin sai ga alamun yarinya a durƙushe ta cure wuri guda. Liman da wani malami cikin sauri su ka kama gadon gabaɗaya su ka ɗaga shi sama.

"Subhanallahi, Tauhidat ce fa" cewar Metron ɗin ta tafi wurin ta miƙa mata hannu "sannu yar nan tashi kinji."

Tana jan hannun ta saki wata razananniyar kara har waje inda daliban suke suna ji. Ɗaya daga cikin malaman maza ya kalli Suwaida idanunsa zallar ɓacin rai.

"Tun ƙarfe nawa take nan?"

Fitsari ta ji zai zubo mata saboda tsabar rudewa "na..naaa...na manta"

A take malamar nan mai duty ta sambada mata bulalar darbejiyar hannunta a baya ta soma faɗa, "kin manta?"

Gantsarewa ta yi azaba na shigarta tana kai hannu bayanta, "kafin ayi lunch ne Ma."

Sake harzuƙa malamar ta yi. Awanni sama da biyar ta tura 'yar mutane ƙarƙashin gado, ga wahalar da ta sha wurin nemanta tun ɗazu suke yawo sun karaɗe makarantar. Bulalar ta shiga jibgawa Suwaida iya ƙarfinta tana ta kururuwa. A gefensu kuma Tauhidat ta kasa juya hatta wuyanta sai mamanta da take ta kira. Liman a dunƙulen nan da take ya ɗagata su ka yo waje za'a kaita clinic ɗin makaranta. Minasco ta kusa sakin zawo da ta ganta a hannu sai yanzu ta gane dalilin ihun kukan Susu. Da rawar jiki ta matsa kusa da Aisha,

"In kina yiwa Allah kice banda ni aka turata ƙasan gadon."

A kunnenta wata ta faɗa ashe, yarinyar ta riga ta san yadda su ke azabtar da Tauhidat ta kwasa a guje ta shiga ɗakin. Malamai mata biyu ta tarar suna ta yi wa Susu faɗa kamar su cinyeta. Tana sauke nishi ta ce, "Ma harda Amina Falalu"

Suwaida taga haske ko dukan zai ragu ta ce, "eh wallahi mu biyu ne."

Minasco ta kama hanyar banɗaki sai jin kira ta yi kamar daga sama ga mutum biyu sunzo kamota. Rantse-rantse ta soma yi har aka direta gaban malaman nan. Bulala dai a wannan dare anyi musu tafi talatin. Sunyi kuka har sun gaji ga sauran ɗalibai su na ta aibata su. Nos ɗin da take clinic ɗin a lokacin allurai ta fara yiwa Tauhidat sannan ta sa aka samo ruwan zafi aka tubeta Metron ta dinga gasa mata jiki. Kukan ma babu sai gurnani kawai na tsananin ciwo da kiran Maami ta zo ta ɗauketa. An riga an sanar da Principal a daren ta baro gidanta can ɓangaren gidajen malamai ta taho ganinta. Kallo ɗaya ta ganeta, yarinyar da ta yi dambe ce saboda an yiwa mamanta dariya. Zama ta yi aka gama gasa jikin ta tura aka karɓo abinci

a gidanta tasa Metron ta bata, sai dai ko rabi bata iya ci ba ta shiga kwara amai a wahale. Yunwa ta ci ta cinyeta ga jiki ko ina yana ciwo abin tausayi.

***

Manya-manyan mutane ne maza masu faɗa aji a cikin Najeriya, saboda ƙarfin arzikinsu da muƙamai aune a wani madaidaicin falo. Su talatin da shida ne cif-cif, mutum ɗaya daga kowace jiha. Zaune suke a kan kujeru na alfarma sun zagaye ƙaton zagayayyen teburin da yake gabansu. Shugaban tawagar ne akan kujera mafi girma da kyau. Jibgegen mutum ne baƙiƙƙirin mai baƙar aniya. Bayan sun gama tattauna abinda ya zaunar dasu meeting ɗin ranar zasu tafi ya dakatar da Alh Audi.

Ba shi da aka tsayar ba, sauran ma gabaɗaya hankulansu sun tashi. Komawa ya yi ya zauna a ɗofane yana jiran yaji me Ogan nasu zai ce. Sai da ya yi gyaran murya sannan ya ce dashi,

"Audi ka tuna shekarun baya da na faɗa maka cewa babban ɗan Ibrahim zai zame maka barazana a gaba ko?"

Wani irin sanyi da firgici ne ya kama Alh Audi domin kuwa saɓanin kawar da Arƙam da aka ce ya yi bai ma san inda yake ba. A take gumi ya shiga tsatssafo masa ko ta ina tsigar jikinsa ta mimmiƙe. Oga tabe baki ya yi, "ina fata ka yi yadda nace da shi."

Cikin sauri ya ce, "ƙwarai. Sosai kuwa. Oga ai don bana son yawan damunka da surutu ne da tuni na sanar da kai. Shekaru shida kenan tun kafin uwarsa ta gama takaba."

Kai Oga ya gyaɗa, "ka taimaki kanka, yanzu ma akwai wani abin da ya tunkaro ka wanda zai iya rusa duka shirinmu."

Jiki na rawa Alh Audi ya ce "wane iri?"

"Mace ce, macen ma kuma yarinya. Ban san yaushe bane za ta shigo rayuwarka ba."

"Oga to me ya kamata na yi?"

"Shigowarta wajibi ne amma zamowarta sillar tonowar asirinka wannan sai ka so."

Dam! Dam!! Dam!! Gabansa ya tsananta faɗuwa.

Tashi ya yi zai fita, cikin tashin hankalin da ba zai faɗu ba. Duk irin taɓargazar da ya aikata a rayuwarsa babu wadda yafi jin

tsoro kamar wannan babban al'amari da yake da yaƙinin shi Oga yake nufin yarinyar za ta tona.

"Ka nutsu ka yi abinda ya dace, idan ba haka ba komai da ka sani zai lalace." Oga ya ce da shi lokacin da ya kama hannun ƙofa zai murɗa. Bai san lokacin da zuciya ta ciyo shi ba ya ce, "don gwafar ubanta me na yi mata to? Saboda gudun ɓacin rai ni fa ko mata ba na bi duk yawo na."

Wata muguwar dariya mai fitar da razanannen sauti Oga ya yi.

"Banyi tsammanin zan ga alamun karaya a tattare da kai ba Audi."

"To ai, to.. to ai, Oga idan sirrina ya fito fa shikenan tawa ta ƙare" cewar Alh Audi a raunane. Cikin dakakkiyar murya Oga ya ce "sai kayi abin da ya dace."

***

Abayomi ya yi kukan rashin matarsa har ya ji babu daɗi. Bai san da wace kalma zai kwatanta Abimbola ba. Matar da duka neman kuɗinta akansa da yayansa yake ƙarewa. Bata da ƙyashi kuma bata taɓa yi masa gori ba, sai ma dai ta ce lokacin da yake cikin wadata yana direban Sanata meye bai yi musu ba. Zuciyarsa wani irin ƙunci take shiga idan ya kalli yadda Shaheed ya zabge yini guda, bai san yadda zai yi da Tauhidat ba. Yana tausayin yadda rayuwarta za ta koma babu uwa. Yar gata ce a wurin mahaifiyarta abar tattali yanzu za ta soma sabuwar rayuwar maraici.

Iyaa Bayo ita ce surukarsa maman Aunty Bimbo. Tun shigowarsa gidan take suma tana farfaɗowa. Yanzu ma da gari ya waye kwance take cikin mawuyacin hali ta tayarwa da kowa hankali. Suna zaune ana karɓar gaisuwa Bayo yayan Aunty Bimbo wanda ya kira jiya a waya ya ratso ɓangaren dangin Abayomi ya yafito shi da hannu zuwa cikin gidan. Iyaa Bayo tana kuka tana kiran sunan jikarta Oluwatosin ya zauna daga gefe yana jiran bayani. Bayo ya kalle shi da tausayawa "jiya a wayar wani ka saka sim ɗinka ka kirani?"

"Oluwa mi o (Wayyo Allah na)" Abayomi ya ce da ya tuna bai karɓi sim din ba ya taho. Bayo ya katse masa tunani,

"Yanzu na gama waya da mutumin ya ce wai Principal ɗin su Tosin ta kira shi cewa bata da lafiya kuma tana ta kuka."

Matar Bayo ta shiga girgiza kai, "ba dole ba, mahaifiyarta ce fa ta rasu. Taji a jikinta ne"

Wani sabon tashin hankalin, da ƙyar ya tambayi Bayo yanayin jikin nata ya ce shi ma bai sani ba amma da mutumin ya kira ya gaya masa Principal ɗin ta nemi da su je su ɗauketa ta bata hutun sati ɗaya. Karɓar wayar ya yi ya kira Mal Sani ya roƙe shi ya turo masa nambar Principal ɗin ta layin Bayo. Ba jimawa ya turo Abayomi ya kira ya buƙaci ta haɗa shi da Tauhidat.

"Mr Abayomi idan mamanta tana kusa ka fara bata saboda tun jiyan ita take nema. Kuma ina so inyi mata bayanin abinda ya faru ne" ya ji ta faɗa a dan tsorace kamar akwai abinda take son ɓoyewa.

Yawu ya haɗiya sannan ya faɗa mata zancen rasuwar. Principal sai da ta kusa kaiwa ƙasa saboda gigicewa. Ranar hutu fa su ka haɗu ashe shi ne farko kuma ƙarshen ganinta da matar. Ga kuma yarta gaɓoɓinta sun kumbura musamman ƙafafu yaya za ta yi da yarinyar alhali likitan nasu da yazo da safe yace lallai a kaita babban asibiti. Sai ta shiga haɗiyar yawu, ta tattaro ƙarfin hali ta faɗa masa abinda yarsa.

Tun yana tsaye sai da ya zube a ƙasa saboda wani irin baƙinciki da ya saukar masa. Da mahaifiyarta tana nan yaya zata ji an yiwa yarta abu irin wannan? Tambayoyi yan uwa su ke ta yi masa ya dakatar dasu cewa su jira ya sami mafita. Mal Sani ya sake kira dai saboda ba shi da lambar kowa sai tasa ya roƙe shi akan cewa akwai maƙocinsa wanda ya kaisu tasha jiya, ya taimaka ya faɗa masa ya ɗauko Tauhidat zai yi ƙoƙarin dawowa shi kuma ana kwana bakwai. Domin su gaggauta ɗaukota ma ya labarta masa abinda Principal ta ce. Yana yi yan uwansu musamman Iyaa Bayo kukanta ya tsananta ga nisa bare su ɗauko yarsu.

Mal Sani tausayin yarinyar ya kama shi, cikin gidan bikin ya shiga ya faɗawa mai girki ta sanar da Hajiya Lami zai ɗan fita. Jiya bayan suman Abayomi bai san inda ya jefa nasa sim ɗin ba sai da Principal ta kira shi sannan ma ya farga da cewa ba nasa bane a cikin wayar. Taron da aka yi jiya a gidan kuwa yawancin yan unguwar da dama basu je ba musamman yan cikin layin. Sun taru ne a gidan maƙocin Abayomi suna nasu zaman makokin. Babu alaƙa ta jini amma akwai kyakkyawar mu'amala tsakanin Aunty Bimbo da maƙotanta, kowa

alkhairinta yake faɗa. Mai girkin sai ta tsayar da Mal Sani ta shiga cikin gidan bayan ɗan lokaci ta dawo ta kira shi wani falo inda Haj Manga take hakimce akan kujera. Gefenta kuma Haj Lami ce.

"Yauwa don Allah Mal Sani me ya sami Tauhidat ɗin?" Haj Lami ta tambaye shi yana shigowa. Yadda Abayomi ya faɗa masa ya maimaita. Haj Manga bata san lokacin da ta yi jifa da takardun hannunta ba,

"Kace me?"

Duk da ya ɗan tsorata saboda ya kula ita yanzun nan take canjawa. Ana abin arziki ta rikiɗe idan abin nata ya motsa, ya lanƙwasar da kai ya kuma koro mata bayani. Goshinta ta shafa cike da damuwa kamar ta san yarinyar,

"This is serious, yanzu cin zalin da ake yi a boarding schools har ya kai wannan matakin?"

Yunƙurin tashi Mal Sani ya yi saboda isar da saƙon Abayomi ga maƙocinsa, domin yadda yake ta kiran wayar tun zamansa a falon. Haj Manga ta dakatar da shi ta hanyar ɗaga hannunta.

"Kira min mahaifin nata."

Idan ma ya yi mamaki bai nuna ba ya ce mata gashi yana kira ma. Ɗauka yayi ya faɗa masa Haj Manga za ta yi magana da shi sannan ya miƙa mata. Ta'aziyya ta fara yi masa tana iya jin rawar muryarsa sannan ta ɗan dake,

"Mr Abayomi za ka karbi aikin da ku ka yi magana da Mal Sani a gidana?"

Shiru ya yi yan uwa suna ta tambayarsa da hannu me ake cewa a zatonsu da Principal ɗin su Tauhidat yake magana. Ɗan guntun haƙurinta ya nemi ƙarewa,

"Na ce za ka karɓi aikin direban ku dawo Abuja da yayanka?"

Kwaƙwalwarsa ba wani dogon tunani za ta iya ba matsawar bai ji halin da Tosin ke ciki ba ya amsa mata da "eh".

"To madallah, ka kira makarantar yanzu ka faɗa musu cewa zan tura a ɗaukota saboda kada su hanashi."

"Da kanki?"

Ya sami kansa da tambayarta cike da mamaki. Shi da yake jiran wayar maƙocinsa da zai ɗaukota. Tamkar bata ji me ya ce ba ta ɗora ta cewa,

"Gobe zamu koma Abuja zan tafi da ita idan ka gama shiryawa bayan an gama zaman makoki ka samemu a can. Sani zai turo maka kuɗin mota da kwatancen gidan tare da numbar da za ka same ni sai ka turo accout number".

Mal Sani ta miƙawa wayarsa ya tsaya galala don bai taɓa tsammanin haka za ta ce ba. Haj Lami kanta ta yi mamakin yar uwarta balle Madam Zainaba. Buɗaɗɗuun bakunansu ta kalla ta dan taɓe baki ta ce,

"Ka jira zan kawo kuɗin da za ka bayar idan an buƙata a makarantar ina so ka taho mata da takardun transfer" sannan ta bar falon. Tana ɓacewa Madam Zainaba ta kalli Mal Sani da waya a hannu "ka yi masa magana kada dama ta wuce shi mana"

Saurin ɗora wayar ya yi a kunnensa ya ce,

"Abayomi kada ka yi wasa da damarka, aiki tare da Haj Manga ba ƙaramin abu bane. Zan ɗaukota zuwa gidan aikina gobe su wuce."

Ji ya yi abin yayi masa yawa lokaci guda amma kuma yana ganin da gaske dama ce bata kufce musu ba da zai samu inganta rayuwar yaransa musamman Shaheed da ya kasa fara jami'a. Haka nan zuciyarsa kuma ta yarda dasu da yake ya san gidan Haj Lami sun jima a unguwar tun kafin haihuwar Tauhidat. Amincewa ya yi ya kira Principal ɗin ya kwatanta mata Mal Sanin.

Haj Manga kudi ta kawo kamar yadda ta ce ta miƙawa Mal Sani sannan ta umarci Madam Zainaba da ta bishi saboda basu san a halin da zasu riski yarinyar ba. Bayan fitarsu Haj Lami ta nuna jindaɗinta sosai na wannan sauyin hali da ta gani a wurin ƙanwarta. Tashi su ka yi daga falon zuwa wurin sauran danginsu aka cigaba da sha'anin biki.

***

An wayi gari makarantar yan mata dake karamar hukumar Bajoga ta jihar Gombe babu walwala a cikinta sakamakon abinda ya faru jiya. Tun sassafe Susu da Minasco su ke durƙushe akan gwiwoyinsu a ƙofar ofishin Principal ɗin suna

jiran matakin da zata ɗauka akansu banda dukan da aka yi musu jiya.

Bata bi ta kansu ba tana jira azo a ɗauke Tauhidat domin ta sami kulawar yan uwanta. Ga daɗin tashin hankalin jin rasuwar mahaifiyarta. Ta kira meeting na gaggawa ta sanar da malamai tare da neman shawarar hukuncin da yafi dacewa da masu laifin. Malamar da ta yi duty a jiyan ta yi saurin cewa a koresu saboda a ganinta yin haka zai tsoratar da sauran ɗalibai akan cin zalin na ƙasa dasu wato bullying.

Basu tashi daga meeting ɗin ba su Mal.Sani suka iso cikin wata haɗaɗɗiyar mota. Masu gadi suna gani ko tsoron miyagun mutane babu suka wangale musu gate. Mal Sani ya faɗa musu aike ne daga Hajiya Manga matar Alh Audi Karam. Sannan ya tambayi hanyar ofishin Principal aka nuna masa. Kafin su ƙarasa yawancin ɗaliban makaranta kowa ya ga wannan haɗaɗɗiyar mota mai matuƙar kyau kirar jeep saboda an tara su a gaban assembly dukkaninsu.

Madam Zainaba dama idan ka ganta babu yadda za a yi a kirata mai aiki saboda gidan da take ciki ya amsa sunansa, biyanta ake yi da kuɗi masu tsoka ba kowa yake samun wannan alfarma ba. Maigadin da ya biyosu har cikin staff room ya kaisu inda ake meeting. Kada ma wani ya riga shi faɗa ya yi saurin cewa Principal ɗin,

"daga gidan Karam ne, Karam dai da muka sani na ƙasar nan." Ya juya ga Madam Zainaba a lokacin Principal da malamai sun fara miƙewa tsaye "uhmm Hajjaju ziyara ku ka kawo mana ko yara za'a saka a makarantar?"

"Baba Maigadi" Principal ta kira shi ganin yana ta rawar ƙafa "je ka abinka zanyi magana dasu."

Haɗe rai ya yi bai iya ɓoye ɓacin ransa ba, dama haka manyan nan su ke idan sun ga masu kuɗi sai su kankane komai su hana na kasa samun romon arziƙin ya ayyana a ransa kafin ya fita. Iyakarsa bakin ƙofa idan sun fito ya yi niyyar ya kuma rakasu bakin gate kamar wasu makafi. Kofa Principal ta nuna musu,

"Muje office ɗina ko"

"A'a muna sauri ne Tauhidat mu ka zo ɗauka ba zama zamu yi ba" cewar Mal Sani. Irin kallon mamakin da su ke jifansa da shi sai kayi zaton wani abu mara kyau ya fada. Oluwatosin dai

yarinyar da kana ganinta ka san gidansu babu maiƙo ita ce mutane daga gidan Karam su ka zo ɗauka. Hankalin Principal kuwa ya tashi da ta tambayi sunansa ya faɗa ta gane shi ne Mr Abayomi ya faɗa mata zai zo. Yau sun shiga uku ashe yana mu'amala da manyan mutane. Duk ta diririce sai mataimakinta ne ya kaisu nasa office ɗin aka tura malamai mata biyu su ka ɗaukota.

Madam Zainaba jikinta sanyi ya yi da aka kawo Tauhidat. Idanu sun faɗa saboda yunwa gashi duk abinda aka bata sai ya dawo. Sai kuma jikinta da ta kasa taka kafafu ga wuya bata iya karkata shi ko yaya sai taji kamar zai balle. Miƙewa ta yi ta rike kafaɗunta ta ce,

"Mal Sani zamu jiraka a mota ka karɓo takardar da Hajiya ta ce."

Ya so mantawa kuwa ya tambayi nawa ake biya idan za'a bada takardar transfer. Nan fa Vice ya soma bashi haƙuri akan cewa zasu ɗauki mataki akan yaran domin sallamarsu ma za ayi daga makarantar. Idan sun cire Tauhidat me aka yi kenan? Principal tana tsaye tana jinsu ta ce dama Papa Abayomi ya faɗa mata. Sai dai basa karɓar komai, ko ana karɓa ma duba da yanayin da yarsu ta tsinci kanta a ƙarƙashin kulawarsu ba za ta karɓa ba. A take aka ɗauko takardar transfer aka yi cike-cike sannan ya yi musu sallama ya fita. Har bakin mota aka biyoshi suna kara yiwa Tauhidat sannu. Kayanta duk an saka a boot tun safe Matron ta haɗo komai.

Tafiyarsu ke da wuya aka koma kan su Susu. Nambar iyayensu ta cikin file ɗinsu na makaranta aka nema Principal ta ce tana buƙatar ganinsu a ranar ko washegari. Daga baban Susu har na Minasco kasa haƙuri su kayi saboda haka a ranar su ka taho tare tunda dama basu da nisa da juna.

Anyi assembly Principal ta ja kunnen ɗalibai akan yi wa juna sata, kwace, fin ƙarfi da zallunci. Ta sanar dasu irin matakin da zasu dinga ɗauka yanzu babu sassauci sannan a gaban kowa ta miƙawa Suwaida da Amina takardar sallama daga makaranta. Minasco ta saka kuka Susu kuwa zuciya kemas.Baƙincikinta bai wuce ace saboda Tauhidat aka koreta ba. Tana cikin ayyana irin tsanar da ta yi mata a zuci muryar Liman ta katseta.

"Mu yiwa Annabi SAW salati...."

Ɗalibai su ka yi shiru suna sauraronsa yana ta kwararo addu'a da larabci a ƙarshe ya kare da cewa "Allah Ya jiƙan mahaifiyar Tauhidat da sauran musulmi."

Sai a lokacin wata mummunar faɗuwar gaba ta saukarwa Susu saboda sam bata ji lokacin da aka fara zancen rasuwar ba. Me yake faruwa? Bata sami amsoshinta ba sai da Babanta da na Minasco su ka zo aka mayar musu da jawabi.

"Abin baƙinciki Alhaji a lokacin da su ke azabtar da yarinyar nan Allah Ya karbi ran mahaifiyarta, ta yi tafiya motarsu ta kama da wuta babu wanda ya tsira. Yanzu haka da aka tafi da ita sai dai taje ta tarar da babu uwa ga rashin lafiya"

Alh Musa sai ya kalli Principal da ta gama yi musu bayanin komai ya kalli yaran. Ɓacin ransa ba zai kwatantu ba ya ɗaga hannu ya kwaɗawa Susu mari ta ƙanƙame kumatunta da take jin kamar zai zazzago don azaba.

"Ke har kin iya gwadawa na ƙasa dake mugunta ko? Muje gidan zaki ga yadda zan yi dake."

Mal Falalu shi ma ransa a bace don ma bashi da zafi kamar Alh Musan ya ce "saura ɗaya shaidaniyar ita ma ka bata nata rabon."

Kunyar idon mahaifi tabbas ita ta hana Alh Musa haɗawa da Minasco, domin shi yana da saurin fushi. Matsalarsa dama bata wuce Iyalle mahaifiyarsa wadda bata yarda a yiwa Suwaida faɗa. Minti goma ya baiwa yaran su tattaro komatsansu su taho. Bayan fitarsu su ka sake bada haƙuri har nambar Papa Abayomi Alh Musa ya karɓa da alƙawarin zai kira shi.

Susu da Minasco sun zama abin kallo da zunɗe a makaranta. Tun da su ka fito zuwa hostel ake kallonsu sai harara da habaici. Yawancin kowa karin tausayinsa ga Tauhidat ya samo asali ne da jin labarin rasuwar mahaifiyarta. Suna haɗa kaya Aisha ce kaɗai me tayasu Minasco na ta zubar hawaye don yau me rabata da Ummansu sai Allah. Susu kuma tana hango Yaya Salihu yana jibgarta don ta tabbatar dole yana daga cikin masu horata a gida. Rasa makamin dogara ta yi ta yankewa kanta shawarar da take jin za ta fissheta ta daidaici kan gadonta ta yanke jiki ta faɗi tana girgiza jiki da surutai.

Ɗalibai an sami abin yi aka sami masu zuwa sanar da malamai Suwaida Musa tana da aljanu. Da mahaifinta ya ji ransa ya kara ɓaci don ya tabbata ƙarya ne. Cewa ya yi a taimaka masa a kawo ta su tafi. A mota bai ce mata komai ba ta kwanta sharaf tana numfarfashi. Sai da su ka je gida ya sauke su Mal Falalu a farkon layin ya shige cikin madaidaicin gidansa da motar sannan ya fizgota ya shiga duka kamar an aiko shi.

"Ni zaki rainawa wayo?"

Ya faɗa yana ɗaga murya abinda ya fito da jama'ar gidan. Alh Musa baza babbar riga yake yana dukanta. Iyalle ta soma faɗa yaƙi sauraronta.

"Musa zan saɓa maka wallahi."

Mama Talatuwa ta ce "haba Iyalle a gaban yara? Baki san me ta yi ba."

"To ba sai ya faɗa min ba, ina cikin gidan saboda ya nuna min shi ne ubanta ya ke dukanta ba tare da wani bayani ba"

Yau ɗaya dai bai saurareta ba sai da Susu ta dena motsi bare kuka sannan ya shige cikin gidan a fusace. Iyalle ta kama ta amma ganin ta kasa tashi ta ce da Mama ta kama mata ita ciki. Dakin Iyallen aka kwantar da ita sannan ta ce lallai Alh Musa yazo ya faɗa mata me Suwaida ta yi. Kafin ya gama faɗa Mama hadda hawayenta na tausayin Tauhidat amma Iyalle sai cewa ta yi wai su basu san sharrin ƙuruciya bane da su ka kasa yi wa Suwaida uzuri. Takaici bai bar Alh Musa ya ce komai ba.

***

Kuka haiƙan Tauhidat take yiwa su Mal Sani a mota tunda aka buɗe gate din gidan Haj Lami. Dama tunda ta hango shagon abincin mamanta ta ce ya sauketa a wurin yaƙi yana bata haƙuri akan ta bari su je gida. To gashi an shigo layin nasu kuma yana cewa mota zai ajiye ya rakata da kansa. Kukan da take yi ko kusa bashi da alaƙa da tsatstsaman jikinta, haka kawai zuciyarta take wani irin nauyi da raɗaɗin da bata san yadda za ta kwantanta shi ba a kananun shekarunta. Tausayinta sosai ya sake shigar Madam Zainaba ta kamota ta fito da ita daga motar a hankali. Dingisawa ta soma yi ta nufi gate za ta fita harda yi musu godiyar ɗaukota da suka yi.

Madam Zainaba ta ce da ita ta shiga gidan su gaisa da Haj Lami. Duk da ciwon da take ji hankalinta ya yi gida tana ta zubar hawayen da bata san dalilinsu ba ta ce,

"Anti idan naje gida zamu zo tare da Maami."

Wannan abin tausayi da yawa yake Madam Zainaba ta aiyana a zuciyarta. Kasa cewa komai ta yi ta juya da nufin neman agajin Mal Sani sai ganinsa ta yi tare da Haj Manga suna ƙarasowa bakin gate ɗin.

Tun kafin su ƙaraso Haj Manga ta ƙurawa Tauhidat ido tana kallon yadda take kokawa da sakatar gate ɗin. Bayanta take iya gani ta gane yarinyar tana da ɗan jiki ba ramammiya bace. Sauri ta ƙara ta isa kusa da ita ta kama hannunta ta riƙe. Wani irin abu ne ya soki zuciyarta a lokacin da Tauhidat ta dago suka haɗa ido. Tana da son yara sai dai Allah bai bata da yawa ba. Kallonta take yi babu ko kiftawa, fuska ce mai nuni da yarinta da shiga rai. Manyan idanuwanta da suka yi jazur suka ƙanƙance sune suka fara ɗaukar hankalinta kafin ta ji ta yi magana da muryar kuka.

"Anti ina wuni, Anti ki ce su buɗe min in tafi wurin Maami." Tauhidat ta ce duk da tsayi da kwarjinin Haj Manga yaso bata tsoro. Ga mamakin duka mutanen wurin harda Haj Lami kuwa sai gani suka yi Haj Manga ta rage tsayi ta durƙusa a gaban Tauhidat tare da juya mata baya.

"Hau muje in baki abinci da magani sannan in faɗa miki inda Maami ɗin ta tafi."

Ita ma kanta mamakin kanta ta yi shi ya sa ta saki murmushi ba shiri. Tauhidat kuwa kallonsu Mal Sani ta shiga yi sai ta ga suna mata nuni da ta hau. Abinka da ƙuruciya da kuma halinta na saurin sakewa da mutane ba musu ta ɗare ta riƙo wuyan Haj Manga da ta miƙe tsaye da ita. Kanta ta tura daidai kunnenta ta ce,

"Maamin ta yi tafiya ne?"

"Eh shi ne ta ce a kawo min ke" cewar Haj Manga tana tafiya muƙarrabanta suna biye dasu a baya ana kuskus.

"To Anti ke friend ɗinta ce?"

"Nanna zaki dinga ce min, haka yayana suke kirana." Ta bata amsa cike da kulawa. Tauhidat ta karɓi gyaran ba musu

"Nanna ke friend ɗin Maami ce? Ban taɓa ganinki ba. Seat ɗin ku ɗaya a aji? School ɗin su fa a Abeokuta ne ke kuma ga ki a Gombe."

Murmushi mai sauti Haj Manga ta yi. Rabonta da nishaɗi har zuci an kwana biyu. Tana son inquisitive kids (yara masu yawan tambaya). Samun kanta ta yi da cewa.

"A'a amma ni sabuwar mamanki ce, suna na Hafsatu Manga."

Sake ƙwaƙumar wuyanta Tauhidat ta yi tana dariya "na yarda! Sunanku ɗaya da Maami amma ita ba sunan babanta Manga ba."

Bushewa Haj Manga tayi da dariya daidai lokacin da ta sauketa akan doguwar kujerar falo.

"To ita Maami ɗin yaya sunanta?"

Tauhidat tana son komai na mahaifiyarta. Cike da shauƙi ta ce "Abimbola Hafsat Abdulwasiu". Kallon Haj Manga ta yi ta ja da baya kaɗan akan kujerar tana yi mata kallon tuhuma "ki ka ce friend ɗinki ce amma baki san sunanta ba?"

Zamowa ta yi daga kan kujerar tana tunanin fita Haj Manga ta zauna ta mayar da ita zaune kusa da ita. Hannu ta ɗora akan kafaɗarta kamar wasu ƙawaye. Hakan ya yi sanadiyar sanya Tauhidat jin nutsuwa da ita. A hankali daidai fahimtar yaro ta ce,

"Tauhidat, Maami ta yi tafiya ne ta ce ni na koma mamanki. Kafin ta tafi ta ce duk abinda kike so in dinga yi miki. Kuma wai idan kika ki zama a wurina ba za ta dawo ba."

Idanu raurau da hawaye ta shiga girgiza kai tana cewa mamanta ba za ta je wani wuri ta barta ba. Rikice musu ta yi sai da Haj Manga tasa Mal Sani ya kira mata Abayomi a waya. Kwantarwa da Tauhidat hankali ya yi ta hanyar rarrashi. Da ya ce ta bita Abuja gobe zai taho tare da Shaheed nan da kwanaki kadan sai ta ƙara sautin kukan. Tambayarshi ta yi ko zai taho da Maami sai ya kasa bata amsa saboda kukan da ya taho masa ya kashe wayar.

Kafin Tauhidat ta iya magana sallamar mata kusan shabiyar ta ɗauke musu hankali. Akan idon wata cikinsu suka shigo gidan kuma ta hango Tauhidat a bayan mota shi ne ta faɗawa sauran makotan. Mai aiki ce ta kaisu falon inda suka ga Tauhidat tare

da matar da ta ɗauki hankalin dukkansu. Yanayin shigarta da komai nata ya nuna musu ba ƙaramar mace bace.

Wadda suka zo dominta ta ganesu duka shi ya sa ta zuba musu idanu itama ganin suna yi mata wani irin kallo. Wurin zama aka nuna musu suka hau koke-koken tausayi da jajantawa juna tare da ta'aziyya gareta. Da farko bata fahimci me ake yi ba sai da wata ta ce,

"Allah Sarki, shikenan yaran nan sun zama marayu. Tauhidat nafi tausayawa ita ce mace."

Fuska a haɗe Haj Manga ta tashi ta kamo hannunta kafin su fasa ƙwai. Maimakon su fara neman jin ba'asin ko an faɗa mata, kawai sun kama maganganu. Takaici sosai ya kama ta yadda wani zubin mata basa lissafi kafin su saki magana. Tauhidat da wayo ba jimawa ta gano me suke nufi da zantukansu. Jikin matar wanda ya kai su Abayomi tasha ta faɗa a gigice.

"Anti Ma'u ina Maami ta tafi?"

"Tosin sai haƙuri, Aunty Bimbo ta rigamu gidan gaskiya", cewar wata daban tana sharar ƙwalla. Razananniyar ƙara ta sakar musu lokaci guda jikinta ya saki ta faɗi ƙasa. Ba yau ta fara jin kalmar gidan gaskiya ba. Ta riga ta san meye mutuwa tun bayan rasuwar kakanta na wajen uwa shekara ɗaya da rabi da suka wuce. Mata sun fi biyar a kan ta suna salati da kiran sunanta. Ran Haj Manga kuwa in ya yi dubu ya ɓaci. A ganinta rashin hankali ne zai sa a faɗawa yarinya ƙarama rasuwar mahaifiyarta ta wannan sigar. Ko minti goma bata yi da haɗuwa da ita ba amma tana jin kamar akwai wani al'amari mai girma tsakaninsu. Yarinyar ta shiga ranta fiye da zatonta. Da ƙyar suka samu ta buɗe ido tana kuka mai ban tausayi. Cikin fushi kuwa Haj Manga ta soma yiwa matan faɗan abinda suka yi tana janyeta daga jikin wadda ta tallafe mata kai. Su kuma jin haka ya sa suka fara tasu masifar don a iya saninsu dai sun ma fi wannan matar mai ji da kai kusanci da Tauhidat. Shiru ta yi musu kawai ta naɗe hannuwanta a ƙirji tana kallonsu daidai. Kaf ɗinsu tana jin babu wadda ta wuce matsayin ta ɗauketa yar aiki. Madam Zainaba ta aika ɗakin da ta yi masauki ta haɗa mata ruwan zafi a banɗaki sannan ta cicciɓi Tauhidat duk nauyinta ta bi bayanta.

Habawa, ganin haka wasu mutum biyu suka hau faɗan wace ce wannan mai son nuna musu iyakarsu akanta. Yar da aka haifa a gabansu kuma ta tashi cikin yayansu. Idan akwai mai iko da ita duk falon ai bai wuce su ba. Haj Lami na ganin yadda yar uwarta ta juyo a fusace lokacin da suka yi wannan magana ta soma bata haƙuri.

"Jeki ki kula da ita Haj Manga zan yi musu bayani."

To ashe cikinsu akwai wadda take da labarin Haj Lami yar uwar Haj Manga ce. Sunanta ya jima da karaɗe ƙasar saboda arziƙinsu tun ba yau ba. Jiki a sanyaye ta dafa wadda ta fi zaƙalƙalewar.

"Maman Faruku yi shiru haka Haj Manga ce."

Wadda aka kira Maman Faruku wata siririyar mace ce da goyon ɗanta. Yatsina fuska ta yi tana yiwa wadda ta yi mata magana kallon biyu ahu.

"Mangooo, nace Mangooo ƙarewar Manga" ta dinga jan karshen harufan a wulakance. Irin kallon da Haj Lami ta yi mata ne ya rage mata ƙwarin guiwar ci gaba da abinda ta yi niyya. Ita kuwa mai magana ta farko bata fasa ba ta ɗora bayani domin sauran su gane da kyau.

"Matar Alh Audi Karam ce ko Hajiya?" Ta nemi ƙarin haske daga wurin Haj Lami.

"Ita ce, ƙanwa take gareni. Iyayenmu mata ciki ɗaya suka fito."

Wata irin murɗawa cikin Maman Faruku ya yi a take saboda tsabar ruɗewa. Sauran ma jikinsu ba ƙaramin sanyi ya yi ba aka soma rige-rigen saka takalmi. Babu ɓata lokaci kowacce ta fice, Maman Faruku ce a gaba. Tana shiga gida ta roƙi mijinta unguwa saboda tsoron kada a turo kama ta.

***

"Hajiya zauna inyi mata wankan" cewar Madam Zainaba bayan sun samu kan Tauhidat da ƙyar ta dena kuka sai ajiyar zuciya. Hararta ta yi ta sake janyo hannun Tauhidat kusa da ita tana kallon kumburarriyar fuskarta.

"Yi tafiyarki ni ki take so na yi mata ko ya ta?"

Bata iya buɗe baki ba sai gyaɗa kai. Kukan da ta yi ya janyo mata ciwon kai ga zazzaɓi yana neman rufeta saboda dama ba

lafiya ce ta isheta ba. Duk yadda take ƙin ayi mata wanka saboda ganin ita ma fa yanzu ta girma bata iya yiwa Haj Manga musu ba. A da duk juma'a Aunty Bimbo sai ta yi mata da kanta suyi ta rigima. Su cika gidan kuwa da ihunta tana magiya da cewa ta iya. Ita kuma maman tana cewa danƙararriyar daudar sati za ta wanke mata.

Haj Manga a gefen bahon ta zauna ƙafafunta duka biyu suna ciki. Idan ka ganta sai ka rantse ba ita bace wannan matar mai tarin damuwa da abubuwa a gabanta. Zagewa ta yi ta gasa mata jiki da gabobi sosai sannan ta yi mata wanka. Hatta askakken gashin kanta ya sha wanki da shampoo mai kamshi saboda ya soma cika. Wani irin farinciki ke ɗawainiya da zuciyarta tana ganin tamkar cikar burinta ne na samun ya mace. Shuɗaɗɗen mafarkinsu ita da Ibrahim ta hasko bata san lokacin da hawaye ya ziraro daga idanunta ba. Lokacin tana gogewa Tauhidat jiki ne da ƙaton tawul ɗin da ya naɗeta gabaɗaya. Hawayen da ta gani a idon babba sai ya bata tsoro. Jiki na rawa tana daga cikin bahon ita kuma Haj Manga tana ciki har lokacin Tauhidat ta ɗora kanta a kafaɗarta wani kukan yana taho mata. Murya na rawa duk ta dusashe ta ce,

"Nanna kema kukan tafiyar Maami ki ke yi? Ba kin ce mu haƙura ba zamu haɗu watarana."

Sake ƙanƙameta Haj Manga ta yi tana jin sabon ciwon mutuwar tsohon mijinta da ɓatan babban ɗanta. Kuka sosai ta fashe da shi daga ƙasan zuciyarta. Irin kukan da ta daɗe tana son yi amma taurin zuciya da kafiya sun hana. Haj Lami na shiga ɗakin ta jiyo alamun suna cikin banɗakin sai ta leƙa. Yadda ta gansu rungume da juna suna kuka ya taɓa mata zuciya sosai. Ita ma hawaye ne ke barazanar fito mata ta juya a hankali ta fita tare da rufe musu ƙofa. Addu'a take yiwa yar uwarta da fatan Allah Ya kawo mata sanyin zuciya dalilin wannan yarinya. Sauran yan uwansu da ke ƙoƙarin shiga ɗakin ganin yarinyar da aka ce mamanta ta rasu ta hana shiga.

"Ku bari ta shirya su fito."

Shi ta iya ce musu kawai. Tsoron kada sanyi ya kama Tauhidat a cikin banɗakin yasa Haj Manga fito da ita suka koma ɗaki. Ko nauyinta bata ji. Mai ta shafa mata suna hira kamar sun daɗe da sanin juna. Tambayoyi Tauhidat ke yi mata cike da zallar ƙuruciya.

"Dama babba yana kuka Nanna? Ko kema mamanki ta tafi gidan gaskiya ne?"

"Tun ina baby ta tafi" ta bata amsa da murmushi a fuskarta. Mamaki ne ya bayyana a fuskarta ta ce,

"Kai, hmmm to kuma waye ya zama mamanki?"

"Wata ce zan kai ki wurinta ki gaisheta."

Tauhidat ta tuna yadda take kaunar mahaifiyarta sai ta ɗan tura baki,

"To ni dai na girma bana son wata maman, nafi son Maami."

Kaɗa kai da murmushi Haj Manga ta yi tana mamakin kanta da yadda ta yi saurin sakewa da yarinya ƙarama,

"Tunda ke ba kya so ni ina son ki zama mamana."

Kunya ce ta kama Tauhidat ta rufe fuska da tafukan hannayenta tana murmushin da ya sake shigar da ita zuciyar Haj Manga. Ina ita ina zama maman babba?

"Ke ce maman ni daughter dai."

Haj Manga ta girgiza kai "ban yarda ba. Ni ce daughter ke kuma mamana."

Tauhidat ta sake cewa "a'a kece". Ita ma taƙi yarda. Haka suka cigaba da yi suna ta dariya tamkar uwa da yar da suka shaƙu da juna. Madam Zainaba ce ta hawo da akwatinta aka bata kaya a ciki ta saka sannan Haj Manga ta sa aka kawo mata abinci ta ci ta sha panadol. A wurin ta ɓingire bacci mai nauyi ya ɗauketa. Papa Abayomi sau biyu yana sake kira Mal Sani ya kwantar masa da hankali da cewa komai lafiya. Ana can ana cigaba da biki da shirye-shiryen kai amarya banda Haj Manga. Zamanta ta yi a wurin Tauhidat ta rufe taga saboda shigowar sautin kiɗa.

Da za'a tafi kai amarya kuɗi mai kauri ta bata a envelop tare da nasiha amma taƙi binsu. Haj Lami dai kamar wadda aka yiwa bushara saboda canjin da take gani ƙarara a wurin yar uwarta. A wuni ɗaya ta koma Mangan da ta sani, Mangan da take so, Mangan da suka tashi tare.

Washegari suka kama hanyar Abuja. Airport ɗin Bauchi Mal Sani ya kaisu suka hau jirgi zuwa Abuja. Tsoro a wurin Tauhidat ba zai faɗu ba. Cikin lafayar Haj Manga ta shige tana

cewa kayan cikinta zasu zube lokacin da jirgin ya tashi. A firgice take hannunta ɗaya ta tallafe ƙasan cikin nata da shi. Dariya a wurin Haj Manga harda hawaye. Neman damuwar da ta dade da kewaye zuciyarta ta yi ta rasa Madam Zainaba tun tana gimtsewa ita ma sai da ta dara. Ta kuma sanya wannan rana a tarihi domin uwarɗakinta tamkar an sauya mata ita ne.

***

Kwana biyun da Haj Manga bata nan Alh Audi ya yi su ne cikin damuwa da tashin hankali. Maganar da Oga ya faɗa masa game da zuwan yarinyar da za ta taka muhimmiyar rawa wurin watsa lamuransa ke ci masa tuwo a ƙwarya. Idan ya ce ya sami baccin cikakkun awanni goma a cikin kwanakin nan ya yi ƙarya. Fanna ta yi iya yinta wurin son jin damuwarsa babu biyan buƙata. Mahaifinta ta kira ta tambaye shi ko yana da masaniyar abinda ya ke faruwa. Alh Ari da ba ya son ace ga wani abu game da Alh Audi da bai sani ba da hanzarinsa yazo bugun ciki. Da yake mutum ne mai shegiyar kisisina kamar tsohuwar karuwa, da wayo da dabara sai da ya fitar da maganar Oga daga bakin Alh Audi.

Sai da maganar ta riga ta fito ta yi rijista a ƙwaƙwalwar Alh Ari sannan nadama ta dirar wa Alh Audi. Ya rasa garin yaya ya ke bawa Alh Ari makaman da zai iya amfani da shi wurin cin amanarsa ta hanyar faɗa masa sirrukansa. Babu wani abu nashi da ke buƙatar ɓoyo da Alh Ari bai sani ba. Kodayake Alh. Ari shi ne silar haduwarsa da Oga saboda haka damuwa ba tasa bace.

Dariyar riƙaƙƙun yan duniya ya yi sannan ya kada baki ya soma magana "banda abinka tunda dai ya ce zuwanta dole ne meye na tayarwa da kanka hankali? Ai kawai Alhaji ka jira ka ga ɓullowarta sai mu san irin matakin da zamu ɗauka."

Ɗauke kai Alh Audi ya yi saboda ya kula Alh Ari ya na cikin farincikin sake samunsa a tafin hannu. Giyarsa ta gulder ya ke marmarin korawa ko zai ji sa'ida. Karar shigowar mota suka ji daga wurin da suke zaune a cikin ƙawataccen lambun gidan, wanda aka wadata da wuraren zama har biyar kowanne da fasalin bukka daga sama. Ta ƙasan kuma zagayayyen tabur ne da kujeru huɗu sun kewaye shi. Ya manta da batun dawowar Haj Manga saboda ruɗanin da ya ke ciki sai da ya hangota ta cikin kofar gilas ɗin wani falo ta buɗe da nufin zuwa wurinsa. Tun daga nesa ake iya hango fara'ar da ta mamaye fuskarta.

Cikin takun nan nata na isassun mata ta tunkaro su. Alh Ari ya murmusa ganin irin kallon da Alh Audi ya ke mata.

"Ka ga wadda ya kamata ka sanyawa ido ba wata ƙaramar yarinya da baka san lokacin zuwanta ba."

"Ka cire kan ka daga harkar iyalina Ari bana son irin haka" ya amsa masa murya ƙasa-ƙasa saboda ta kusa isowa. Duk irin kyawun da ta yi masa bai mantar da shi cewa ita ɗin kunama ce mai jiran saransa ba. Sakin fuska ya yi yana mayar mata da murmushi har ya rage taku kaɗan ta isa gabansu suka ji wata daddadar murya ta ƙwala mata kira.

"Nanna?"

Ta ce a tsorace saboda barinta da Madam Zainaba ta yi a falon bayan Haj Manga ta fito.

"Gani nan Tauhida, come."

Ta miƙa mata hannu tana jiran ta karaso. Ai tunda ta buɗe ƙofar har dan gudun da ta yi zuwa wurinta da Alh Audi da Alh Ari bakunansu a buɗe suke cike da mamaki da fargaba. Tana isowa Haj Manga ta tsayar da ita a gabanta ta ɗora hannuwanta a kafaɗunta tana sakar musu murmushi.

"Alhaji ga yar da Allah Ya bani amana. Ka tuna na faɗa maka an samar min direba da mai girki a Gombe ko? To Allah Ya yiwa matar rasuwa shekaran jiya. Wannan yarsu ce Tauhida."

Yawun da ya haɗiya mai masifar ɗaci ne ya kusa ƙware shi saboda tambayar da ya ke son yi mata. Murya a kausashe ya ce "ban tari numfashinki ba, ita wannan ɗin a gidana za ta zauna ki ke nufi?"

Gira ɗaya ta dage da yanayin rashin damuwa sannan ta nunawa Tauhidat ɓangaren dabbobi ta ce taje ta kalla. Sai da ta tafi ta kalle shi "haka nake nufi, idan tsarin bai maka ba sai mu koma nawa gidan."

A gigice yake ta kula sannan ya kasa ɗauke ido daga kan Tauhidat. Hannayensa jike da gumi ga laɓɓansa a bushe ya buƙaci Alh Ari ya basu wuri. Ba dai haka ya so amma dole ya miƙe ya koma falon. Wuri ya nuna mata ya ce ta zauna ta yi masa bayani sosai. Ko motsi bata yi ba daga tsayen nan ta faɗa masa abinda ya kamata ya sani.

"Ki ka ce Babanta da yayanta suna tafe ko?"

"In sha Allahu."

"Da na kowa ne, ta zauna a wurinki ɗin kafin su iso. A ɓangaren masu aikin na san akwai spare room da zai ishesu."

Ko sake kallonsa bata yi ba kira Tauhidat suka hau sama ɗakinta. Ranar tare suka kwana don bata yarda da a kaita ɗakin masu aiki ba. Bacci ta yi cike da nutsuwa da mafarke-mafarken da suka sanya zuciyarta jin kamar ana warware mata wani ƙulli. Rayuwarta da uban yayanta ke yi mata gizo. Irin zamansu da shi da tsantsar fitina da sangartar Arƙam. Kaifin tunani da karambanin Jamal sai kuma kyakkyawar fuskar Sa'adiyya ma'abociyar dariya. Yarta mace da ta biyo bayan Arƙam wadda ta rasu tana da shekara ɗaya da kwanaki. Da ta farka cikin dare janyo Tauhidat ta sake yi jikinta tana fatan Allah Ya sanya alkhairi da albarka a haɗuwarsu.

Sai bayan kwana goma Papa Abayomi da Shaheed suka iso gidan. Yanayin da ya ga Tauhidat ɗinsa ya faranta masa rai matuƙa. Girman Haj Manga ya ƙaru ninkin ba ninkin a zuciyarsa. Farinciki ne ya kusa yi masa yawa a lokacin da Haj Manga ta kawo kuɗin registration da accomodation (wurin kwana) na Shaheed ta ce ya je Lagos ya ji matsayin admission ɗin da aka bashi bara. Idan gurbinsa yana nan ana soma sabon zangon karatu nan da watanni kaɗan sai ya koma. Idan kuma da matsala ya dawo sai ta sake nema masa. Bayan doguwar addu'ar da suka yi mata da godiya Shaheed ya tafi Lagos. Mutumin da ta ce ya nema idan ya je shi ya taimaka masa aka sake masa alƙawarin samun gurbi a zango mai zuwa. Da murnarsa ya kira mahaifinsa wanda ya fara aikin da aka dauko shi dominsa ya sanar dashi.

Washegari ya dawo kuma a ranar ne Alh Audi ya aiwatar da nasa ƙudirin bisa shawarar Alh Ari. Kamar wasa da kansa ya cewa Shaheed ya kawo masa takardunsa ya gani. Da ya ɗauko ya kai sai Tony ya tarar ya karɓi takardun wai Alhaji ya hau sama. Bai kawo komai a ransa ba ya koma ɓangarensu. Bayan wata guda ya soma shirin tafiya Lagos. Lokacin Haj Manga ta saka Tauhidat a wata private school mai kyau da tsada sannan ga islamiyya tana zuwa idan ta taso. Kulawar da ta ke bata ita ta rage yawan kiran mahaifiyarta da ta ke yi.

Kwanaki kaɗan suka ragewa tafiyar Shaheed wata Talata sai ga kira daga Alh Audi. Shi da mahaifinsa ya nema a gaban Haj Manga tana zaune a falon. Mamaki ta yi tunda kuwa ta faɗa

masa waɗannan mutane a ƙarƙashinta suke bata so shi ko Fanna su shiga sabgarsu kamar yadda ita ma ta janye kanta daga garesu. Girkinsu Madam Zainaba ke yi yanzu.

Papa Abayomi a tsorace ya shigo suka gurfana a gabansu yana jira ya ji ance ya yi laifi sai Alh Audi ya miƙo masa wasu takardu fuska a sake.

"Abayomi kayi haƙuri nayi muku karambani irin namu na tsofaffi. Ga wannan admission na samarwa Shaheed a Turkey. Zasu fara karatu nan da sati uku saboda haka gobe Tony zai kai shi ayi masa passport a nemi visa."

"Me ka ce?"

Haj Manga ta mike tsaye rai a ɓace. Ran ta har wani makaki ya ke yi mata saboda tana da tabbacin da biyu Alh Audi ya ke son shige musu. Buɗe baki ta sake yi da niyyar soma faɗa sai idanunta suka sauka akan Abayomi da Shaheed. Kallonta suke yi a tsorace saboda basu saba ganin fushinta haka ba tun zuwansu. Abayomi ba zai so mata da miji suyi rigima a kan iyalinsa ba. Fasa maganar ta yi don dole ta zauna zuciya na tafasa.

Alh Audi ya yi dariya a ran sa sannan ya langaɓar da murya ya karyar da kan sa. Yanayinsa irin na mai son bada haƙuri ya ce,

"Ki yi min haƙuri na san tun farko munyi maganar zan ɗauki nauyin karatun yayan yan uwanki biyu ne a ƙasar waje. Kada ki ga na ƙara da Shaheed ki damu, ba zai hana ni cika miki alƙawari ba kinji Hafsatu."

Ashar ne ya subutu daga bakinta ba tare da ta yi niyya ba. Wai ita Alh Audi zai yiwa duniyanci. Wato ya fente ta baƙa a gaban direbanta da ɗansa ta yadda ko a gaba ya nemi haɗin kansu zasu bayar da gudu. Idan bata gyara lamarin da wuri ba tabbas zuwan Abayomi da iyalinsa zai koma kamar ta ɗauki wuƙa ne ta dabawa cikinta.

Ita da ta fi shi sai ta hau muryar kuka tana mammatse idanu "Alhaji ka bar batun waɗancan yara duka basu ci jarabawa ba. Ba komai ya sa ka ga na nuna ɓacin rai ba sai tunanin kada Papa Abayomi ya ga kamar muna son nuna masa iko da ɗansa. Kada ka manta bai daɗe da rasa matarsa ba. Yaran nan biyu su ne yake gani yaji daɗi. Amma me ka ce?"

Ta yi tambayar ga Abayomi. Idanunsa cike da ƙwallar godiya ga Allah da Ya haɗa shi da mutane masu kirki da son cigaban iyalinsa ya ce a raunane,

"Ba na son ɗora muku nauyi. Lagos ɗin ma ya isa Alhaji."

Ɓacin rai Alh Audi ya nuna "saboda ita ka ke yiwa aiki shi ya sa ni za ka watsa min ƙasa a ido? A wurina ɗa na kowa ne. Yadda zan kula da nawa haka zan yiwa duk waɗanda suke ƙarƙashina."

Da sauri ya girgiza kai yana bashi haƙuri.

Alh. Audi ya ce "In dai haka ne to ya fara shiri. Ga wannan Shaheed ka sayi kayan sawa. Idan bai isa ba ku yi mata magana zan ƙaro" ya miƙa masa kuɗi. Kin karɓa Shaheed ya yi sai ya ajiye a cinyar Haj Manga ya tashi ya basu wuri.

Alh Audi ya kasheta da mamaki. Yanzu kuskure guda za ta yi ya janyo rashin yarda tsakaninta da Abayomi. Ba don yadda take jin Tauhidat ba da babu abinda zai hanata sallamawa Alh Audi su, domin har kasan zuciyarta tana jin wani abu mara daɗi zai biyo bayan wannan alherin da ya yi musu. Kuɗin ta miƙa musu ta bi bayansa.

A falon ɗakinsa ta same shi yana kora giyarsa don yanzu ba ya kunyar uban kowa. Tsayuwa ta yi a gabansa ta soma faɗa akan wannan shigar sauri da ya ke shirin yi mata. Tana masifa yana lumshe idanu saboda daɗin da ya ke ji na abin shan sa. Tuna masa ta yi da haƙurin da ta yi lokacin da ya ci zarafinta ya kwace plazarta ta Lagos. Karashe zancen ta yi da cewa,

"Ka sauwaƙe min na kama gabana"

Gama sauraronta ya yi sannan ya tashi ya tsaya a gabanta ya turata ta zauna daɓas a kujerar bayanta. Yanayinsa abin tsoro don bata taɓa ganinsa a haka ba. Nuna ta ya yi da yatsa yana ƙankmƙance idanu.

"Manga a tafin hannuna fa ki ke. Na daɗe da sanin zaman me ki ke yi a gidana sai dai ina son sanar da ke cewa shigowa ce ganin damanki amma fita sai na so."

Tashi ta yi da ƙarfinta ta tunkuɗe shi baya ya yi taga-taga kamar zai faɗi. Ita ma nuna shi ta yi yana tsaye bayan ya dafa wata kujera ya tsaya,

"Baka isa ba tunda zaman aure babu dole a cikinsa."

Ran Alh Audi ya sake ɓaci dama yana jin haushin kawo Tauhidat da ta yi gidan. Fincikota ya yi ɗankwalinta ya faɗi ƙasa. Jelar siraran kitson kanta ya damƙo na tsakiyar da ƙarfinsa yana ja. Saboda azaba ta kusa sakin fitsari amma taki roƙonsa da ya sakar mata kai. Duƙar da kansa ya yi daidai kunnenta tana jin numfashinsa mai haɗe da warin giya ya ce,

"Namu auren zamansa wajibi ne a gareki indai da gaske kina son wannan shegen yaron naki Arƙam."

Da sauri ta ɗago kai ya yi murmushi ya cigaba da magana "ƙwarai kuwa Hafsatu. Ni kaɗai na san inda Arƙam yake. Ina so ki zubar da makaman yaƙinki ki bini a sannu domin na haɗaki dashi."

Sakar mata kai ya yi da ya ke mata azababben zugi ya ƙara da cewa "kada kiyi tunanin haɗani da hukuma domin bana jin akwai dan sandan da idonsa ya yi tsararon da zai ɗaura min ankwa a hannu. Ni ne Alh Audi Iro Karam! Shaheed zai tafi karatu kamar yadda na tsara sannan ubansa da ƙanwarsa su cigaba da zama da mu."

Haj Manga ji ta yi kan ta ya kulle ta kasa dogon nazari. Da ƙyar ta iya cewa "mece ce manufarka a kaina da su?"

Dariyar mugunta ya yi mata kafin ya riƙe habarta a tsakiyar hannunsa "da sannu idanunki zasu gane miki. Ke dai ki zame min mace ta gari a idon duniya ni kuma zan kawo miki Ibn Ibrahim Al- Karamawi, hahhh hahhh" ya kece da mahaukaciyar dariyar da bata san ya iya ba. Jiki a sanyaye ta fice zuwa ɗakinta ta faɗa gado tana wani irin kuka mai ban tausayi. Duk wani makaminta a lokacin ta ajiye shi saboda bata hango komai sai duhu a gaba da bayanta.

Washegari ko ruwa ta kasa kurɓa saboda tashin hankali ya tura Fanna ta kira masa ita saboda ta kashe wayoyinta. Shiryawa ya ce ta yi kafin shabiyun rana sun sauka a Kano gidan Dada. Kwantar da kai ya yi a gaban dattijuwar nan ya faɗa mata ƙarya da gaskiya akan dalilinsa na ƙin barin Arƙam ya zo hutu. Ba tun yau take jin tsoronsa ba shi ya sa bata ja zancen ba har ya yi ya gama. Bayan sun fita idanunta na zubar da hawaye ta ce,

"Allah Ya jikanka Arƙam."

Ta riga ta yardar ma zuciyarta cewa lallai asiri Alh Audi ya yi da shi saboda yadda dukiyarsa ta kara haɓɓaka. Tausayin surukarta ne ya dirar mata tana ganin ƙila ita ɗin ma bisa tursasawa suke zaman auren. Da wannan tunanin ta tara sauran yayanta na wurin mijinta na biyu su biyar ta ja musu kunne da babbar murya cewa kada wanda ya sake tayar da zancen Arƙam.

"Rana dubu ta ɓarawo ce, rana ɗaya ta mai kaya. Idan dubun duk mai hannu akan salwantar jikana ta cika ina mai tabbatar muku da cewa duniya za ta yi atishawar yan tsaki. Za'ayi walkiya mu gansu. Ban lamunce ku yanke zumunci da Jamalu ba ko bayan raina. Wannan yaron (baban su Jamal) yayanku ne kuma dukkaninku daga arziƙinsa ku ke ci saboda haka zare hannu daga kan abinda yayi saura daga zuri'arsa ba naku bane. Allah Ya yi muku albarka." Wannan su ne kalaman Dada na ƙarshe ga Nana, Safiyanu, Garba, Rabi’a da Usman akan lamarin Arƙam.

***

Tun daga waje ake jiyo hayaniyar matasa tana tasowa daga wani wuri da aka rubuta cafeteria da manyan harufa. Wannan wurin cin abincin da ya ke cikin Medical College reshen Johns Hopkins University matattarar malamai ce da ɗaliban makarantar. The Johns Hopkins Medical College tana cikin manya manyan makarantun karatun aikin kiwon lafiya mafiya girman daraja a duniya ba ma ƙasar Amurka kadai ba. Yankin Baltimore na garin Maryland suna ji da wannan makaranta shi ya sa ake ganin girman ɗalibanta.

Yau ta kama Valentine's day saboda haka cafeteria ɗin ta sha ado da jajayen fitilu, balan balan da banner waɗanda aka yi rubutun kalaman soyayya. Samari da yan matansu ne suke ta kai kawo, wasu na raye-raye wasu kuma suna cin abinci ko shaye-shayensu ana raha. Cikin wannan hayaniyar wani matashi ne zaune akan kujera mai tsayi da ta daidaita kirjinsa da dogon teburin gabansa. Hannuwansa ya saka ya dafe kunnuwansa sakamakon ihun kiran sunansa da wasu gungun ɗalibai suke yi suna bubbuga tebura da kofuna.

"A.I.K! A.I.K!! A.I.K!!!"

Suke ta maimaitawa ana ingiza shi da ya tashi ya hau stage ɗin da aka tanada musamman dominsa a wannan rana.

"I've got a cold (mura nake yi)" ya faɗa cikin wata siririyar murya, mai nuni da an kusa galaba a kansa.

"NOOOOO" ita ce kalamar da suka haɗa baki wajen furtawa da karfi, amon muryoyinsu ya sake karaɗe wurin. Ya yi ɗan murmushi "not in the mood today (bani da ra'ayin yau)."

Maimakon su rabu dashi sai suka ƙara ƙarfin bugun teburan da kiran sunansa. Wani babban mutum ne ya taso ya zo gabansa, ya ja hannunsa sai da ya tayar dashi tsaye ya yi masa magana da turanci.

"Kayi na minti goma kacal. Ranar ba za ta cika ba idan ba ka ƙawata mana ita ba"

Matashin turo baki ya yi sannan ya miƙe tsayinsa sosai. Dogo ne sosai mara ƙiba sai dai alamu sun nuna yana motsa jiki. Fatarsa baƙa ce irin ta mutanen da duniya ta yi musu daɗi. Ta murje ta yi kyau. Kyakkyawar fuskarsa tana ɗauke da madaidaitan idanu, hanci mai dan faɗi da tsini ta gaba sai bakinsa da siririn gashin baki ya ƙawata. Arƙam Ibrahim Karam kyakkyawan saurayine ta kowace siga. Kallo ɗaya za ka yi masa indai ka san Haj Manga ka gane cewa tsatsonta ne. Yadda ya ɗebo mahaifiyarsa a komai haka ƙaninsa Jamal ya ɗebo mahaifinsu. Wannan dalilin ya sa a lokacin ƙuruciyarsu akan tsokane su da Telu fari da Telu baƙi.

Sanye yake da dogon wandon chinos ruwan ƙasa mai duhu ya yi zanzaro da farar vest ɗinsa. A sama kuwa t-shirt ce baƙa wadda ya buɗe maɓallanta daga sama har ƙasa. Kansa ya sha rangaɗeɗɗean kitso guda takwas wanda tsagar ta fito raɗau, ga jelunan sun dan zarta kafaɗunsa. Yana tafiya kan stage ɗin ana ihu ya ƙarasa ya tsaya a gaban loudspeaker da take kafe a wurin. A gefen hagunsa wani bature ne mai suna Josh zaune a gaban piano. Daga ɓangaren dama kuma mutumin ƙasar Philippines ne Tomaz zaune da guiter a hannu. Sipikar ya zaro daga marikinta ya soma rera waƙar soyayya cikin harshen turanci cikin wata daddadar murya mai ratsa zukatan masu sauraro.

Irin ihun da aka saka a wurin sai ka rantse rabon arziƙi ake yi. Masoya su ka shiga filin rawa wasu hadda hawaye saboda irin kalaman da ya ke amfani dasu masu tsuma zukata. A can

ƙarshen wurin mutumin nan ne da ya tayar dashi zaune da wasu mutane su biyu suna magana. Arƙam da abokansa ya nuno musu ya ce,

"Me kuke tunani akansu?"

Ɗaya daga cikin mutanen ya kaɗa kai, "ka ce medical students ne, ta yaya ka ke ganin zamuyi signing ɗinsu a agency ɗinmu?"

"Yaran nan da kuke gani suna da basira sosai. Shekararsu biyu da fara waƙa a nan kuma ban taɓa jin Karam ya yi waƙar wani ba. Shi ne shugabansu kuma shi ya ke rubuta waƙoƙinsa." Ya gyara zama sosai "ɗan baiwa ne don yanzun nan sai ya haɗa waka ka ji wurin nan ya ruɗe da ihu saboda daɗinta. Idan duka ku biyun babu mai son ɗaukarsu zan nemi wasu."

Mutumin da yaki magana tun zamansu ne ya ɗauke ido daga ƃangaren da ake waƙar, ya dubi shugaban cafeteria ɗin da ya kira su.

"Sun san kana nema musu agency?"

"Ko ɗaya, ina dai son taimaka musu ne saboda na san waƙa tana kawo arziƙi fiye da tunani. Ka duba da kyau mutumin Africa ne ɗan Nigeria kuma musulmi da wannan basirar."

Duka mutane biyun kowannensu kalmar musulunci sai ta zaburar da zuƙatansu. Na farkon da ya fara nuna rashin ra'ayi bai yi wata wata ba ya yanko wasu makudan kuɗi a matsayin abinda kamfaninsa zasu biya mawaƙan a shekara. Manufarsa a zuci bata wuce ra'ayinsu na ɗauke hankulan musulmi daga addini ba. A ganinsa addinin musulunci naƙasu ne ga rayuwar mabiyansa musamman matasa maza da mata. Da irin haka suke yiwa mutane shigo-shigo ba zurfi. Son kuɗi da burin yin suna a duniya yana taka rawa sosai wurin lalata tarbiyar mutane musamman musulmi. Kan kace meye wannan zuciya ta karkata sai haram ta koma halal. Kuɗin kawai ake hange ban da lahirar.

Bayan ya faɗi kudin Raymond mai kula da cafeteria ya yi murmushi da zummar amincewa, sai ɗayan ya ruƃanya kuɗin da wancan ya faɗa sau biyu. Jin haka shi kuma ya mayar sau uku. Wancan ya mayar huɗu...A haka sai da suka yi ta jayayya inda kuɗin ya koma daidai da ruƃi takwas kuma na farkon ne ya yi nasara.

Bayan sun gama waƙar Raymond ya kirasu teburin da suke zaune. Ɗaya mutumin ya tashi cikin ɓacin rai ya tafi. Zama suka yi a gajiye ya gabatar musu da shi.

"Ga Mr Darcy shugaban Ace Entertainment yana son ɗaukarku contract ɗin waƙa a ƙarƙashin kamfaninsa."

Arƙam ne ya fara tashi fuska a tsuke "Raymond tun yaushe na faɗa maka cewa waƙar da nake yi ba sana'a nake son mayar da ita ba?"

Lallashin sa Raymond ya soma yi "ka zauna ka ji nawa zai baku a shekara."

"Bana so kuma kada ka sake yi min irin haka."

A fusace ya tashi ya bar wurin. Waje ya fita yana shaƙar iskar wurin hannuwansa a aljihu. Bai daɗe da tsayuwa ba Raymond ya fito. Cikin laluma ya dinga nuna masa irin alkhairin da zai samu a dalilin waƙa. Misali ya bashi da Westlife da Backstreet boys saboda yanayin waƙarsu ta Pop music ɗaya ne. Sunyi kuɗi sunansu ya zaga duniya. Sannan ga Tomaz aiki wurin kala huɗu yake yi saboda kufin makaranta. Josh kuma daga gidan marayu wasu suka yi adopting ɗinsa. Yanzu sun mutu basu bar masa komai ba sai tulin bashi.

"Kai maikuɗi ne amma indai abotarka dasu da zuciya ɗaya ne ba za ka so zama sanadin shiga tsakaninsu da arziƙi ba." Ya dafa masa kafaɗa da hannuwansa biyu "kaine mawaƙin, su kiɗa kawai suka iya. Idan baka shiga ba su ma sai dai su ga samu su ga rashi." Daga haka ya koma ciki ya bar shi da tunani.

Washegari da safe a ɗakin karatu ya haɗu da Josh da Tomaz fuskokinsu babu yabo ba fallasa. Tabbas abokan nasa suna buƙatar taimako. Takaici da ƙuncin zuciya ke nuƙurƙusarsa. Shekara shida da watanni kenan da mahaifiyarsa da wan babansa suka raba shi da mahaifarsa. Bakin gwargwado yana ta ƙoƙarin tsayawa a turbar addini amma abin da wahala. Babu mafaɗi sannan Nanna da ta rage masa ta yi rantsuwar muddin ya sake sauke ƙafafunsa a Nigeria batare da kwallin shaidar ya zama cikakken likita ba sai ta yi masa baki. Ya rasa me yake faruwa, kuɗi dai bai taɓa rasawa ba tun bayan Tony PA ya ɗauko shi daga makarantar da Kawunsa Audi ya kaishi ya dawo dashi America kuma shi ne ya yi masa waɗannan bayanai game da mahaifiyarsa. Tun yana buga numbar gidansu bata

shiga har ya haƙura. Daga baya Tony ya bashi ta Nanna amma har yau idan ya kira wata Madam Zainaba ke ɗauka ta ce masa Nannansa bata son magana dashi saboda laifin da ya yi mata. Ranar farko cikin tashin hankali ya tambayeta laifin ta faɗa masa wai makarantar da aka kaishi nan mamansa taso ya yi amma shi ne ya koma inda Alh Audi ya zaɓar masa. Ya so yi mata bayani cewa Tony ne ya canja masa kuma ya ce inda ya kaishi nan Nanna ta zaba saboda duka takardun ya ga sa hannunta da idanunsa. Wasu maganganun sam baya gane ma'anarsu ma. Abu ɗaya ya fahimta shi ne, Nanna tana fushi kuma ba za ta yafe ba sai ya gama karatu.

Tun yana son sanin me yake faruwa har shima tasa zuciyar ta kangare ya dena damuwa. Wurin Raymond ya tafi batare da sanin abokansa ba aka kaishi ofishin Mr Darcy. Takardar contract ɗin ya sakawa hannu an ɗaukesu shekara biyu. Banda zunzurutun maƙudan kuɗaɗe ga gida da mota da aka haɗasu dashi. Sai da aka kammala komai sannan Raymond ya yi kiransu Tomaz zuwa ofishin. Sunyi mamaki da matuƙar farinciki ganin cewa Arƙam ya damu da rayuwarsu. A matsayinsa na shugabansu dai kuɗinsa yafi nasu amma hakan bai dame su ba. Dukkaninsu sunyi bankwana da fatara da shiga aljihunsa, kodayake yanzun ma alfarmarsa suke ci. Bayanin ƙarshe a contract ɗin shi ne basu yarda a saka su waƙa a lokutan karatunsu ba. Suna buƙatar a dinga basu isasshen lokaci saboda su ukun duka cikar mafarkinsu shi ne zama cikakkun likitoci.

Da wannan ne *3ripleA* suka samu kafuwa. Sunan nasu inkiya ce ta nahiyar da suka fito. Africa ta Arƙam, Asia ta Tomaz sai America ta Josh. Sati guda da gama jarabawarsu ta ƙarshe wadda a ƙa'ida bayan fitar sakamako zasu fara internship ne suka yi reporting a Ace Entertainment. Waƙoƙi takwas Mr Darcy ya buƙaci suyi domin fitar da album ɗin farko. Watanni uku garesu kafin fara zuwansu asibiti saboda haka nauyin kacokan yana wuyan Arƙam. Ba dare ba rana ya duƙufa wurin rubutun waƙoƙin, rerawa da kuma gyare-gyaren da Mr Darcy ya ke ganowa. Rashin bacci, ƙara taɓarɓarewa da raunin ibada da rashin walwala saboda ƙarancin hutu ne suka sarkafi wuyansa. A ƙoƙarinsa na ganin ya kammala rubuta wakokin a wata uku sai ya zamana ɗaukar video ne ya rage ko sun fara zuwa asibiti ya jefa shi cikin takura. Cikin sati goma ya gama

haɗa komai. Wannan ƙwazon nasa ya sake tafiya da imanin Mr Darcy.

Sun fara zuwa asibiti aka nemi sulhu da ƙyar da siɗin goshi da hukumar asibitin wurin samar musu lokutan zuwa shooting. A tsukin wata biyu sun soma fita hayyacinsu sai da afa ƙwayoyi suke iya wasu ayyukan. Idan za'a fara recording sai an tabbatar sunyi akalla baccin awa takwas sannan a basu maganin wartsakarwa. Daga nan sai masu kwalliya su gyara musu tun daga kai har kafa sannan designers su kawo kayan da suka dace. Hauka ne kawai basu yi ba saboda mugun stress a dalilin haɗa gudu da susar duwawu.

Arƙam ya fi kowa jigata shi ya sa ma ya fisu shan ƙwayoyin. Ranar da aka gama ɗaukar tamkar sallah take garesu. Sai dai suna komawa asibiti aka sanar dasu sai sun sako wata biyun nan saboda basu taɓuka abin kirki ba. Ba haka aka so ba amma sun san anyi musu adalci sosai. Koyon aiki suke yi ka'in da na'in. Wata guda bayan an gama shirin komai aka saki album ɗin 3tripleA na farko. Cikin sati guda Mr Darcy ya mayar da kuɗaɗɗen da ya kashe harda mahaukaciyar riba. Ba jimawa album ya zaga ƙasar Amurka da kewaye babu zance sai na sababbin mawaƙan nan. Sunyi suna saboda daɗin murya da waƙoƙin Arƙam. Kyawun samarin ya ƙara rura wutar samun alkhairinsu. Kuɗi kam tashin farko suka yi na ban mamaki. Tun ba a gane ba kuwa har aka waye dasu a asibitin da suke. Mutane suka dinga tururuwar zuwa ganinsu. Idan aka hanasu shiga sai suyi ƙaryar cuta. Hanyar kuɗin shiga ta ƙaru ga asibitin duka darajar waƙoƙin ɗan Haj Manga.

Ga kudi ga suna amma duk waɗannan basu hana rayuwar Arƙam shiga wani irin yanayi na dimbin damuwa da kaɗaici ba. A zahiri kullum ya fito sai sakin fuska da yawan murmushi saboda faranta rayukan masoya. Babu wanda ya san irin ƙuncin da yake tattare dashi na rashin ɗumin mahaifiya da yan uwa. Privacy tuni ya yi ƙaura. Yanzu bai isa ya shiga wuri mai mutane ba indai ba cikin asibiti ba sai da masu tsaronsu. Idan ba haka ba kuwa mutane ke kewayesu ayi ta ɗaukar hoto ana rungumarsu. Yan mata da dama suna cikin gararin soyayyar waɗannan zaratan matasan.

Bayan an gama cin kasuwar album ɗin farko da wata biyar Mr Darcy ya buƙaci su fara shirin na biyu da za a saki a shekara mai zuwa. Arƙam da ya tabbatar da cewa kansa zai iya bugawa

bai yi wata wata ba ya nemi a soke contract ɗin tunda basu karɓi wasu kuɗi na shekarar ba. Mr Darcy ya yi tsallen daka yaƙi amincewa saboda shi ya san me ya samu a dalilinsu. Abu dai ya kusa zama rikici ana batun zuwa kotu tunda sun sa hannu. Sai da aka kai ruwa rana Arƙam ya yarda da album na biyu amma ya jaddadawa su Josh daga wannan ba zai ƙara ba. Rayuwarsa gabaɗaya a ƙuntace yake jinta. Babu wata walwala ko manufa. Irin rayuwar da ke samun akasarin mutanen da suke harkar entertainment industry dai. Waɗanda suke bibiyarka da dama saboda suna ƙaruwa da kai ne, karancin kusanci da mutane saboda tsaro, shaye-shaye saboda yawan damuwa da stress da sauransu. Mafiya yawansu a haka rayuwarsu ke lalacewa suyi ta yawo tsakanin asibiti da rehabilitation centres. Idan damuwa ta yi yawa tare da ƙarancin imani sai ka ga mutum yana harin rayuwarsa da kansa. Wa iyazu billah!

Kwanaki na ƙara tafiya al'amura suna ƙara rikicewa Arƙam. Sun cika alƙawarin contract da blockbuster album wanda ya sama musu kuɗi fiye da zato da tsammaninsu. Mr Darcy ya so matuƙa ko shekara su ƙara yarda ayi amma fafur Arƙam yaƙi. Hargitsin rayuwarsa shi ne babbar damuwarsa. Shekara da shekaru uwa taki nemansa. A ɓangare guda kuma masoyansa sun hana shi mayar da hankali akan karatunsa sosai. Daga ƙarshe asibiti daban ya nema inda zai yi residency ɗinsa duk don ya sami nutsuwar zuciya. Sai da ya rage tsayin gashinsa ya dena kitso sai barin afro da ya ke shan gyara. Ya kuma ƙara da tara kasumba kuma ya yi sa a ba kasafai ake gane shi ba.

Wata rana ya dawo daga asibiti a gajiye zuciyarsa ta kwaɗaitu matuƙa da son gida. Numbar Tony ya nemo a tsohuwar wayarsa ya kira. Bugu biyu Tony ya ɗauka a gigice don rabonsa da Arƙam yafi shekara uku. Karya ya ke yiwa wanda ya sa shi ɗauke shi a kodayaushe ya ce a bashi kuɗi yana damunsa da son zuwa gida. Kuɗin makarantarsa tuni aka gama biya duk don kada ya sami damar cewa zai zo gida. Muryarsa ya canja kamar mai shirin kuka,

"Arƙam kaine?"

Mutumin da bai iya faɗa ko ɗaga murya ba yau ɓacin rai ya sanya shi yiwa Tony tsawa. A wannan lokacin babu abinda Tony ya hasko sai fuskar Haj Manga, ya haɗiyi yawu da ƙyar.

Arƙam ya cusa yatsunsa cikin tulin gashinsa wanda na gaban yafi tsayi da cika,

"ka haɗani da Nanna yanzu."

Cikin rawar murya Tony ya amsa da cewa,

"Arƙam ka kara haƙuri ka gama karatun kafin ka nemeta."

Yadda zuciyarsa ta raunana bai san lokacin da ya sake ƙanƙame kan wayar yana zubar da zafafan hawaye "Tony! I am not happy. I need my mother, am so lonely."

A karon farko da tausayin Arƙam ya ɗarsu a zuciyarsa kenan. Yana da kyakkyawar masaniya akan manufar mutane biyu akansa. Alh Audi da wanda ya ke yiwa aiki a bayan fage, idan ya barshi ya koma gida yanzu yana da yaƙinin zai iya rasa rayuwarsa. Bayan gajeren tunani kawai sai ya katse kiran. Matarsa da take amsa waya a matsayin Madam Zainaba ya kira daga ɗaki. Umarni ya bata cewa idan Arƙam ya kirata ta katse wayar kada ta yarda ta yi masa magana. Abin ya bata mamaki tunda ta san komai akan abinda maigidan nata yake yi. Ba jimawa kuwa ya kira ta ɗauka taƙi amsa tarin tambayoyinsa sai ma kashe wayar da ta yi.

"Tony meye manufar yi masa haka?"

Da dukkan gaskiyarsa ya ce "ina ganin lokaci ya yi da zai dawo wurin mahaifiyarsa. Na gaji da yaudararsa da ƙarya. Zuciyata tana bani shirunmu zai tunzura shi ya kamo hanyar gida. Ki zama cikin shiri garin zamu bari."

Shi kuwa Arƙam shirun nasu ba komai ya ƙara masa ba sai hasala da mugun bacin rai. Wayarsa mai tsada ya rotsa da ƙasa saboda takaici. A take ya ƙudurtawa zuciyarsa ba zai kuma neman Nanna ba sai ta neme shi da kanta. Ya sha yin kuka, ya yi roƙo da magiya ga Tony da wadda ta kira kanta da Madam Zainaba duk a banza. Tabbas kafin tahowarsa Madam Zainaba ta koma gidansu. Ko fuskarta ba zai iya tunawa ba bare murya, amma ya tabbatar da kusancinta da Nanna shi ya sa bai taɓa ƙaryata ta ba.

***

Kwanci tashi Tauhidat ta shiga js3 yayin da Jamal ya fara Abti America, jami'a me zaman kanta a garin Adamawa. Soyayya da gatan da Haj Manga ke nuna musu babu kama hannun yaro.

Zuwa yanzu Tauhidat ta san matsayinsu a gidan saboda haka take ƙoƙarin kamewa daga wasu abubuwan kada a dinga ganin zaƙewarta. Hakan yana ɓata ran Haj Manga amma mahaifinta yana yawan ja mata kunne da cewa ita ɗin ba kowa bace face yar Abayomi direba. Yawan nasihunsa a gareta ya sa ta iya riƙe matsayinta duk da tana da ƙarancin shekaru.

Girma ya fara zuwa ta zama yar budurwa mai shiga rai da wuri saboda halinta na surutu da yawan tambaya. Iyakar surutun nata dama daga babanta sai Nanna da Madam. Idan taje hutu wurin danginsu sai ka gani a yanayin Haj Manga. Gidan gabaɗaya dena yi mata daɗi ya ke yi sai yarta ta dawo. Jamal tun yana cewa ta yi masa ƙwace har ya dawo ya zama basu da sirri ga juna. Babbar matsalarsa ita ce zamansa riƙaƙƙen ɗan ƙwaya da shaye-shayen kayan maye. Kunnuwar wannan masifa cikin rayuwarsu ba ƙaramin tashin hankali yazo wa Haj Manga ba. Alh Audi ne da wannan aikin kamar yadda ta gano daga baya. Shi ya umarci Tony ya ƙulla abota da Jamal ya dinga jansa a jiki. A haka rayuwarsa ta ɗauki turba daban har ya sauya suna zuwa Tarantula a wurin abokan shashancinsa. Haj Manga ta yi kukan ta yi faɗan sai daga baya ta fuskanci Alh Audi da gangan ya yi mata haka. Bai ji kunya ba ranar da ta tunkare shi ya ce yana son nuna mata cewa yayanta basu isa komai akansa ba. Duk wani shiri da ta fara akan gina Jamal dole ya rushe.

Mutane suna ganin baƙinta akan rashin nuna ƙyama akan halin ɗan nata sai ma ƙara jansa a jiki da take yi. Ita kuwa ta fi kowa sanin idan ta bar Jamal gabaɗaya tamkar ta amince Alh Audi ya yi galaba akansu ne. Tauhidat tana daga cikin mutanen da suka san ɓoyayyun halayensa don ta sha kama shi a wurin dabbobi yana yi. Kullum roƙon rufin asiri yake yi a gareta yana nuna mata zai dena. Damuwarsa bata wuce yawan kukan mahaifiyarsa akan yayansa ba da sababbin halayensa, sai dai kuma duk yadda ya so denawa abu yaci tura. Gashi har yanzu bai san takunkumin da Alh Audi ya sanya mata ba. Hasali ma jansu yake yi a jiki sosai da shi da Tauhidat ɗin. Shamsu a lokacin yana bautar ƙasa bai fi a kirga ba ta taɓa ganinsa tun zuwanta gidan.

Yau ta kama Asabar Jamal ya zo hutun ƙarshen mako gida. Yana zaune a ɗakinsa ya ji bugu haɗe da sallamar Tauhidat. Da sauri ya kashe tabar wiwi ɗin hannunsa ya tura kwalaben benelyn ƙarƙashin kujera ya tashi yana layi. Airfreshner ya

dinga fesawa sai da ɗakin ya yi ƙaramin hazo sannan ya buɗe. Sanye take da kayan islamiyya riga ta dan wuce gwuiwa da wando sai hijab. Rinannun idanunsa ya sauke mata ta ja da baya. Dama ba shiga zata yi ba don Papa da Madam Zainaba suna mata gargaɗi sosai akan haka. Tsabar wayonta yasa ta gane ya sha wani abu ta taɓe baki "Tarantula ne ko Jamal?"

"Ke. Fa. Akwai sa ido" ya ce murya na rarrabewa

Murmushi ta yi masa wanda ya hasko siririyar wushiryarta ya kara mata kyau "na dai gane Tarantula ne. Nanna ke kiranka dama."

Gabansa ya ɗan faɗi don ko yaya ya sha wani abu tana saurin ganewa. Cewa ya yi ta faɗa mata yana wanka zai shigo idan ya fito. Dariya ya bata ganin bai yi tunanin Nanna za ta iya gano ƙaryarsa ba, ta ce,

"To waye ya faɗawa Tauhidat ɗin yana wanka?"

"Eh to kuma da yar gaskiyarki. To jirani minti goma, a'a biyar ma ya isa." Ya koma cikin ɗakin da sauri duk da yadda take faɗa masa islamiyya za ta tafi. Tsayuwa ta yi a bakin ƙofar saboda muddin ta koma sai Nanna ta tambayeta ina yake. Idan ta yi mata ƙarya kuma za ta yi saurin gano cewa ya yi halin ne ta shiga damuwa. Karar buɗewar ƙofar ɗakin Shamsu ta ji ta kawar da kan ta gefe. Tun zuwanta gidan bata taɓa ganin ya sakar mata fuska ba. Wani wari da bashi da ƙari ne suka haɗu suna silalowa daga ɗakin nasa zuwa hancinta. Cikinta ne ya soma yamutsawa amma maimakon ta ja baya sai ta tunkari ƙofar hannunta akan hanci.

Ko wani abu ne ya mutu a ɗakin ta tambayi zuciyarta. Niyyarta ta rufe ƙofar ta sanar da mai yi musu shara ya duba sai ganin mutum ta yi tsaye ƙiƙam a bakin ƙofar. Da saurinta ta ja baya a daidai lokacin da ya watsa mata wani mugun kallo ya rofo ƙofar garam akan fuskarta.

Jiki na rawa ta juya za ta bar wurin kiran da Jamal ya yi mata ya ƙarasa gigita ta. Ganin yadda tsoro ya bayyana a fuskarta ya sanyaya masa jiki. Kofar ɗakin ya kalla ya bita da kallon tuhuma. Tambayoyi ya dinga jero mata yana bin ƙofar ɗakin da harara tamkar ita ce Shamsun.

"Kin haɗu da Shamsu ne? Ya yi miki wani abu?"

Gaba ta yi da sassarfa kafin ta iya bashi amsa "mu tafi Jamal na san Nanna ta gaji da jiranka kuma nima na makara islamiyya."

Zargi ne ya ɗarsu a ransa game da Shamsu saboda ganinta da ya yi a bakin ƙofar dakin. Nan da nan kuwa zuciyar yan kwaya ta tunzura shi ya kama ƙofar ya murɗa a fusace. Ko gezau bata yi ba alamun an rufe da mukulli. Bai tsaya tunani ba ya shiga bugun ƙofar da ƙarfinsa.

"Kai dalla Malam ka buɗe ƙofar nan idan ka cika namiji."

Mugun tsoro ne ya sake kama Tauhidat ta dawo tana roƙonsa ya bari saboda babu abinda ya yi mata. Kallon da ya yi mata da jajayen idanunsa da mayen wiwi ya fara saki ya sata yin baya. Bata bar magiyar ba shi ma ya cigaba ƙofar. Daga shi sai tawul a kugu ga danshi a jikinsa da gani daga wanka ya fito. Abinka da dama ta ciki na ciki ga kan ba daidai ba yan abubuwan da ya sha sun fara yi masa karo kawai sai Jamal ya kai masa naushi a baki.

Tauhidat cikin gida ta ruga a guje lokacin da Shamsu ya shararawa Jamal mari rai a ɓace. Sa'ar ganin Haj. Manga ta yi a ƙasa za ta fita ta riƙo hannunta da sauri tana faɗa mata me yake faruwa. Ita ma nata hankalin tashi ya yi suka dunguma harda Fanna da suke kallo ita da Kulsum da yarta ta biyu Aimana.

Turus kowa ya yi musamman Haj. Manga da suka fito. Shamsu ne da hannu ɗaya ya shaƙe Jamal ya manna bayansa da bango. Yanayin jikinsu dama ba ɗaya ba. Shamsu ya ɗara shi tsayi sannan kana ganinsa ka ga ƙaƙƙarfan namiji. Jamal kuwa ɗan hutu ne daga sama har ƙasa. Wai amma duk wahalar nan da yake sha yana kakari bata hana shi magana ba.

"Ko kallon banza ka sake yiwa ƙanwata sai naci b...."

Haj. Manga ta daka masa tsawa "ya isa haka". Ta kalli Shamsu da ko kunyarta bata sa ya sake shi ba ta ce masa "sakar min ɗa kai kuma."

"Idan na ƙi fa?" Ya ce a wulaƙance yana taɓe baki.

Furucinsa ya ɗaurewa Tauhidat kai. Fanna ma duk tsagerancinta sai a bayan ido take iya yiwa Haj. Manga maganar banza, shiyasa yau daɗi ya kama ta. Faɗan da babu ruwanka dadin kallo ne da shi.

Cikin takunta na matar da bata ɗauka bare jurar raini ta isa gabansu ta ɗauke Shamsu da marin da ya yi sanadiyar sanya shi sakin Jamal. Wurin tamkar ɗaukewar wutar nepa don kowa shiru ya yi. Ransa ya yi matukar ɓaci ya dago ido ya na kallonta,

"Ki ka mareni?"

Ta cikin zagayayyen farin gilashin idanunta ta zuba masa nata idanun sannan ta nuna shi da yatsa, "ko za ka rama ne?"

Rai na ƙuna ya shige ɗakinsa ya bugo ƙofar da ƙarfin tsiya. Juyawa ta yi ta kalli Jamal takaicinsa yana mamayarta. Cikin faɗa ta ce, "me ya haɗaka dashi? Ban gargaɗeka akan iyalin Audi Karam ba?"

Mamakin maganarta ya saka kowa mutuwar tsaye banda Jamal da ya daka tsalle yana ɗaga hannuwa irin na jinjina, "wooo Nanna, wooo Nanna kina fire my sweet..."

"Shut up!" Ta daka masa tsawar da ta sa ya kama baki ya bame kamar ba shi ba sannan ta sake tambayar me ya haɗa su. Zumburo baki ya yi ta ɗago hannu za ta make shi ya yi saurin mayar da shi sannan ya nuna Tauhidat, "fitowa nayi naga ƙanwata a tsaye a ƙofar ɗakinsa jiki na shaking."

Haj. Manga ta gyaɗa kai tana jiran ya ɗora bayanin ta ji ya yi shiru. "Daga nan sai aka yi me? Ta ce ya yi mata wani abu ne?"

Sosa keya ya kama yi yana ɗan murmushi "Eh to gaskiya bata ce ba, amma yanayinta yasa naji gara na tauna aya ko don tsakuwa taji tsoro."

Fanna kasa daurewa ta yi saboda yanayin maganarsa ta kwashe da dariya. Ita fa saboda shirmensa shi ya sa take ɗan dasawa dashi.

"Jamal ba tauna tsakuwa kayi don aya taji tsoro ba?"

Yana tsaye gaban mahaifiyarsa ya ɗago mata hannu da yar dariya "sammakal Anti Fanna tunda kin gane."

Ita ma Haj. Manga dariyar ya so bata ta riƙeta tare da kama kunnensa "gashi nan an tauna ka ai kafin ka tauna ayar. Tauhida ya taɓa ki ne?"

Girgiza kai tayi idanunta akan Jamal da ta ke jin takaicin ya janyowa kansa duka a dalilinta.

"A'a Nanna kawai fa war..."

Kafin ta ƙarasa Haj. Manga ta ja hannunta suka koma ciki saboda hasashen me za ta ce. Fanna ta so samun kanun labarai ta samu ta haɗa gulmar da za ta kaiwa mahaifinta. Haj. Manga ta ja ta har ɗakin farko idan an shiga falonta kafin babban wanda ta barwa Tauhidat. Nan suka shiga tana riƙe da hannunta har lokacin. Ita duk tsoro ya kama ta. Jamal na isowa Haj Manga ta tura ƙofar. Ransa kuwa ya ɓaci ya soma ƙunƙuni.

"Not fair Nanna, ni ne fa na fara shigar mata. Ya ci ace dani aka ƙarasa komai. Sai da aka zo wurin dadin za ki koreni"

Kama ƙofar ya yi zai buɗe yaji ta ce,

"Jamal" da muryar gargaɗi. Ba don ya so ba ya haƙura amma sai da ya manna kunnensa a jikin ƙofar. Ganin yadda Tauhidat ta tsure yasa Haj. Manga sakin fuska tana murmushi, "ni kam abar a tausayawa ce! Daga ke har Jamal din babu wani jajirtacce. Yara sai kace yayan tsintuwa ba raino na ba."

Dariya ce ta so suɓucewa Tauhidat ta sa hannu ta danne bakin. Daga waje kuwa muryar Jamal suka ji yana ce wa "Nanna ya haka ne, sai ki sa ta raina ni. Namiji kamata kina zubar masa da aji a gaban ƙanwarsa."

Dama ta yi zargin ba zai tafi ba. Taɓe baki ta yi "Namamajo dai."

Tana jiyo takunsa ya bar wurin yana mita suka yi murmushi ita da yarta. Tambayarta ta yi ko wari taji a ɗakin Shamsun ta amsa da eh duk da kasancewarta a waje. Gargaɗi Haj. Manga ta yi mata sosai akan ko hanya kada ta yarda ta dinga haɗata da shi. Babu doguwar tambaya ta yi alƙawarin bin umarninta. Duk da muguwar makarar da ta yi kuwa a haka ta wuce islamiyya.

Shi kuwa Shamsu tunda ya koma ɗakin zuciyarsa take tafasa da ɓacin rai. Yadda ba ya son mutane ko shiga shirginsu haka ya ke so shi ma kada a shiga nasa. Duk faɗin gidan kuwa ba shi da abokiyar hamayya kamar Haj. Manga. Wayar mahaifinsa ya kira yana kumbure-kumbure ya faɗa masa cewa matarsa ta mare shi sannan wannan yar aikin ta ta wato Tauhidat ta ji warin ɗakinsa. Da farko Alh Audi sai da yaji tsoro ya sarƙafi zuciyarsa saboda sanin wace ce Tauhidat a gareshi. Haƙuri ya baiwa Shamsun akan zai yi mata magana idan ya dawo sannan

ya ajiye wayar. Hularsa ya cire ya soma shafa sankon kansa yana faman tunani. Sai ga shi yana murmushi bayan mintuna kalilan daga baya ma ya kwashe da wata muguwar dariya. Jinjinawa ƙwaƙwalwarsa mai zurfin tunani da hango mafita a lokacin da ya dace ya yi. Daki-daki zai bi komai har ya samu biyan buƙata.

Koda ya dawo da daddare bayan ya ci abinci ya tara iyalin nasa gabaɗaya banda Haj. Manga. Lokacin da saƙo ya risketa na kiransa waya take yi. Hannu ta ɗagawa Madam Zainaba alamun kada ta dameta da kiran nasa. Sai da suka yi jiran kusan rabin awa sannan ta iso tana zuba wani irin ƙamshi mai ratsa zuciya. Jamal kallonta ya yi tare da yin alamar ta yi kyau da hannun damansa. Kan sa ta shafa cike da kulawa ta sake ƙular da Alh Audi da Shamsu. Zama ta yi ta ɗora ƙafa ɗaya kan ɗaya sannan ya soma magana yana ta ƙoƙarin danne ɓacin ransa.

"Hafsatu me ya kai ki shiga rigimar yara harda marin Shamsu? Gidan nan kaf kun san cewa shi ba mai son hayaniya bane shi ya sa yake ƙoƙarin nesanta kansa daga kowa."

Ɗago kai ta yi cike da isa ta ce "ka tara mu ne ka ji abinda ya faru ko ka tarewa ɗanka? Idan na farkon ne na riga na yiwa Tauhidat faɗan kada ta sake bari wani abu ya haɗata dashi. Sannan kuma na mare shi saboda rashin kunyar da ya yi min. Idan kuma na biyun ne to sai in ce asuba ta gari don ina da abinyi kafin na kwanta."

Tashi ta yi abinta ko waige babu ta ƙara gaba. A yadda Alh Audi yake jan Jamal da Tauhidat a jiki kuwa sai kunya ta rufesu. A fahimtarsu suna da laifi suma bai kamata ta bada wannan amsar ga mijinta ba a gabansu. Shi kuwa Shamsu da igiyar saki a hannunsa take da ta daɗe da bar musu gida. Fanna dai nata ido ne take ta rarrabawa a tsakaninsu.

A kunyace Jamal ya ce "Baba kayi haƙuri" ya kuma juya ga Shamsu shi ma ya bashi haƙurin. Tauhidat ma sahunsa ta bi. Alh Audi kuwa ya dinga rangwaɗa kai gefe kamar tsohon ƙadangare yana cewa babu komai tare da saka musu albarka. Kuɗi ya kawo masu tsoka ya damƙawa Shamsu.

"Gobe ka ɗauki ƙannenka kuje shopping kowa ya sayi abinda yake so."

A take ya raba kuɗin gida huɗu ya miƙawa Fanna kashi biyu na Kulsum da Aimana sannan ya bawa Jamal kaso ɗaya ya miƙe.

Alh Audi kuwa ya nuna kamar ransa ya yi masifar ɓaci ya daka masa tsawa "ba na son rashin hankali. Ina na Tauhidat? Ita da yayanta yaya Nannanku ta ɗaukesu saboda haka a wannan matsayin kai ma za ka mu'amalance su. Sannan cewa nayi kuje shopping ba a raba kuɗin ba."

Miƙewa Jamal ya yi da ido ya yiwa Tauhida inkiya ita ma ta tashi.

"Baba sammakal fa, no worries. Ni da ƙanwata zamu raba wannan. Ke muje."

Ita dai duk abinda aka yi babu wanda ya ɓata mata rai domin ta san matsayinta kuma ta riƙe shi. Tsoronta ɗaya bai wuce rigimar da ta janyo ba. Tun zuwanta gidan ta san Nanna da Baba da wuya su kwana uku ba ka ji tana maida masa magana ba. Tana matuƙar ƙaunar Nanna amma ta kasa fahimtar me yasa tsakaninta da mijinta ba irin yadda yake da Anti Fanna bane.

A koridon da zai sada Jamal da falon hanyar ɓangarensu ya tsaya ya bata kuɗin ko ɗaya bai zara ba. Girgiza kai ta yi ta ja baya. Ya murtuke fuska kuwa.

"Ina wasa dake ne? Come on karbi ki ware dare ya yi aje a kwanta."

"Nanna za ta yi faɗa fa."

"Ki ce mata yayanki ne ya baki."

"Yau kuma?" Ta ce da murmushi a fuskarta. Kememe yaƙi yarda ta kira shi Yaya ko Broda yadda take kiran Shaheed. Wai kara masa tsufa za ta yi ya tashi daga autan Nanna. Duk abinda suka yi a idon Haj. Manga, har kullum wadannan hallaye na Tauhidat su ke ƙara mata matsayi a zuciyarta.

Lokacin da Tauhidat ta shiga aji huɗu a sakandire ya yi daidai da kammala digiri ɗin Shaheed daga Abdullah Gül University a ƙasar Turkey. Zuwansa gida sau ɗaya tun bayan tafiyarsa. Duk lokacin da ya yi waya da mahaifinsa ko Tauhidat zancensa ba ya wuce na matsananciyar kewarsu da take damunsa. Su ma ɗin hakan take a wurinsu. Papa Abayomi ba ya gajiya da yiwa

jama'ar gidan nan hidima musamman Haj. Manga da Alh Audi. Sunyi masa komai a rayuwa. An raba yarsa da maraicin uwa ga makaranta mai kyau tana zuwa. Babban ɗansa kuwa sai son barka. A nasa ɓangaren shi ma Shaheed ɗin ba ƙaramin ƙoƙari ya ke yi a makaranta ba saboda kada ya bawa waɗannan mutane kunya. Burinsa ya dawo ya sami aiki mai kyau domin mahaifinsa ya huta.

Yau ta kama Juma'a shabiyu da rabi Tauhidat ta dawo gida. Tun a mota take yiwa Papa kuka yana bata haƙuri. Speech and Prize giving day ɗinsu zai kama ranar hutu ne suna ta shirye-shiryen gabatar da drama. An yi rehearsal (gwaji) na sati uku sai da ya rage kwanaki goma aka cire sunanta daga yan dramar wai ta fiye murmushi. Da yarbanci suke magana a motar hancinta ya yi ƙato saboda kumburi.

"Papa meye laifin yawan murmushi?"

"Babu" ya ce da taushin murya. Ya tabbatar da wuya idan Haj. Manga ba ta ɗora masa laifin saka ta kuka ba.

"A drama ɗin taku amma wane matsayi aka baki? Ana buƙatar yawan murmushi ko kuwa?"

Kai ta duƙar a hankali ta ce "ɓarauniya zan fito. Sata zamu je gidan soja a kama mu."

Abayomi ya kashe motar yana dariya "banda abinki ɓarawo ina ya ga ta dariya. Yana dariya fa za'a kama shi da sauran abokan sana'ar tasa."

Yadda taci burin dramar nan dole ta yi kuka. Jan hanci ta yi ta ce "to su bani police mana."

Dariya maganar ta bashi "kiyi haƙuri kawai, Police ɗin ma ai ba a son wanda basa iya rufe bakinsu. Sai a raina su."

Fushinta ta ƙaraci yi saboda ganin ya goyi bayan abinda aka yi mata ta haƙura. Alƙawarin tafiya da ita wurin Iyaa Bayo hutu da ya yi mata ne ya sanyaya ran ta. Ta saɓi jakarta za ta shiga gidan ya sake kiranta. Fuskarsa kaɗai ta sanar mata magana ce da ya ke so ta ɗauka da mahimmanci.

"Hajiya ta faɗa min zaku je a nema miki wata takarda da zaki iya zuwa wurin Shaheed jiya. Wai tana so muje graduation ɗinsa. Ni dai na faɗa mata ba zan je ba."

Tauhidat ta ce "Papa me ya sa?"

Murmushi ya yi mata ganin tana neman tayar da hankali "duka irin kyautatawar da ake yi mana a gidan nan kada ki manta matsayina bai wuce direba ba. Bai kamata na saki jiki nayi ta ƙara musu nauyi fiye da wanda suka ɗauke min na karatunku da ciyar damu ba. Kema ba don Hajiya ta nuna ɓacin rai ba da kinyi zamanki. Bana so a kwaɗaita miki rayuwar da ba taki ba."

Maganganunsa sun sanya jikinta yin sanyi. Nuna masa ta yi ita ma za ta cewa Nanna ba za ta ba ya ce kada ta soma. Ya gwada kuma tabbas ba ƙaramin ɓacin rai ta nuna masa ba. Nasiha dai ya dora mata irin ta uban da ya ke tsantseni da ƙoƙarin kare martbar iyalinsa a idanun masu kyautata masa.

Ɗakinsu da Nanna ta wuce kai tsaye da zummar kai mata ƙarar malamin da ya cireta daga drama. Ta yi sallama ta kai sau biyar a ƙofar ɗakin babu amsa. Nata ɗakin ta shiga da yake jikin na Haj. Manga ta cire uniform ta yi wanka. Sai da ta gama shiryawa ta shiga ɗakin da sallamarta. A zaune ta ganta bayanta jingine da gado da alamun sallah ta idar bacci ya ɗauketa a wurin. Fuskarta ta yi shatin hawaye da ya bushe ga hoto ta damƙe a hannunta.

Kwalla ce ta cikowa Tauhidat ta fita daga ɗakin da sauri. Bata da buƙatar neman bayani ta gama gane hoton da ya ke yawan sanya Nanna kuka. Hoton Jamal, babansu da ɗayan kamar yadda take kiran Arƙam. Tun bata daɗe da zuwa gidan ba ta san babbar damuwar mariɓiyarta. Nata ɗakin ta koma ta ci kuka ita ma har bacci ya ɗauketa.

Sai dare suka haɗu da Haj. Manga wadda ciwon kai ya hana fitowa. Kamar babu abinda ya faru haka ta sakarwa Tauhidat fuska tana ta tsokanarta akan cireta daga drama da aka yi ita kuma tana mita. Madam Zainaba sai kallonsu take yi ɗaya bayan ɗaya suna ta dariya cike da nishaɗi. Abu ɗaya ne zai tabbatar da farincikin Hajiyarta, bayyanar babban ɗanta. To ita ma Tauhidat ɗin abinda yake damunta kenan. Kwanaki ma sai da tayiwa malamin islamiyyarsu tambaya akan addu'o'in biyan buƙata. Amsar da ya bata take son faɗawa Nanna yanzu da ta ga hankalinta a kwance. Jira ta yi sai da Madam Zainaba ta tafi kwanciya sannan ta matsa jikinta. Shafa kanta Haj. Manga ta yi tana murmushi,

"Akwai magana a ɗan bakin nan namu ko Tauhida? Ya aka yi?"

Kai ta sunkuyar saboda nauyin abinda za ta faɗa. Sai da Haj. Manga ta sake tambayarta sannan ta faɗa mata malaminsu ya ce duk mai son biyan buƙata ya yawaita sadaka da sallar dare. Farinciki ne ya mamaye fuskarta bayan ta gama sauraron bayanin. Ko a mafarki bata tunanin akwai wata rana da za ta yi dana sanin sanya Tauhidat a ƙarƙashin inuwarta. Yarinya ce mai kyawawan hallaye da ɗabi'u, ga ta sam bata iya fushi ba. Fuskar nan kamar gonar auduga. Sai ayi abinda ya kamata taji haushi ta bar Nanna da ɓacin rai ita kuwa tana murmushi.

"Kin ga muna sadaka sosai Tauhida, kuma sallar ma ina ƙoƙarin yi cikin dare."

Keya Tauhidat ta sosa da ɗan murmushinta "Nanna harda kuka fa Malam ya ce. Muna addu'a muna ƙanƙantar da kai da kukanmu."

Haj. Manga bata san lokacin da ta rungumeta ba. Ba wai don bata yin ƙiyamul laili ba, sai dai maganar Tauhidat ta ƙara mata ƙaimi sosai. Sun ɗauki lokaci suna hira mai daɗi tsakaninsu, tana son ta tambayeta wannan ɗayan na jikin hoto amma kuma tana gudun ƙara mata damuwa. Da haka suka yi sallama, har ɗakinta ta rakata tana tunatar da ita yin alwala da kuma addu'a kafin ta kwanta ta ja mata ƙofar. Koda ta koma ɗaki zurfi ta yi cikin tunanin maganganun Tauhidat.

Karfe ɗaya da rabi na ranar kuwa alarm ɗin gefen gadon Tauhidat ya buga ta tashi daga bacci sosai a idonta. Ɗakin Haj. Manga taje ta tasheta. Alwala suka ɗauro suka tayar da sallah akan ƙatuwar dardumar da ta shimɗida musu. Tun a raka'ar farko ta soma gyangyaɗi saboda bacci. A daddafe ta karanta suratul A'ala a ta farkon da Nas a ta biyu. Tana sallamewa ta zauna kamar mai addu'a, nan bacci ya sake awon gaba da ita. Haj. Manga da ta yi kusan rabin awa a biyun farko tana sallamewa ta kalleta da tausayawa. Kafaɗarta ta dan bubbuga a hankali.

"Tashi ki hau gado kinji Tauhida."

Firgigit ta buɗe ido ta ce "Nanna kada mu manta da kukan, it is very important." Ta ɗaga hannuwa tana cewa,

"Ya Allah Ka bayyana mana ɗayan."

A haka akayi sallar rabi gyangyaɗi rabi ibada a gun Tauhidat har ukun dare sannan suka kwanta akan gadon Nanna.

***

"Dr. Karam idan baka yi hankali ba depression zai kama ka." Cewar babbar likitan ɓangaren Psychiatry na cikin asibitinsu. Maimakon ya nuna damuwa ko tashin hankali sai ya gyara zamansa kamar wanda ya ke kallon ƙayataccen shiri a TV.

Ta san za a rina, patient ɗin nata ba ya jin magana bare shawara. Dama can da ƙarfin tsiya Tomaz da Josh suka kawo mata shi. Abokin nasu ya canja sosai. Babu wani abu da yake burge shi yanzu, kullum cikin ƙunci zuciyarsa take. Ba don aikin da yake zuwa ba ma da al'amarin nasa sai ya fi haka ɓaci. Yanzu ta kai ta kawo ko bacci ba ya iyawa sai ya sha magani. Kuma sau tari kafin huɗu ya farka. Ya mayar da asibitin gidansa saboda ba kasafai yake tafiya gida ba. Duk likitan General Surgery department inda yake residency mai neman a kama masa aiki musamman call (aikin kwana) Arƙam yake bawa. Wuyarta ka ce masa yau kana da uzuri, ko tambayar ƙarin bayani ba zai yi ba saboda tuni ya gano ƙarya suke yi da yawansu. Aiki yake yi tuƙuru shi ya sa duka resident doctors ɗin ya fisu experience da gogewar aiki.

"Doctor da kai nake fa."

Cikin yanayin ko in kula ya kaɗa kafaɗunsa "ke ce likitan saboda haka ki faɗa min abinda ya kamata nayi?"

Girgiza kai tayi ta ɗauki waya ta kira shugaban General Surgery ɗin. Arƙam yana zaune ya lumshe idanunsa ya ji shigowar dattijon likitan. Ya riga ya san komai daga wurin matar shi ya sa bai ce masa komai ba ya kama hannunsa suka koma ɓangarensu. Ofishin Arƙam ɗin ya buɗe da ID card ɗinsa ya shiga ya ɗauko masa mukullin motarsa ya damƙa masa a tafin hannu.

"Dr. Karam na baka hutu, bana buƙatar ganinka a harabar asibitin nan sai na nemaka da kaina."

"Idan ka bani hutu me kuma ya rage min da zanyi da rayuwata?" Ya ce da wata irin murya mai nuni da ɓoyayyan ciwo a zuciya.

"Kaje club, ko wurin budurwarka ko kayi tafiya wani garin. Kawai ka nemi abinda zai baka nishaɗi. Arƙam rayuwarmu ta wuce zaman asibiti kawai. Kana da abokai da yan uwa. Ka nemesu kuyi wani abu na shaƙatawa."

"Patients ɗina fa?"

"Ni da kaina zan yi taking over."

Gajeriyar dariya ya yi saboda yadda ya ga babu fuskar musu. Shiga office din ya yi ya ɗauko yan tarkacensa ya zuba a jaka ya fita. Garin da alamun hadari duk da dare ne ana iya ganin yadda sama ta yi baƙi. Maimakon ya je kasan wurin parking ya ɗauko motarsa sai ya zabi yin tafiyar ƙafa saboda rashin nisa tsakanin gidansa da asibitin.

Tafiya yake cikin nutsuwa yana faman kwaɓar zuciyarsa daga karkata zuwa tunanin Nanna. Wannan hutun dolen ba komai zai janyo masa ba sai tunani. Ya zo daidai wani gidan sayar da abincin 'yan Pakistan daga gefe ya ji kamar ana kabbara. Tsayuwa ya yi cak ya dan koma baya yadda zai sake ji saboda ba a bari su saka spika su dami mutane a cewarsu. Ai kuwa Ladanin kamar ya sani cikin zazzakar muryarsa ya ce,

"SAMI'ALLAHU LIMAN HAMIDAN"

Wani irin gudu jinin jikinsa da ya tsinke a take ya soma yi. Dan leƙawa ya yi ko zai hango masallatan amma bai gano ba saboda sai an shiga wata ƙofar. To sallar me suke yi shaɗayan dare?

"Ohhh Shit!" Ya ce tare da sakin siririn tsaki. Shaf ya manta tun satin da ya wuce ake cewa watan Ramadan ya kusa kamawa. Har ga Allah Ya so yin azumin sai dai rashin mai tuna masa da kuma shi kansa da bai bawa addini mahimmamci ba ya sa shi mantawa. Juyowa ya yi da sauri da zummar barin wurin ya ji ya yi karo da wani.

"Subhanallah"

Mutumin ya ce lokacin da ya riƙe hannun Arƙam don kada ya faɗi. Kallon da yaga Arƙam din ya yi masa ne ya sa shi saurin bashi haƙuri "sorry, it is a Muslim expression (kayi hakuri, kalma ce da musulmi suke a amfani da ita.)"

Gyara zaman jakarsa ya yi a kafaɗa ya ɗago idanunsa ya zubawa magidancin mutumin da kallo ɗaya za ka gane ɗan ƙasar Pakistan ne "kada ka damu, na san ta. Nima musulmi ne."

Murmushi ne ya mamaye fuskar mutumin "Oh Masha Allah, mu shiga ciki. Kaima sallar taraweeh ka zo yi ko?"

Hannun Arƙam ya ja suka shiga ya kai shi har wurin alwalar maza.

"Idan kuma kayi alwala a gida ka wuce ciki nima zan shigo yanzu idan nayi."

Kamar wanda aka ɗaurewa harshe sai ya kasa cewa komai. Jakarsa ya ajiye a gefe ya yi alwalar sannan ya jira mutumin suka shiga masallacin tare. Ni'ima, salama, farinciki, tsoro da tararrabi ne suka dirar masa a lokaci guda. Yaushe rabonsa da shiga masallaci? Yau fa sallar safiya kaɗai ya yi don ba zai kirata asuba ba. Jiya bai yi azahar da la'asar ba. Shekaranjiya...lissafin bashi da daɗi. Mutumin na ƙoƙarin jansa sahun ƙarshe su tsaya kusa da mutane sai yaƙi binsa. A can ƙarshe ya tsaya ya kawo sallolin da ake binsa cike da wasi wasin samun karɓuwarsu. Yana masallacin aka idar da sallar taraweeh. Matsawa ya yi kusa da mutumin da ya janyo shi da sauri ganin ya miƙe. Tambayar da ya yi masa shi kansa sai da yaji kunya.

"Yau azumi na nawa aka yi?"

"Biyar" ya bashi amsa yana ƙoƙarin danne mamakinsa. Duk yadda aka yi yaron nan yana neman taimako. He looks lost. Wurin zama ya nuna masa "ka jira ni a nan na gama karatu don Allah."

Shi da ba gida yake son zuwa ba bai ga dalilin ƙi ba. Zama ya yi ga mamakinsa Limamin sai ya tashi mutumin ya maye gurbin zamansa. Dan matashin da ya yi ladanci ya turo masa speaker gabansa. Bayan sallama da ambaton sunan Allah ya soma tafsir na Suratul Isra'. Kamar ruwa ya cinye Arƙam haka ya zauna yana jin kalaman da suke fitowa daga bakin mutumin nan. Minti talatin da biyar da farawa matashin ya nuna agogo. Nan mutumin ya ƙarƙare karatun da doguwar addu'a kowa ya watse saboda dare ya yi sosai. Daga shi sai matashin sai Arƙam ya taso ya iso gabansa ya miƙa masa hannu.

"Suna na Luƙman amma anfi kirana da Abu Usama, wannan ne Usaman babban ɗana" ya nuna ladanin.

"Arƙam" ya ce a takaice.

Sai da ya sallami ɗan nasa ya ce ya jira shi a waje sannan ya ce "Na kula baka yi sallah tare damu ba. Sallar jam'i tana da lada mai yawa musamman ga shi watan azumi."

"Banyi azahar da..."

"Garin ya ya?" Abu Usama ya katse shi cike da mamaki.

"Ba matsalarka bace" Arƙam ya ce tare da juyawa ya fice abinsa.

Ajiyar zuciya Abu Usama ya yi saboda ƙarfafar zarginsa. Lallai yaron na tare da damuwa. Ya rasa dalilin da yake sa mutane sakaci da sallah kuma su nuna rashin damuwa akan girman laifinsu. Sai ka ga al'amuran rayuwarsu suna taɓarɓarewa su rasa gane dalili. Da sauri ya fita ya umarci Usama da ya bishi har gidansa saboda yana tunanin a kusa yake. Ya taɓa ganinsa har sau biyu.

Arƙam bai san ana binsa ba har gida. Abin mamaki condo (condominium jerin gidaje ne iri ɗaya hawa hawa. Ya kan kai hawa 20 ko sama da haka, kowanne hawa da gidaje aƙalla biyar) ɗinsu kusa da na su Abu Usama ne don gate dinsu ma daya. Sai dai shi nasu ya fi kyan tsari da tsada. Hankalin Arƙam din yana kan wayar da yake yi yana bayanin maganin da za a bawa wani patient ɗinsa bai kula da shigar Usama lift ɗin da ya tsayar ba. Shi kuwa yaro ya kare fuskarsa da hannu yana biye dashi har ƙofar gidansa a hawa na sha bakwai. A gida ya sami mahaifinsa ya faɗa masa. Da ya tambaye shi dalilin son sanin gidan sai ya yi murmushi.

"Nima ban sani ba Usama, haka nan nake jin ina son sanin damuwarsa."

Karfe huɗu da rabi assalatu take yi a ƙasar a lokacin, shan ruwa kuma takwas da arba'in na dare. Haka yake kasancewa a sauran ƙasashen duniya. Lokaci da yanayi suna canjawa tare da lokutan sallah. Uku daidai Abu Usama ya ƙwanƙwasa ƙofar Arƙam tare da sallama.

Idonsa biyu lokacin ya kasa runtsawa duk da tarin gajiyar da ya kwaso. Kamar daga sama ya ji bugu da sallama. Abin ya ɗaure masa kai amma haka ya je ya buɗe saboda kada maƙota su fara ƙorafi.

"What the fuc..." Kasa ƙarasawa ya yi saboda kwarjinin Abu Usama.

Mamakinsa ƙaruwa ya yi da ya ga shigo masa falo riƙe da wani abu kamar jaka ƙarama.

"Kayi haƙuri naga baka yi kama da mai aure bane shi ne nasa matata yin abincin sahur da kai. A block B gidana yake."

"I don't care, please get out!" Cewar Arƙam kamar ya sa ihu. Abu Usama sai ya nemi wuri ya zauna "kawo plate na nuna maka yadda ake ci. Beef Mandi ce da curry (wata na'u'in miya ta mutanen ƙasashen Asia). Ko ka taɓa ci?"

Rai a ɓace Arƙam ya ce "wai me ka ke nema a tare dani?"

"Abota."

"Ba na abota da waɗanda suka girmeni."

"Sai ka fara da ni. Yauwa me ya hana ka bacci?"

Ya ma dena mamakinsa sai ɗaure fuska da ya yi ya zauna. Abu Usama ya buɗe jakar ya zaro ƙananun robobi da matarsa ta zuba komai na haɗin abincin. Haɗaɗɗen ƙamshin na shiga hancin Arƙam wata muguwar yunwa ta dake shi sai da cikinsa ya yi ƙara. Abu Usama ya buɗe duka robobin ya tura masa gabansa.

Ɗage gira ɗaya tare da nuna abincin da hannu Arƙam ya yi "me ka ɗauke ni ne? Mara hankali? Ka shigo min gida da tsakar dare daga haɗuwar da bata wuce awa biyu ba ka ke tunanin zan ci abincinka."

Dariya ya bashi domin kuwa kallon yunwa sosai ya ga yana yiwa abincin. Cokalin da aka sako cikin jakar ya ɗauka ya ci daga cikin kowacce roba. Arƙam na ganin ya ci ya ɗauko wani cokalin a kitchen ɗinsa ya soma ci. Idan ka ga yadda yake yi sai ya baka tausayi. Da gani rabonsa da abincin kirki an kwana biyu. Damuwa taci ta cinye shi daga coffee sai dan abinda ba a rasa ba kamar biskit ko yayan itatuwa yafi ci a wurin aiki. Sai da ya gama tsaf ya tashi zai ɗauko ruwa ya yi kicin-kicin da fuska yana kallon Abu Usama.

"Bana son asarar abinci shi ya sa naci."

"Ka ji nayi magana ne?" Cewar Abu Usama yana ɓoye dariyarsa.

"Kafin kayi ne na faɗa maka dalili. Kada ka fara tunanin wani taimako kayi min babba, kai na taimakawa saboda matarka."

"Naji, yanzu dai kayi alwala mu tafi masallaci Usama ya kusa kiran farko."

Ɗan jim ya tsaya daga baya kuma yaje ya ɗauro alwalar ya dora jacket akan rigar jikinsa saboda sanyin asuba. Ba ya son faɗa amma yaji daɗin kasancewa da Abu Usama. Ashe haka ya yi kewar kusanci da musulmi ɗan uwansa bai sani ba. A hanyar masallacin babu abinda suka cewa juna. Bayan sun shiga ne Abu Usama ya ce suyi nafilar tahiyyatul masjid raka'a biyu. Idan Arƙam ya taba jin sunan wannan nafilar to ya daɗe da mantawa.

Da suka idar ya kuma saka shi yin ra'atainil fajr bayan kiran farko. Daga nan masallacin ya ɗan cika Limamin ɗazu wanda ya kasance ƙani shaƙiƙi ga Abu Usama ya ja su sallar asuba. Ana idarwa aka gaggaisa da gajeriyar hira kowa ya fita sai su biyu. Nutsuwar da yake ji ce ta sa ba ya son barin masallacin. Da wannan ɗaure fuskar don kada Abu Usama ya ce yana jindaɗi ya ce masa yana son zama a ciki. Zai jira zuwa wayewar gari har azahar idan sun zo sallah sai ya fita.

"Nima karatu zanyi sai na dan yi bacci zuwa safiya."

Ba haka ya so ba amma sai ya ce "idan ka san kana juye-juye ko minshari ka faɗa min nayi tafiyata gida. Bacci yana yi min wahala kuma motsi kaɗan ke tayar dani."

"Kada ka damu, karatun ma a hankali zan yi."

Can jikin bango Arƙam ya samu ya ɗan kwanta. Tun yana jin sautin ƙira'a mai daɗi daga Abu Usama har bacci mai nauyi ya ɗauke shi. Rabonsa da bacci irin wannan ba zai iya tunawa ba. Minsharinsa saboda rashin daɗin kwanciya ne ya ankarar da Abu Usama gare shi. Ya zura hannuwansa a cikin aljihu ya cure wuri guda kamar ƙaramin yaro. Ji ya yi yana son sanin sa. Yana son jin damuwarsa idan wadda zai iya ce sai ya taimaka masa.

Bacci ya yi daɗi ba shi ya farka ba sai da Abu Usama ya yi gyaran murya a spika zai kira sallar azahar saboda Usama na makaranta. A zabure ya tashi ya ga mutane uku a zazzaune suna karatu. Agogonsa ya kalla da sauri ya kalli lokaci, bai san sanda murmushin farinciki irin wanda ya manta yadda ake yi ya kwanta a saman kyakkyawar fuskarsa ba. Kana ganinsa ka san yana cikin farinciki. Mutumin farko da ya miƙo masa hannu su gaisa ya cewa

"Bacci nayi na awa takwas, awa takwas ko motsi ban yi ba."

Murna mutumin ya taya shi duk da mamakin da ya bashi. Sai da aka idar da sallah Abu Usama ya ce su zo su tafi gida kafin la'asar. Kiri-ƙiri ya ce ba zai tafi ba ai ba gidansu ɗaya ba. Sai da ya yi dariya yace masa saboda suyi wanka ne, yau ya janyo masa bai yi wanka ba har azahar. Haka nan ya bi bayansa yana ɓata rai.

A masallacin Abu Usama ya same shi kafin la'asar don ya riga shi zuwa. Magrib a nan ta riske shi. Ana buɗa baki lokacin ƙamshin girke girken restaurant ya cika harabar wurin da kewaye. Maza da mata haka aka yi ta tururuwar shiga. Ruksana matar Abu Usama ita ce ke shugabantar komai. Ita da matar ƙaninsa da wasu maaikatan ke girki, samarin yayansu da masu tayasu aiki su rarraba zuwa kowane tebur. Musulman kusa da na kewayensu haɗa kudi suke yi domin ciyar da junansu da azumi. Wadataccen abinci Ruksana ta zubawa Arƙam ta ajiye masa a gabansa tana murmushi.

"Yau abincin daban aka yi saboda kai. Ina fata zai yi maka daɗi."

Ba ƙaramin daɗin karramar da aka yi masa ya yi ba "Nagode, amma ya akayi ki ka san zan zo?"

"Duk masu zuwa masallacin nan yan uwan juna ne a musulunci. Muna maka barka da zuwa Brother Arƙam" cewar wani dattijo da ya fi kowa tsufa a wurin. Idanunsa ne suka ciko da ƙwalla da irin kulawar da mutanen suka bashi. Daga ranar ya mayar da masallacin nan gidansa na biyu. Kamar haɗin baki da shugaban sa a wurin aiki bai neme shi ba har sallah ta gabato. Tsakaninsa da Abu Usama kuwa tun yana sharewa har sabo mai ƙarfi ya kƙullu ta yadda kullum suna tare. Duk tsahon lokacin nan bai taɓa tambayarsa labarin komai a kansa ba har aka yi sallah. Ibada musamman nafila da karatu su ya dinga nusar dashi da dabara ta hanyar cewa suyi tare. Sun idar da sallar idi yanayin wurin na haɗuwar musulmai ya ƙayatar da shi matuƙa. Hawaye ya goge a fakaice wanda Abu Usama ya gani. Daren ranar fa kansa ya je gidansa ya bashi labarin irin rayuwar da ya yi a ƙasar da banzatar da rayuwarsa da mahaifiyarsa ta yi. Abu Usama shawara ɗaya ya bashi

"Ka yi ƙoƙarin daidaita tsakaninka da Mahaliccinka Shi kuma zai daidaita maka duk wani abin da ya shige maka duhu game da yan uwanka"

***

Anyi sallah da sati ɗaya Tauhidat da Papa suka dawo daga Abeokuta. Lokacin saura kwanaki shabiyu tafiyarsu Turkey, duk wani shiri da ya kamata sun gama yi sai jiran rana.

Washegarin dawowarsu Baffa Alƙali ya sauka a garin Kano batare da sanin kowa ba cikin yayansa. Motar da aka turo ɗaukarsa kai tsaye Kano Tropicana Hotel ta wuce dashi. Direban motar ya faɗa masa lambar ɗakin da zai je. Da sassarfa ya shiga aka karɓi jakarsa. Bayan ya faɗi sunansa a ƙagauce ya ce akwai mai jiransa a ɗakin da ya basu lambar. A reception ɗin an riga an sanar da zuwansa su ma basu ɓata masa lokaci ba aka yi masa jagora.

Girma da shekaru basu rage masa kuzari ba. Da zafinsa yake tafiya har ya isa bakin ƙofar ɗakin. Yana murɗawa cikin Tony PA ya karta saboda tsabar tsoro. Baffa na shiga kuwa ya yi kansa gadan-gadan ya zaro kwalin DVD ya cilla masa a fuska. Muryarsa har korido ɗin waje ana ji lokacin da ya ce,

"Tony nawa na baka akan Arƙam? Nawa na kashe iya ni da kai da kuma a gaban Haji Lawalli akan yaron nan? Amma shi ne ka kasa cewa komai sai da al'amura suka ɓaci gabaɗaya ka turo min wannan abin. Arƙam ya zama mawaƙi ya gama zaga duniya."

Zuciyarsa tamkar ta buga haka yake ji. Haji Lawalli da ke zaune a kan kujera ya dafe kai ya taso ya riƙo hannunsa "Baffa kayi haƙuri, yanzu abinda ya kamata mu sani shi ne ko Haj. Manga ko Jamal sun taɓa gani."

"Manga bata sani ba domin ko da wasa idan ta sani ba za ta ɓoye min ba."

"To yanzu me ya kamata muyi?" Cewar Haji Lawalli.

"Idan kana da visa to a shirye nake mu bar ƙasar nan jibi don na riga na sayi ticket ma." Baffa ya ce tare da hararar Tony wanda bakinsa ya yi nauyi saboda firgici.

"Saura bai fi wata biyu ta yi elapsing ba. Ina fita daga nan zan fara processing ticket ɗin ko ba rana ɗaya da kai bane dole nima na je."

Yadda Tony ya tsorata yasa Haji Lawalli ƙarawa da cewa ya kwana da shirin sai sun ɗaure shi. Baffa kuwa ji yake kamar ya tashi ya shaƙo wuyansa don baƙinciki.

"Wane irin rashin imani da rashin tausayi gareka da ubangidanka? Ashe hawayen da ya ta take zubarwa bai isa ya sa ku tausaya mata ba? Musamman ma kai Tony. Na daɗe da tunanin lallai Alh. Audi ne ya ɗauke min jika. A matsayinka na PA ɗinsa ba irin kyautar da bana yi maka da roƙo guda ɗya tak, idan ka ji labarin Arƙam ko nawa ka ke so zan baka ka sanar dani."

Haji Lawalli fuskarsa ta yi rauni matuƙa ya ce "kayi haƙuri Baffa, ko babu komai mun san inda zamu same shi yanzu."

"Bayan ya zama mawaƙi? Mawaƙin ma a ƙasa kamar America. Lawalli ɗan Ibrahim ne fa da kitso a kansa. Ya ya Manga za ta ji?" Baffa ya ce muryarsa na rawa ga ƙwalla ta ciko a idanunsa.

Tony dai nasa ido ne. Bayan ya ji shiru Arƙam bai zo ba hankalinsa ya ɗan kwanta. Sai kwatsam satin da ya gabata yaci karo da album ɗinsa a DVD ana saidawa a junction. Ba don ya san shi da kitso ba da ba zai gane shi ba. Mafita ɗaya gare shi wato neman Baffa tunda ya daɗe yana bibiyarsa akan jikan nasa. Ko ba komai zai roki alfarmar su yi masa hanya shi da matarsa su bar ƙasar kafin asirinsa ya gama tonuwa. Abu ɗaya yake son warware musu saboda tarar Alh. Audi da rigima sai mutum ya yi shirin gaske.

"Ranka ya daɗe wallahi Alh. Audi bashi da masaniya akan inda Arƙam yake. Shi ma nemansa yake yi."

Baffa ya ji kansa ya kulle "to wa kake yi wa aiki?"

"Ba zan iya faɗa ba domin makusanci ne ga Alh. Audi and he is very dangerous."

Da sauri Haji Lawalli ya ce "Alh. Ari? Lallai amma mutumin nan baƙin munafiki ne."

"Bani da tabbacin ko shi ne. Ni kaina ko wuƙa za a saka min bana ce gashi ba. Amma na tabbatar yana tare da Alhaji."

Ɗaukar maganar tasa suka yi a matsayin salon rainin wayo. Abinda ke gabansu yafi ƙarfin lallaɓa Tony ya haɗasu da ɓoyayyen ubangidansa. Cheque Baffa Alƙali ya damƙa masa

sannan suka fita shi da Haji Lawalli zuwa Central Hotel inda zaiyi masauki kafin shi kuma ya sayi ticket.

Bayan tafiyar Haji Lawalli da daddare ya dlɗauko wata jaka da yazo da ita ya baje takardun cikinta akan gadonsa. Duk wani abu da ya kamata ayi na cike-cike akan su anyi an gama saura sa hannunsa ya rage. Takardu ne na dukiyar gadon amanarsa Hafsatu Manga. Bayan rasuwar ƙaninsa da matarsa shi ya ajiye mata gadonta daga baya ya saya mata hannun jari dasu. Tsautsayi ya sa kamfanin ya kusa durƙushewa mutane suka ɗibga asara. Da yawa tun a lokacin an biya su kuɗaɗɗnsu. Baffa Alƙali kuwa duk da mutum ne mai zafin zuciya yana da kawaici. Shugaban kamfanin amininsa ne. Nauyin neman a biyasu ya ji ya kasa cewa komai. Bai ɓoyewa yar tasa ba da mijinta Ibrahim a lokacin. Alfarma ya nema da su ƙarawa mutumin lokaci tunda ya ce yana jiran kammaluwar wani contract domin tabbatar da asara ta hau su da gaske ko akwai kofar farfaɗowa. Allah Rahimi kamfanin ya farfaɗo da ƙarfinsa bayan shekaru sai ga dukiya ta haɓɓaka na ban mamaki.

A lokacin da ya ke shirin mallaka mata komai ne Alh. Audi ya shammacesu ya kwace plaza ɗin da ta gina. Ya san irin yadda ta shiga tashin hankali ga rashin nutsuwa saboda Arƙam. Wannan ya sa ya dakatar da bata kuɗin tukunna saboda gudun kada Alh. Audi ya sami kmƙofar wawashe mata dukiya a yanayin da take ciki. Yanzu kuwa da ya ke da yaƙinin gano jikansa ya tabbatar zai iya bata kuɗinta ta juya yadda ya kamata. Ya duƙufa yana ta rubuce-rubuce wani tunani da shi ko wani nasa a iya saninsa basu taɓa yi ba ya ɗarsu a zuciyarsa. Ina dukiyar Manga, Arƙam da Jamal ta gadon da Ibrahim ya rasu ya bar musu? Yaushe dukiya da gumin Ibrahim Iro Karam ta koma ta Audi Iro Karam?

Zumbur Baffa ya tashi daga kan gadon ya ɗauko wayarsa da ke caji hankali a tashe. A shekaru goma sha ɗaya da watanni da rasuwar uban yayan Manga amma ba a raba gado ba. Yana ina haka ta faru? Ko shi ya sa suka damu da ƙwace kamfanin daga hannunsa batare da sanin ƙwaƙƙwaran dalilinsu ba? Sun dai san kawai kamar haƙƙinsu ne. Tunowa ya yi da kaɗan cikin maganganunsu da Alh. Audi ranar da aka taru da sunan rabon gadon ya dafe kansa. Akwai wata a ƙasa! Lambar babban ɗansa Ali ya kira amma abin mamaki sai ya nemi dalilin kiran ya rasa. Tamkar wanda aka shafewa kai ko kaɗan ya kasa tuna

me yasa ya kira. Karshe sai gaisawa suka yi ya tambayi lafiyar iyalinsa ya aje wayar.

Da mummunan ciwon kai ya kwana a daren. Washegari da yamma Haji Lawalli ya sayi ticket suka shirya komai na tafiya. Ba za su sanar da Haj. Manga ba sai sun ga ga su ga Arƙam ba wai wai ba. A ranar da suka tashi zuwa USA daga Lagos a ranar ne kuma Oga wato shugaban su Alh. Audi ya tashi daga bacci a firgice. Mafarkin wata guguwa ya yi wadda ta nufo Alh. Audi da ƙarfinta. Karfin wannan guguwar har ya fi irin wadda ya gani game da Arƙam da Tauhidat. Tashi ya yi a hankali ya sauka daga kan gadonsa. Wata durowa ya buɗe ya ɗauko wani ƙyalle wanda yake ɗauke da jinin Alh. Audi da ya yi masa aiki a kai shekarun baya. Bayan ya gama aikinsa akan idon Alh. Audi jinin ya rabe kashi uku. Oga ya fassara masa wannan rabuwar a matsayin mutane uku da zasu iya zama barazana gare shi. A haɗuwar farko lokacin ta'aziyya ya gane Arƙam. Guguwar Tauhidat ita ta sanar da zuwanta. To waye ko wace na ukun?

***

Ranar talata su Baffa suka bar Nigeria suka sauka a Baltimore/Washington International Airport. Ba don dare ba a ranar za su wuce Johns Hopkins Medical School inda Tony ya faɗa musu Arƙam na karatu. Baffa bai iya runtsawa ba sai addu'ar da ya kwana yana yi domin komai ya zo musu cikin sauƙi. Gari na wayewa kuwa ko karyawa basu iya yi ba suka tafi makarantar.

Ɗalibin farko da suka tambaya abin mamaki garesu ya san Arƙam. Da initials ɗinsa ya kira shi wato AIK. Yanayin tsayinsa da na Baffa duk da tsufa ya kama shi ya sa shi gaskata maganarsa ta cewa shi kakansa ne. Sun kawo masa ziyara amma sun kasa samunsa a waya shi ne suka zo makarantarsu. Cafeteria ya kaisu wurin Raymond ya ce babu inda zasu sami cikakken bayani akansa sama da nan.

Addu'a takobin mumini, duk tsirfa irin ta bature amma Raymond bai iya yiwa su Baffa tambayar kwakwa akan Arqam ba ya basu nambar wayarsa, adireshin gidansa da sunan asibitin da yake residency. Ya sha godiya kamar su ari baki. Bayan fitarsu ya kira Arƙam don ya faɗa masa kakansa ya zo amma bai ɗauka ba. Josh ya nema ya sanar da shi cewa daren jiya ya yi call bai daɗe da tafiya gida ba. Indai bai amsa waya ba ta yiwu bacci yake yi. Kafin a barsu su shiga security ya

tambayesu wurin wa suka zo da nambar apartment ɗin. Sun bashi suna sa komai amma duk da haka sai da ya kira gidan Arƙam da layin da ake kiran mazauna condo ɗin.

Cikin bacci ya ji waya da ƙyar ya iya buɗe idanunsa. Yanzu kam Alhamdulillah ba kamar da ba yana samun bacci. Kara wayar ya yi a kunne aka sanar da shi yana da baƙi. A tunaninsa su Abu Usama ne har yana jin haushin me ye kuma na tsare shi bayan shi ma a daya block ɗɗn yake.

"Na san da zuwansu ku barsu su hawo." Ya ce ya ɗauki pillow ya danne kansa yana ihun an hana shi bacci. Yau sai ya yi wa Abu Usama bore ko ya saka shi zaman gadinsa a masallaci ya runtsu ko na awa ɗaya ne.

Haji Lawalli da Baffa sai baki ya mutu a lokacin da lift ya buɗe a hawa na sha bakwai. Jikinsu sai ya soma sanyi da fargabar rashin sanin irin tarbar da zasu samu. Kada ya watsa musu kasa a ido ya nuna bai san su ba. Hannun Baffa dai tuni gumi ya jiƙe shi a haka ya soma ƙwanƙwasa kofar tare da sallama. Wata doorbell nan da ya gani bai ma yi tunanin dannata ba. Allah Ya so kan Arƙam babu kitso sai uban tulin gashi da kasumba da ta sha gyara. Tarawa yake saboda ƙoye kansa daga mutane masu hana shi nutsuwa ya yi aikinsa a asibiti. Daga shi sai wando 3-quarter baƙi da farar vest ya zo ya buƙe ƙofar. Da farko juyawa yaso yi tunda gidan ba baƙon Abu Usama bane sai kuma ya juyo da sauri yana kallon mutanen da suke tsaye a bakin ƙofar gidansa.

Wani irin kallon tausayi, kewa da dumbin soyayya suke yi masa. Tsohon kuwa ƙwalla ta cika masa idanu har ta fara gangarowa kan kumatunsa. Shi Arƙam yafi kallo gabansa yana faɗuwa sosai. Ya gane su sai dai yana gudun ko mafarki yake yi. Jiki a mace ya dafa bango da hannunsa ɗaya tare da runtse idanu shi ma yana hawaye.

Cikin yaren hausa da ya kwashi shekaru rabonsa da wani ya yi masa magana dashi Baffa ya yi masa magana muryarsa na rawa.

"Jikana Arƙam Ibrahim Karam muke nema."

"Baffa..."

Arƙam ya ce kamar me raɗa kafin ya ankara Baffa ya janyo shi jikinsa sun rungume juna. Sun ɗauki kusan minti uku kafin ya iya sakin Baffa ya koma kan Haji Lawalli.

"Baba Lawalli ashe baku manta dani ba?"

Koke-kokensu suka sha a bakin ƙofa sannan suka shiga ciki. Arƙam gani yake kamar mafarki ne ba gaske ba. Suna zama ya ce "Baffa ina Nanna? Me na yi bata son ganina kuma?"

Abinka da rashin samun wanda zai yi magana da yarensa da shi, gabaɗaya bakinsa ya juye. Hausar ta sa a turance take fita kuma a birkice.

"Nannanka tana nan lafiya. Bayanin namu da tsaho ba maganar da zamu yi a tsaye ba ce." Haji Lawalli ya bashi amsa.

"Na zauna. I am listening (ina sauraronka)" ya faɗa lokacin da ya zauna a kusa da Baffa da ya kasa cewa komai sai kallonsa kawai. Murmushi Baffa ya yi,

"har yanzu baka girma ba, ji yadda kake hawaye kamar wani yaro."

Goge hawayen ya yi da saurinsa "Am sorry, now please tell me about Nanna and Jamal."

Bai barsu sun yi motsin kirki ba sai da suka faɗa masa abinda suka sani game da ɓatansa. Mamaki sosai ya kamashi shi ma ya faɗa musu yadda Tony ya rabo shi da waccan makarantar da wayoyinsu hadda zancen Madam Zainaba. Kansu kullewa ya yi saboda abin ya ƙara rikice musu. Baffa ne ya ce su kwantar da hankulansu da sannu zasu binciko komai har ƙarshe. Arƙam na jin haka ya ce bari ya shirya ya kaisu su ci abinci sai ya duba ko akwai jirgi su yi booking zuwa Nigeria a yau. Haji Lawalli ya ce masa "Yi hakuri Yallaɓai, kai da zuwa gida sai mun gane waye yake harinka kuma me ya sa."

Kallon wasa ku ke yi ya musu kafin ya ce,

"Nanna kuma sai na haƙura da ita?"

"Nanna za ta zo gareka" cewar Baffa.

A lokacin ya buƙaci su bashi nambarta ya kira. Baffa ya soma ja masa rai yana cewa shi fa yunwa yake ji. Kamar yasa ihu ya ɗauki waya ya kira Abu Usama. Order ya yi musu na special abincin wurinsu sannan ya ce duk wanda yake cikin restaurant

din a lokacin a maida masa kuɗinsa a haɗa masa bill. Da aka kawo abincin ya biya yaron da ya kawo ya jera musu komai akan dinning table suka zauna. Hannu ya miƙa musu "please ku bani phone number ɗinta."

"Sai ka zauna mun ci abincin tare" Baffa ya kuma tsokanarsa.

Haji Lawalli yana dariyar yadda ya ɓata fuska ya miƙa masa tasa wayar bayan ya danno sunanta. Yana faɗa masa cewa bashi da sim din kasar a ciki Arqam bai saurare shi ba ya shige ɗakinsa zuciyarsa na bugawa da sauri da sauri.

***

Tazarar awa bakwai ne tsakanin America da Nigeria. Ƙarfe shabiyu saura na rana a wurinsu Arƙam ya yi daidai da bakwai saura a Nigeria. Haj. Manga da Tauhidat basu daɗe da shigowa gida ba. Siyayyar kaya ta yi mata na tafiyarsu Turkey akwati guda. Tauhidat ta riga idar da sallar Magariba tana azkar wayar Nanna ta fara ringing. Ita kuma lokacin raka'ar farko ma take. An kira sau biyu a jere a na ukun sai ta ɗauka domin ta bawa mai kiran hakuri. Baƙuwar namba ta gani ta kasar waje kamar kada ta dauka sai wani kiran ya sake shigowa ta kara wayar a kunnenta.

Alamun numfashi kawai Arƙam ya ji cikin wata irin murya da ta yi sanadiyar tayar da tsigar jikin Tauhidat ya ce, "Nanna, ni ne?"

A hankali Tauhidat ta ce, "Nanna tana sallah. Ka kashe idan ta idar sai ta kira ka. Wa zan ce mata?"

Yadda muryarsa ta janyo gudun jinin jikinta ya ƙaru haka shi ma ya sami kansa da shiga wani yanayi na takaitaccen lokaci a dalilin jin ƙaramar muryarta.

"Wa zan ce?"

Ta sake tambaya da dan ƙarfi jin ya yi shiru. Tsoron kada a sake maimaita masa irin yadda matar da ke kiran kanta Madam Zainaba ya sa shi cewa,

"No. Wait. Please don't disconnect the call (A’a, tsaya, don Allah kada ki katse kiran)!"

Ya faɗa da sauri. Yadda ya yi magnar tsoro ya bata, a ɗarare ta sake cewa, "za ta kira idan ta idar."

"Kiyi min hira kafin ta idar kinji. Ya sunanki?" Ya sami kansa da cewa da taushin murya. Haka kawai ba zai kuma yarda da irin excuses ɗin da aka dinga bashi ba a shekarun baya ba. Idan zasu kwana akan waya a shirye yake har sai Nanna ta idar ta karɓa. Tauhidat gabaɗaya sai ta rasa abin cewa. Kallon Nanna ta yi ta ga a raka'ar ƙarshe take sai ta murmusa. Ko waye wannan ita dai bata son tsawaita magana dashi saboda yadda ta tsinci kanta a wani baƙon yanayi. Kuma ma bata san sunansa ba shi zai nemi sanin nata?

"Kai ya ya sunanka?"

"Arƙam" ya bata amsa a takaice.

Bata san lokacin da ta sake ƙanƙame wayar ba hankalinta a tashe tana kallon Nanna da ke zaman tahiyya ta sake tambayarsa sunansa domin tabbatarwa. Muryarta har rawa take yi alamun ta soma kuka.

"Me ka ce? Sake faɗa don Allah"

Yanayin tambayar ya tabbatar masa da ta ji abinda ya ce da farko.

"Do you know me (kin sanni ne)? Nanna tana yin maganata dake?"

Fashewa kawai ta yi da kuka "tana yi, kullum sai ta yi. Da gaske kai ne?"

"Kuka ki ke yi? Kema kin damu dani ne?" Ya ce da mamakin ita wace da ta damu dashi haka.

"Sosai!"

Nanna ta sake kallo lokacin ta sallame sallar ita ma ta ƙura mata ido. Suna haɗa ido kuwa ta yi mata alama da ta kashe wayar. Ko waye bata ga dalilin da zai saka mata ya kuka ba. Maimakon ta kashe sai kawai ta saka wayar a speaker ta ƙure sautin sannan sannan ta rarrafa kusa da ita tana murmushi haɗe da hawaye. Kamar daga sama, tamkar saukar ƙanƙara a zuciyar da wuta take ruruwa a cikinta Haj. Manga ta ji muryar Arƙam ta doki kunnuwanta. Muryar da daɗewar shekaru da ƙaruwar sautinta ba zai sa ko a mafarki ta manta da ita ba tana cewa, "I miss her so much. Ki faɗawa Nanna ta yafe min ta yi magana dani. I have a lot to say."

A hankali Tauhidat ta gyaɗa kai kamar yana kallonta yayin da wasu zafafan hawaye suka shiga kwarara daga idanun Haj. Manga. Runtse idanu kawai ta yi tana fatan idan mafarki ne Allah Ya tsawaita mata shi.

Kukan da Haj. Manga take yi ba karamin tsayawa Tauhidat a rai ya yi ba. Ga muryar Arqam tana ji yana ta cewa "hello" cikin tashin hankalin rashin amsa masa da aka yi. Dora mata wayar tayi a tafin hannunta kamar mai bada umarni ta ce, "Ki yi masa magana."

Kai ta gyada kawai ta sake fashewa da wani kukan a lokacin da Tauhidat ta tashi a guje ta fita daga dakin. Nata dakin ta shiga ta dauko wani envelop a cikin tsohon akwatin mahaifiyarta. Hotunansu ne da Aunty Bimbo da yawa ta rungume daya tare da fashewa da kuka mai tsuma rai.

Haj. Manga kuwa kasa motsa bakinta tayi sai kukanta da ya tsananta. Jin muryar Arqam ya wanke mata damuwa sannan ya dawo mata da wata damuwar. Rayuwar da a da take ta ganin za ta dauwama a ciki ke mata gizo a kwakwalwa. Lokutan da take tare da Ibrahim da irin dumbin soyayyar da yake nuna musu ita da 'ya'yanta. Saboda irin abin nan na dan fari da take gwadawa Arqam yasa shi jansa a jiki sosai. Yadda Ibrahim dinta ke da sanyin hali haka dansa yake. Duk wannan tunanin tana yinsa ne yayin da hawaye ya jike mata fuska da hijabi.

Shi kuma jin shiru yasa shi komawa falo zai roki su Baffa da su taimaka su bashi lambar da zai sameta sai ji ya yi cikin dasashshiyar murya ta ce,

"Sai yau Arqam?"

Duk girma da ji da kan namiji, karamin yaro yake a wurin mahaifiyarsa. Tsigar jikinsa gabadaya ta mimmike saboda yadda muryarta take kwarara tana bin sassan jikinsa. Jagwab haka ya zauna akan kujerar da tafi kusa dashi yana zubar da hawaye masu zafi.

"Ba za ka yi min magana ba Yaron Abba?" Ta ce da wata irin murya mai cike da shaukin tuna baya.

Rabon da yaji wannan suna tun ranar da mahaifinsa zai rasu yana bar masa wasiyar kulawa da Jamal da Nanna.

"Nanna kinyi fushi ko? I am so sorry."

Ji tayi inama za ta iya zura hannu ta finciko shi daga wayar ta rungume.

Rarrashinsa take so ta yi "Banyi fushi ba, ka daina kukan haka."

"I am sorry, anyi min karya da yawa but still I should have come home (duk da haka ya kamata ace na dawo gida)."

Bata son jin wani dogon bayani yanzu. Lafiyarsa ta damu ta sani tukunna. Suna kukan farinciki a gefe Baffa da Haji Lawalli na kallonsa. Haj. Manga ta shiga jero masa tambayoyi wata na bin wata ko amsa ba ta jira.

"How are you? Kana cin abinci? Kana karatu ko ka gama? Kila ma kayi aure har matar ta haihu? Allah Yasa musulma ka kwaso dai. Ka kara tsayi kuwa? Lokacin da ka tafi ba ka da wani jiki... "

Dariya ya yi ga hawaye "all these questions Nanna na dade ba a yi min su ba. Ina lafiya. Ba na cin abinci sosai. I am taller dan Baffa (na fi Baffa tsaho)."

Baffa ya share kwallarsa yana murmushi ya dawo kusa dashi ya zauna.

A razane Haj. Manga ta ce "auren fa? Kada kace min da gaske kayi kuma ba musulma bace."

Bai san lokacin da dariya ta kufce masa ba "babu mata Nanna, ni kadai ne. And am a third year resident doctor."

"Masha Allah" take ta cewa ta mike da sauri ta tafi dakin Tauhidat. Tambayarta yake yi ina Jamal ta ce yana makaranta amma ga kanwarsa da bai sani ba.

Akan gado ta sameta tana risgar kuka amma ganinta yasa ta boye hoton saboda kada taji ba dadi. Bata rasa komai na soyayya da gata a wurin Haj. Manga ba. Shi ya sa bata cika son tayar mata da hankali ba. Gani take yi kamar za ta ga ta raina kulawar da take bata ne.

Wayar ta dora mata a kunne bayan ta rungumeta suna kukansu. Cike da murna ta ce "kin ji Tauhida Dayan ne ya kirani. Ashe bai manta dani ba. Ashe ina ransa."

Farincikin da take ji yayi mata yawan da ita kadai ba za ta iya rikonsa a zuci ba. Haka nan saboda doki ta manta ma Tauhidat din ce ta amsa wayar.

"Arqam ga Tauhida."

Muryar da tayi masa sallama dazu da ta dauki wayar ita ya sake ji ta daki dodon kunnensa.

Daga sallamar sai ta rasa abin fada musamman saboda ganin yadda Nanna ta tsareta da idanu tana ta zuba murmushi.

Shi ya katse shirun ta hanyar cewa "thank you Tauhida. You have won my heart (kin saye zuciyata) tun kafin mu hadu."

Zaro idanu tayi a tsorace "Eyye?"

Cigaba da magana ya yi abinsa don bai ganin ya fadi karya a maganarsa.

"Kin bawa Nanna waya when I asked. Hakan ba karamin abu bane a wurina. Kuma ta ce ke sister dina ce. Can't wait to meet you."

"Nima haka" ta ce a kunyace. To me za ta ce sama da hakan?

Haj. Manga ta sake karbar wayar ta cigaba da yi masa tambayoyi. Nan ta zauna tayi kuka tayi dariya kamar yadda yake yi a nasa bangaren. Sun kwashi awa guda kafin hirar ta karkata zuwa bayanin cewa Baffa da Haji. Lawalli ne suka zo gidansa. Daga nan Baffan ya karba ya mata takaitaccen bayani da kwabarta akan kada kowa ya san sun ganshi a gidan. Da ta tambayeshi ko zasu taho gida tare ya ce a'a. Ya bata yau zuwa gobe ta san yadda zata yi ta nemi izinin mijinta ta taho batare da ya zargi komai ba. Ya yarje mata ta ce shi ne bashi da lafiya ya tafi check up bai sanar da kowa ba sai yanzu. Da kyar suka ajiye wayar ita da Arqam sannan ta kira Jamal da kyakkyawan albishir.

Shi kuma Arqam tsare su Baffa ya yi da tambayar wa take aure yaji ance mijinta. Ai sai da ya yi dana sanin tambaya kuwa domin Baffa na cewa kawunsa ne Audi yaji kamar duniyar ce ta kife dashi. Bai taba kaunar Kawun nasa ba tun fil'azal jininsu bai hadu ba. Sai kuma wani abu da ya taba gani wanda ya tsaya masa a kokon rai. Tsautsayin da ya sami Abbansa a ranar ne ya mantar dashi abinda ya gani. Wane irin mutum ne zai

daga hannu ya shake wuyan kanin mahaifiyarsa? Babu magana guda da suka yi da ya iya ji sai wannan shakar da ya hango da dan manuninsa da ya nuna shi dashi yana masa gargadi da kakkausan harshe.

Girgiza kai ya yi bayan Baffa ya fada masa cewa dalilin nemansa ne ta aure shi.

"Tunda an ganni sai ya saketa. Kuma guda ukun zaiyi mata." Ya ce a kufule.

"Arqam ka bari a nutse idan ta iso za ka ji komai. Kai da ka ke farincikin haduwa da ita kada tunanin Audi ya dameka."

A tsorace ya ce da Baffa "Allah Yasa dai ba ta son shi."

"Bata son shi kaji. Bata taba son shi ba kuma ba za ta taba ba. Ka sa ranka a inuwa." Baffa ya amsa masa da murmushi.

***

Alh. Audi ya gama jin bayanin Haj. Manga tsaf ya kwantar da murya kamar gaske.

"Yanzu shi Baffa sai ya tafi har America check up bai fadawa kowa ba?"

Tabe baki tayi ta gyara kwanciyar Tauhidat da tayi pillow da cinyarta tana sharar bacci.

"Kaima ka fada, ya kasa gane cewa ya tsufa dole ya nemi mataimaki. Yanzu gashi ya je ance sai an ajiye shi for observation. Yayun nawa kuma babu mai visa shi ya sa nake son tafiya."

Kwalbar giyarsa ya daga ya ga babu saura a ciki ya mike zuwa fridge din dakin hotel din da ya yi masauki a kasar Japan ya dauko wata. Sai da ya kurba ta sauka a tulelen cikinsa sannan ya bata izinin tafiya harda alkawarin kara mata guzuri da shawarar ta tafi da Jamal. Dama ko bai fada ba ai dole ne zuwa dashi. In don karatunsa ne carry over yana da ita tafi cikin kwando. Zuwa ganin dan uwansa ba zai rage masa komai ba. Ajiye wayar tayi ta buga tsaki shi kuma yana jin ta kashe ya soma dariyar mugunta.

"Shegen tsoho, Allah Yasa daga nan ka sheka kowa ya huta."

***

Jirgin safe Jamal ya biyo daga Adamawa zuwa Abuja washegari. Haj. Manga ta hada shi da Tauhidat ta ja musu kunne akan ko da wasa kada su taba zancen ganin Arqam da akayi da kowa. Shi dai yana mamakin yadda take yiwa baban nasu boye-boye tunda har yau idan ka cire kwace plaza bai ga aibunsa ba. Tauhidat kuwa bata taba yi mata musu. Shi ya sa ma bata ji bacin rai ba da ta bata hakuri akan soke zuwansu Turkey.

"Bazan yarda bane ki tafi ke kadai tare da Fanna ta bar miki raino. Da ace rainon ma da zuciya daya ne bazan damu ba. Amma ba kirki gareta ba. Sai ta kuntata miki kafin ku dawo."

Jamal da ke sharce cukurkudadden gashinsa mara aski da gyara ya ce "to mu tafi da ita mana."

Cike da damuwa ta ce "bata da visa, da na sani lokacin da muka je renewal kema na nema miki."

Murmushi tayi ta ce "Nanna kada ki damu,tunda za ki da Tarantula ai sammakal."

Dariya Jamal ya kwashe da ita ganin Haj. Manga ta zaro idanu tana hararsa.

"Kanwata bani da ta biyunki. Ashe kina gane yaren."

Kunnuwansu ta kama tana ja "don kaniyarka bata min yarinya za ka yi? Ke kuma kiyi ta makale masa ke mai dan uwa. Na sake jin kuna min yaren 'yan kwaya sai na gwara kawunanku."

Tana fada suna hada ido suna dariya. Tun tana masifa ta koma dariyar ita ma.

Kwana biyu a tsakani suka kaisu airport. Ta sha kukanta kuwa saboda zaman kadaici da zata yi. Madam Zainaba tun jiya ta tafi garinsu za ta kwana biyu sai ana gobe zasu dawo ita ma ta dawo. A hanya Papa Abayomi yake fada mata cewa gobe ta hada kaya zai kaita Gombe suyi zumunci da tsofaffin makotansu. Ya riga ya baiwa Shaheed hakuri akan uzurin rashin lafiya da ya tasowa Baffa. Kuma Alh. Audi zai je daga Japan sannan Fanna da bata gajiya da yawo ita ma za ta je. Baccin da Tauhidat tayi a hanya ne ya bashi damar cigaba da tunanin yadda Alh. Audi ya mayar da Shaheed jikinsa sosai.

Yana yawan kai masa ziyara gashi wai ya biya masa ya dora Masters kafin ya dawo gabadaya. Hutu kawai zai zo idan an fara karatu ya koma. A bangare guda Haj. Manga ta tsare kofar bar masa 'ya tayi maraicin mahaifiyarta. Zuciyarsa ta kan raunana da tunanin kada wani abu ya bullo nan gaba da zai sanya shi zama maci amana ga wadannan mutane. Yadda suka dauke shi da zuciya daya haka yake fatan su rabu cikin aminci.

***

Daga uhm sai uhm-uhm Haj. Manga take iya yi a jirgi idan Jamal ya sako mata hira. Hankalinta kamar ba ya jikinta sai hasashen yadda za ta ga Arqam take yi. Gajiya ya yi da hirar ya kunna TV din gabansa yana kallo har bacci ya kwashe shi.

Tun safe Arqam yasa housekeeper dinsa Mrs Brown ta gyara ko'ina na gidan. Dakuna biyu ne ya siyo sababbin bedsheets da kayan bukata na mata ta jerawa Haj. Manga a daki daya. Dakinsa kuma sai su kwana da Jamal tunda su Baffa suna hotel. Abu Usama da mutane da yawa na masallacinsu sun san mahaifiyarsa za ta zo yau. Sauran basu san me yake faruwa ba amma duk da haka suna taya shi murna saboda tsananin farincikin da ya kasa boyewa. Abinci kala biyar ya ce Ruksana ta dafa saboda bai san wanda zasu so ba. Abin mamaki ga shugabansu a asibiti da kansa ya nemi hutun sati guda. Babu bata lokaci aka bashi. Kowa yafi jindadin mu'amala da wannan Arqam din mai yawan fara'a da jan mutane da wasa.

Jirgin nasu sai biyar na yamma zai sauka amma a airport din hudu ta riski Arqam. Awannin da zaman ko kadan basu dame shi ba. Shi kadai ya zo don su Baffa sun ce ba da su ba wannan zama. A gidansa ya baro su ya taho a hadaddiyar motarsa kirar chrysler convertible ruwan toka. Wurin parking ya nema a hawa na biyar ya ajiye motar. Sai da ya dan jira mutanen da suke wurin da za a iya ganinsa sun ajiye ko kwashe ababen hawansu ya fito. Sanye yake da bakin jeans da bakar turtle-neck top wadda ta kama shi, ya yi zanzaro da ita. Ya dora sky blue din blazer. Kansa a saisaye ya rage gashin fuskarsa. Ba karamin kyau ya yi ba musamman da ya dora gilashin ido kalar blazer din wato sky blue ya rufe idanuwansa.

Kallo daya ya ishi duk wanda ya san kungiyar 3ripleA ya gane mawakin cikinsu Arqam. Wata magazine ya samu ya kare fuskarsa lokacin da ya shiga lift. Ya zo fita a inda zai jira isowarsu wata ta bangaje shi da gangan. Magazine din ta fadi

ya bita da sauri, kafin ya dauko yaji an rungume shi. Ihu matan wurin suka saka manya da yara. Concerts din da yake zuwa mata na suma yau gasu ga shi. Wurin nan da nan ya cika da dandazon mutane masoyansa ana ta kiran sunansa da daukar hotuna. Duk wanda ya amsawa musabaha kuwa ya mika nasa hannun sai ya yi da gaske suke saki. Security ne suka bambare mutane daga jikinsa ya samu ya sulale. Wani office aka kai shi na VIP ya zauna. A nan din ma bai tsira da signing autograph ba. Kamar wanda yake kan kaya biyar na yi ya tashi ya ce wadanda yake jira sun sauka. Ba a barshi ya fita shi kadai sai da aka hada shi da security biyu hagu da damansa. Saboda matsayinsa a garesu da son takaita hayaniyar da kasancewarsa a wurin ta kawo aka kai shi daidai wurin fitowarsu. Yana kallo security din ya radawa wani maaikacin kamfanin jirgin da suka biyo wata magana. Bai san me suka ce ba sai ga mutumin ya zo gabansa yana murmushi ya tambayeshi sunayen wadanda yake jira.

Ya fada da minti goma aka bude jirgin dake jone da jikin ginin airport din ta yadda mai fitowa ko shiga ba zai ga jikin jirgin ba. Haj. Manga da Jamal na zaune suka ji sanarwar ana kiransu su. Ai sai suka tsure gabadaya har tana yiwa Jamal fadan ko ya hado da kwayoyinsa a cikin kaya. Gani suka yi a mutumce an zo an karbi kayansu su suka fara fita daga jirgin. Arqam yana tsaye ya zura hannuwa a aljihu a daidai inda zasu ganshi idan sun gangaro.

Zazzafar kwalla ce ta cika musu idanu duka su ukun a lokacin da idanuwansu suka hadu da juna tun kafin su iso inda yake. Mahaifiyarsa sanye da navy blue din laffaya mai rangwamen ado ya fara kallo sannan ya kalli rabin jikinsa Jamaluddeen. Kasa tsayuwa yayi kamar yadda Jamal din shi ma ya debo a guje tare da riko hannun Nanna don ta kara sauri. A tsakiyar wurin suka hadu kwallar idanuwansu duka ta fara wanke musu fuskoki.

A tsorace Arqam ya mika hannuwansa garesu. Jamal ya rike daya Haj. Manga ta rike daya. Wata irin ajiyar zuciya ya saki domin ya tabbatar da gaske ba mafarki yake yi ba. Duka su biyun ya keresu a tsayi. Haka ya rungumesu da iyakar karfinsa su ma suka kankame shi kamar za a rabasu. Kuka suke yi sosai babu mai bawa dan uwansa hakuri. Kafadarsa aka taba ya juya wurin daya daga cikin securities din. Inkiya aka yi masa da

cewa su bar wurin saboda an fara fitowa. Tsayar dasu ya yi ya dauko trolley ya dora kayansu.

Wanda aka yi checking-in Jamal ya tafi daukowa ya barsu su biyu a wurin.

Haj. Manga da take jin kanta kamar a gajimare ta daga hannuwa ta rike fuskar Arqam a tafin hannunta.

Cire hannuwan ya yi ya sumbaci tsakiyarsu sannan ya dago da sababbin kwallarsa "Nanna ki kira sunana please."

Hawaye ya goge mata da yatsansa tana masa murmushi ta ce "Arqam yaron Abba."

Sake rungumeta ya yi yana jin jikinsa gabadaya tamkar ana warware masa wasu igiyoyi da suka yi masa dabaibayi. A haka Jamal ya samesu suka kama hanyar wurin parking din karkashin jagorancinsa.

Mutane ne jingim a wurin suna jiran fitowarsa. Haj Manga da Jamal sai mamakin yadda ake ihu a kansa da yadda securities suka wahala kafin su sama musu hanya suka shiga ya tayar.

"Yayana celebrity ne ga dukkan alamu. Ka shiga hollywood ne?" Cewar Jamal abin yana kara burge shi.

"Nope" ya ce da murmushi.

Haj. Manga ta girgiza kai na rashin yarda "Anya Arqam? Ji fa yadda wata ta kusa shidewa da ihun ganinka."

"Haduwa ce kawai suka gani tsagwaronta ko Bros?" Jamal ya ce yana leko da kansa gaba tsakaninsu.

"ActualIy I used to be a singer amma yanzu na dena."

Idanun Haj. Manga kamar su fito "Waka Arqam? Wace iri? Irin wadda 'yan mata ke yanyameku kamar kyankyasai?"

Dariya suka yi shi da Jamal ya roketa da ta bari su isa gida. Tafiyar minti arba'in da biyar ta kaisu gidan nasa. Abu Usama da matarsa da dansu suna gidan ta jera komai akan dinning table ana jiran isowarsu. Tarba mai kyau ta yiwa Haj. Manga kamar sun dade da sanin juna. Irin gaisuwarsu ta rungume mutum a sumbaci kumatu hagu da dama tayi mata. Kayansu Arqam ya kai daki tunda duka yunwa suke ji suka zazzauna kewaye da table din.

Arqam ya sake gabatar da Abu Usama, Usama da Ruksana ga iyayensa. Da turanci suke maganar yadda kowa zai fahimta.

"Abu Usama ya taimaka min sosai a lokacin da rayuwata take cikin mawuyacin hali. Na daukesu tamkar jinina saboda sun cetoni daga mummunar rayuwa."

Baffa ya gyara zama ya kalli kowa a wurin da murmushi "Duk wanda ya taba taimaka maka ko na rana daya ne Arqam ya cancanci mutumtawa da karramawa daga garemu. Ni da 'ya'yana da jikokina muna farincikin samunku cikin ahalinmu."

Abu Usama hannu ya sake mika musu suka gaisa. Ruksana kuwa hawayen dadi take yi saboda yadda fuskar Arqam ta cika da annurin kasancewa wuri guda da iyalinsa.

Suna gama cin abinci Haj. Manga ta ce za ta yi wanka. Arqam ya kaita dakin da ya tanadar mata ya sami wuri ya zauna.

"To fita mana in shiga wankan ko."

"Zan jira ki Nanna. Ban gaji da kallonki ba." Ya kashingide akan gadon.

"Yi hakuri nima ba gajiya nayi ba. Ina shiryawa zan fito."

Tana fama dashi sai ga Jamal. Da zuwansa tsalle ya daka ya fada kan gadon.

"Don Allah ku fita jikina har kaikayi yake min."

Babu wanda ya motsa. Idanu suka zuba mata tana ta fada suna dariya. Gani tayi abin nasu harda zolaya ta dauki tawul ta bude kofar bandakin za ta shiga Arqam ya ce, "Nanna ina Tauhida? I was hoping to meet her."

"Zo muje na nuna maka hotonta." Cewar Jamal yana jan hannun yayansa.

"Hamdan, katheeran, dayyiban, mubarakan fihi. Allah Ka cancanci kadaita da bauta Ya Zhuljalali wal Ikhram" Haj. Manga ta fadi ta kai sujjada ga Sarkin Sarakuna tana mika godiyarta da ya nuna mata wannan rana.

Laptop Jamal ya dauko daga jakarsa ya kunna ya bude wata folder da ya sakawa sunan Tauhidat saboda hotunanta ne a ciki. Wanka ya shige bayan ya tura laptop din gaban Arqam.

Zama ya yi ya tankwashe kafarsa daya akan gadon dayar kuma tana kasa ya bude hoton farko. Tana tsaye a jikin mota ita da Papa Abayomi zai kaita makaranta aka dauka. Murmushin nan da baya rabo da fuskarta take yi wanda ya bayyana siririyar wushiryarta. Kasa yin gaba ya yi yana ta kallon kyakkyawar fuskarta. Hoto na gaba da ya danna sai da zuciyarsa ta tsaya cak na wucin gadi. Tsigar jikinsa ce ta tashi lokaci guda. A tsaye take a bayan Nanna ita kuma tana zaune. Tauhidat ta zuro hannuwanta ta wuyanta ta dan kwanto tana dariya.

"Breath taking..." ya ce kamar wanda ya kai tsere saboda irin bugun zuciyarsa. Ba wai kyau tafi kowa ba amma ya rasa me ya taba shi tun ranar da yaji muryarta. Washegari da ya kira Haj. Manga sai da ya nemeta suka gaisa. Yau kuma daga ganin hoto tana neman kurdawa inda bai sani ba a cikin jinin jikinsa. Gaba ya yi da sauri amma bai tsira ba. Duka hotunan fuskarta a sake kamar gonar auduga. A wurin Jamal ya fito ya same shi.

Bai san muryarsa ta shake ba can kasa ya tambaye shi meya sa basu zo tare ba. Kafin ya bada amsa Haj. Manga ta kwankwasa musu kofar ta shigo. Ko zama bata yi ba ta hango hoton da yake kallo.

"Ka ga Tauhidan Nanna ko Arqam? Yarinyar nan ta rage min kewarka fiye da zato."

Jamal ya ce "To dai kada kiyi mana kuka." Ya juya yana kallon Arqam "in fada maka ko kai da ake ta nemanka baka kai Tauhida matsayi ba fa. Ita ce number one a zuciyar Nanna."

"Na bar mata indai ba kai tafi so ba." Cewar Arqam yana murmushi.

Zama tayi ta fada masa yadda ta hadu da Tauhidat ta kare da cewa "a matsayin 'ya na dauketa kuma Jamal yana mutunta min ita kamar jininsa. Don Allah kaima kada kayi mata wani abu na kaskanci saboda tana 'yar direba. Na dade da son ya bar aikin amma yaki. Ni kuma ina tsoron matsa masa ya ce da ita zai tafi."

"Jamal da gaske ta fi sonta. After all these years baki tambayeni komai ba sai hirar Tauhida" Arqam ya ce yana sake kallon hotonta.

Dariya suka yi sannan aka koma falo inda aka baje kolin hirar yaushe gamo. Abu Usama da iyalinsa sun tafi. Haji Lawalli ma sai ya fake da gajiya ya gudu hotel dinsu ya bar iyalin su kebe.

Arqam bai boye musu komai ba na rayuwarsa tun ranar da ya baro England. Haj. Manga tun tana kuka sai ta koma gyada kai kawai. Babu abinda yafi bata tausayi kamar irin rayuwar da ya yi ta kunci kamar mara gata. Batun waka kuma tunda ya ce ya dena taji dadi sosai. Sana'a irin wannan a kasar da addini ba shi da mahimmanci sai wanda Allah Ya tseratar. Rayuwa ce bahaguwa mara alkibla akeyi. Babban abinda ya tayar mata da hankali kuwa bai wuce sunan Madam Zainaba da ya ambata a matsayin mai daukar wayarsa ba.

Rike baki tayi cike da matukar mamaki tana kuka "Baffa ka ji abinda yake cewa? Zainaba fa..." kasa karasawa tayi saboda ranta ya kai kololuwar baci da wannan cin amana. Lallai Alh. Audi ya nuna mata har yanzu bata kama kafar yakarsa ba. Shekara da shekaru tana tafin hannunsa a dalilin Madam Zainaba bata sani ba. Wannan abu ya yi mata mugun ciwon da ya sanyata tafiya daki ba shiri ta banko kofar. Allah Sarki rashin sani...

Jiki a sanyaye su ma suka shiga daki. Dare ya yi sosai saboda haka Arqam sai ya barwa Jamal da Baffa dakinsa shi kuma ya dawo falo. Da suka damu da ya dawo dakin ko a kasa Jamal sai ya yi shimfida sai ya ce shi karamin sauti ke tada shi bacci. Bai dade da kwanciya ba akan doguwar kujera Haj. Manga ta fito ta ganshi. Ta riga ta yanke hukuncin yadda zata yi da Madam Zainaba shi ya sa ta saki ranta. Akanta ba za ta kuntatawa zuciyarta a lokacin farincikinta ba.

"Kana nan da rashin son kwana da mutane ko?"

Dago kansa ya yi daga kan throw pillow din kujerar yana sosa keya "I don't feel comfortable (takura nake yi)."

Zama ta yi a wata kujerar suka dasa hira. Idonta ya soye saboda bambancin lokaci. Ba su suka kwanta ba sai bayan sunyi sallar asuba.

Daga ranar aka ajiye kuka da bakinciki suka sake suna jindadin kasancewa da juna. Kullum sai Arqam ya kaisu yawo. Aminansa Tomaz da Josh sun zo har gida gaishe da iyayensa. Jamal ya sha mamaki harda sakin baki da ya ga video din wata waka da yake yawan sauraro a gida ashe su suka yi. Nan fa ya makalewa su Josh. Barkwancinsa yasa suka saba cikin kankanin lokaci. Bayan sati daya Arqam ya koma aiki. Amma yana dawowa gida zai tare a wurin mahaifiyarsa.

Yau kwanansu goma kuma suna shirin tafiya idan sun cika sati uku. Tafiyar tasu dole ce saboda wata shari'a da dole Baffa ne zai yi zaman karshe da mutanen ya yanke hukunci. Babu dalilin ace wanda tazo jinya ya koma gida ita tana nan sai zargi ya shigo tsakani. Arqam tun yanzu ya fara damunta kuwa akan yadda zai cigaba da rayuwa idan sun koma.

"Nan da wata biyu in sha Allahu zan dawo. Ka kara hakuri har mu san abinda ya kamata muyi. Nima ina son kaje gida ko don Dada."

Suna wannan hirar waya da shigo mata da sunan Haj. Lami. Murmushi ta doka saboda tun dazu take kira yau bata ji muryar Tauhidat ba. Kememe taki yarda idan sun je Gomben ta kwana a gidan abokin babanta makocinsu. Bata son 'yarta ta takura. Haj. Lami ma tana shan kashedi akan a kula da abincin da za a bata. Ita dai dariya take yi akan wannan uwa da 'yar.

Sai da suka gama gaisawa Haj. Lami ta tambayi jikin Baffa sannan ta soma tsokanarta akan Tauhidat kafin ta bata. Arqam dake gefe yana ji ta soma hira da ita ya kwabe mata fuska tare da tara hannuwa kamar mai roko.

Dariya ma ya bata kamar wani dan almajiri ta mika masa. Yana karba ya zame daga zaune ya kashingide akan kujera ya saka speaker. Kai tsaye sai cewa ya yi, "Nayi miki laifi ne you don't even ask for me (ba kya nema na)."

Da muryarsa ta gane shi duk da sau daya ta taba ji. Murmushi Tauhidat ta sami kanta da yi. "Laahhh, Dayan kayi hakuri. Ina cewa Nanna da Jamal su gaisheka."

"Meyasa ba za ki gaisa dani ba sai sako? Bana so."

"Kayi hakuri" Tauhidat ta ce a sanyaye.

Haj. Manga kuwa dukan kafadarsa tayi ta mika hannu "kai bani wayata. Ya za ka tsare min yarinya da rigima saboda ka dawo gida a gajiye? Rabu dashi kinji ko."

Sai da ya matsa can gefe rike da wayar ya ce "nima ki dinga kirana. I am your brother too. Zan karbi number dinki wurin Nanna."

"Ai bani da waya, ka bari ta dawo sai na dinga kira da wayarta har sai ka gaji."

"Seriously? Nanna wai bata da waya?" Kai ta gyada masa tana cewa sai ta kare secondary ya ce da Tauhidat "I'll send one for you with Jamal okay? (Zan bawa Jamal ya kawo miki guda kinji.)"

Ba wai turancin bane Tauhidat bata ji sai dai accent dinsa (fitar sauti) ya bambanta da irin turancin da ta iya. Ko kadan bata gane me ya ce a karshen maganar ba. Kasa tayi da murya "ko me ya ce?" Sai kuma ta daga muryar yadda zai ji ta ce "uhmm" alamun bata ji me ya ce ba.

Haj. Manga ta tuntsire da dariya "kana magana da hanci yaushe za ta gane? Muma nan wahalar damu kake yi. Hausa da turancin duka da hanci suke fita."

Dariyar Tauhidat ya ji ya bata fuska ya ce "me nayi?"

"Tauhidat wai waya zai saya miki." Cewar Haj. Manga.

"Ba kin ce sai..."

"Kada ki ki karba ai yayanki ne. Kai kuma bani wayar kayi naka wuri."

Sosai ya hade rai "ni ban gama ba."

Murmushi tayi tana jindadin yadda yake nuna damuwarsa akan kanwar tasu tun kafin su hadu. A haka aka kare hirar su uku. Tauhidat ta sake sosai saboda tana jin muryar Nanna. Shi kuma Arqam yadda suke hirar ne yake burge shi. Haka kawai yake son muryarta...da fuskarta.

Laifin dadi karewa. Kamar kifta ido da budewa haka sati uku suka wuce. Arqam tun asuba ya koma dakin Haj. Manga ya hanata komawa bacci. Gani yake kamar idan sun tafi shikenan zai koma gidan jiya. Da wannan tunanin yake kwana yake tashi. Tayi iya bakin kokarinta wurin kwantar masa da hankali

da alkawarin ba za ta dauki lokaci ba zata dawo amma jikinsa ya yi matukar sanyi. Kansa ya dora akan cinyarta tana jin saukar hawayensa akan rigarta. Namijin kokari tayi bata son ta karasa karyar masa da zuciya ta hadiye nata kukan.

"Kada ki manta da yi min addu'a kullum."

"Wannan dole ne, kana kasar nan da ba mafadi ga Kawunku Audi ai dole na zage dage."

Dago kai ya yi ya kalleta "Nanna me ki ke gani reason dinsa na yi min haka? Its not like muna neman wani abu a wurinsa" sannan ya kara da cewa "Idan kin koma ki kashe auren fa."

Sama ta kalla tana kokarin mayar da kwallarta "ban sani ba Arqam, deep down ina ji a raina kamar akwai wani abu tsakaninmu dashi da bamu sani ba. Kaina a kulle yake. Dubi dai yadda ya lalata min yaro. Haji Lawalli ya ce Tony da bakinsa ya fada masa shi ya sa shi koyawa Jamal shaye-shaye. Zuwanmu nan ne ya hana shi yi saboda ganin ido. Amma kaninka ko kashin awaki aka ce zai bugar dashi fes zai tura a baki."

Wani dadin abin haushin kuma da yake damunsu shi ne ganin ko kadan Jamal yaki yarda da cewa Alh. Audi baya son su. Jiya kamar ta doke shi da safe har ya yi fushi.

Sai da suka yi la'asar a gida sannan suka kama hanyar airport. Abu Usama da iyalinsa sun zo sunyi musu sallama aka rabu ana kewar juna. Bayan sun isa an gama duba kayansu Arqam ya shiga mugun tashin hankali. Yau da yake ya saka hula ya kuma rufe rabin fuskarsa ya tsira daga mutane kuma ya sami damar kukansa na zuci da na zahiri a boye. Rabuwa ce mara dadi cike da tsoro da fargabar ko za'a sake haduwa. Duk wanda ya ga yanayinsu dukkansu sai sun bashi matukar tausayi. Tsayuwa ya yi yana daga musu hannu har suka bacewa ganinsa.

***

Kauyen Dakasoye

Mace ce durkushe a gaban murhu tana ta hurawa da baki da kasan zaninta amma wutar taki kamawa sai uban hayaki. Dududu ba ta haure shekaru ashirin da biyar amma wahala ta yankwaneta tamkar wadda ta baiwa arba'in baya. Dago kai tayi idanu jajir hanci na yoyon tsinkakkiyar majinar wahala ta kira

kaninta dake yashe akan wata guntuwar ragowar tabarmar kaba.

"Mammalo agaza min da kirare ko na samu wutar nan ta kama mana." Ta ce tana mikewa tsaye da kyar. Siririya ce sosai ga rashin tsayi tana sanye da dankwali da zanin atampa daban daban da tayi daurin kirji dashi. Hakan shi ya kara bayyana tudun cikin jikinta da ya kusa cika watannin haihuwa.

Yaron da ta kira Mammalo shi ma babu jikin. Zafi ya ishe shi daga shi sai dan buje yake kwance. Cikinsa a dame kamar zai hade da bayansa saboda tsabar yunwa. Bata fuska ya yi ya soma magana da kunkunin da ba ta iya jiyowa.

"Dan gwafar ubanka baka ji ni bane? Idan wutar ta kama na dafa waken ba har da kai za a ci ba?"

Dogon numfashi ya ja sannan ya tashi zaune yana numfarfashi "ke kuwa Yaya Uwani babu lamuni cikin lamuranki, banda rashin tausayi ina ni ina neman kirare yanzu?"

Waken da ta zuba a tukunya ta kamfato a tafin hannunta ta watsa masa "sai ka ci a haka tunda ba za ka iya fita ba."

Tausayinta ya ji ya mike ba don yaso ba ko riga bai saka ba ya fita. Cikin kankanin lokaci ya hado kananun itatuwa ya kawo. Da kyar Yaya Uwani ta samu wutar ta kama ta dafa musu waken da aka basu zakka daga gidan Sarkin noma. Man kwanturola ta diga musu a kai ita da kanin nata da guntun gishiri suka hau ci hannu baka hannu kwarya. Wata muguwar gyatsa Mammalo ya saki bayan ya gama kora waken da ruwan da ya sha daga wata tsohuwar buta.

"Alherin Allah Ya kaiwa Sarkin noma da iyalinsa. Rabo kuma Allah...."

Hannu ta dago masa da sauri "to mara mutumci za ka fara diban albarkar ne saboda ka koshi ko?"

Dariya ya yi kamaninsa da ita na kara bayyana. Dan jikinsu iri daya. Bakake, sirara marasa tsaho.

"Diban albarka ko fadin gaskiya? Yasin kwana biyun nan da babu abin dorawa a gidan nan na galabaita. Ko kinsan ko ga'idi ba na iyawa idan naje tsuguno? Haka zan gama nishi na tashi. Babu komai a cikin to me zan fitar? Tusa wannan hegiya

haka nake fitar da sautuka kamar busa sarewa amma babu hamami don bala'i."

Harara ta maka masa duk da ta san gaskiya ce yake fada "idan ba ka iya zaman gidana ai muna da yawa yayun naka. Ka koma gidan masu arziki inda ba'a kwanan yunwa."

Ba nufinsa ya bata mata rai ba. Duniya kaf yanzu ba shi da kamarta. Sauran 'yan uwansu suna gudun ya zauna musu a gida saboda kiriniya da daukar magana. Uwani kuwa da suke sakwanni dashi ta ce taji ta gani. Innarsu ta so autanta don bata raye bai kamata zumunci ya yanke ya rasa wurin zuwa ba. Matsalarta guda a gidan aurenta, mugun talaucin da ya yiwa maigidanta kawanya. Da babu ta addabe shi ya sayar da kazarsa ya je gidan wani Malami neman sa'ar arziki. Malami ya dafe 'yan canjin ya ce masa iyalinsa ce mai farar kafa sannan ya hada masa da wuridin arziki. Rabo na jin haka bai kara sati ba ya dankara mata saki ya kuma tattara komatsansa ya bar garin. Gidan ma bar mata ya yi tunda yana hasko arzikinsa. Wuyarta dai ya yi nesa da ita ya sami damar yin wuridinsa. Idan arziki ya zo sai kowa ya yi mamakinsa.

Daga ita sai kaninta a gidan, sai kuma cikin da ya bayyana bayan tafiyar Rabo. Su kam sun wuce ajin talauci sai fatara. Basu da komai sai abinda Allah Ya hore musu a rana. Tun suna yawon zuwa gidajen 'yan uwa da tsakar rana daidai lokacin cin dumame har dai gori ya hanasu fita. Uwani akwai bakar zuciya. Habaicin 'yan uwanta ya sanya ta dena zuwa duk da yunwar dake sasakarsu. Mammalo kuma dama malalaci ne. Bai iya komai ba sai yawon gidan kallo. Ya dane bishiyar darbejiyar wajen wurin yana kallo a bagas. Shekarunsa ashirin da biyu. Yana son yayarsa kamar rai duk da fada suke kullum kwanan duniya.

Hakuri ya bata ta kuwa sauko tunda tsakaninsu ba ta baci. Sako mata zancen tafiyarsa birni ya yi a karo na biyar cikin satin nan ta kuwa sake hade fuskar nan kamar bata taba dariya ba.

"Yadda Rabo ya guji mai farar kafa kaima guduna za kai ko?"

Kwantar da murya ya yi kamar jikan maroka ya soma magiya da ban baki yana nuna mata alfanun tafiyar.

"Ni fa na gama tsara komai. Gidan kallon nan da nake zuwa ba banza ba. Kamar yadda na gani a wani fin nima ina zuwa zan sami arniyar motar gidan masu kudi ta bige ni."

Da sauri ta dafe kirji jin wannan rashin hankali "idan ka mutu fa?"

"Za su biya diyya sai ki rike duka ki kula da kan ki da jaririn da za ki haifa. Ko kwandala ki ka baiwa wani cikin su Yaya Talle Al-Qur'an ban yafe ba kuma sai nayi muku fatalwa."

"Ba ka da hankali. Idan kuma ka hada da 'yan yankan kai fa?"

"Kurwata kur...ke da nake miki bayanin masu kudi zasu bigeni. Daga nan muje gidan sai 'yarsu ta makale min, a kai ruwa rana karshe ayi aurenmu ni da ke mu wataya me ya kawu zancen 'yan yankan kai kuma?"

Dariya ya bata kuwa "ashe harda aure, eh lallai. Har an daura ma ta tare. Mammalo mijin Hajiya ranka ya dade."

Bai ji haushi ba ya cigaba da bayanin yadda zai je birni neman auren 'yar masu kudi. Ya tabbatar kyaunsa kadai ya isa ya janyo masa soyayyar yarinyar ko 'yar waye. Kuma a shirye yake da ya jure duk wani wulakancin mahaifinta a dalilin talaucinsa kafin karfin soyayyar tasu ya sa a bashi ita. Tashin farko gida zai dankawarawa Yaya Uwani. Ya wadata ta da abinci ita ma ta dinga bayar da zakka duk shekara. Abinda za ta haifa kuma zai kaiwa matarsa har ma ya ja mata kunne cewa idan ta wulakanta jinin Yaya Uwani ta wulakanta igiyar aurenta ne. Wata irin zabura da tsallen murna ya yi bayan ya gama shirya komai a cikin kwanyarsa.

Abu kamar wasa karamar magana ta zama babba. Cikin wata guda sai da abokan huldar Mammalo suka san zai je birni. Karya ya shata musu wai ya sami aiki ne a birnin tarayya Kaduna. Wadanda suka san karya ne suyi ta dariya suna zuga shi. Bayan 'yan kwanaki kawai ya hada 'yan kayansa ya yiwa Yaya Uwani sallama. Ranar tayi kuka tayi roko harda fada amma ya dage cewa shi fa zuciyarsa tana bashi lallai da arzikinsa zai dawo kauyen nan. Babu irin fadi tashin da bata yi ba wurin hana shi amma ya tubure. Babban yayansu ya ce a barshi ya tafi ai bari ba shegiya bace da ubanta. Idan ya kwana biyu kacal a birnin da kafarsa zai dawo gida. Tana ji tana gani abokan arziki masu jindadin shaftarsa suka hada masa kudin mota ya samfe...

***

Ana sauran kwana biyu su Haj. Manga su dawo Abayomi da Tauhidat suka dawo Abuja. Madam Zainaba tana garinsu babu lafiya. Ashe tana da ciwon suga sai yanzu aka gane. Ga damuwar rashin waya daga uwardakinta ta saka a rai. A zatonta jikin Baffan ne ya yi tsanani tunda bata fada mata gaskiya ba kafin tafiyar. Sun saba duk inda ta je tana kiranta ta bata lambar wayarta. Jikinta har lokacin babu kwari shi ya sa danta ya ce ta zauna idan sun dawo zai kira ta ya sanar da ita.

Bayan dawowarsu Tauhidat washegari ta gyara dakin Haj. Manga da nata. Babu inda bata share ta goge ba. Tun daga falo har dakunan da bandakunan biyu. Abinka da dakin mutanen Maiduguri ba sa rabo da kamshin turaren wuta. Na safe daban na yamma daban. Su kansu uwa da 'yar sassanyan kamshi ya ratsa jikinsu. Tauhidat kam sai dai a kirata babarbariyar bayerabiya kuma bahaushiya a baki domin yaren gidan kenan. Da wuya ka ji Haj. Manga na magana da yarenta indai ba da Baffa ba. Jamal ba wani iyawa ya yi ba bare kuma Arqam da ya dade ba ya nan.

Karfe bakwai suke sa ran saukar jirgin kamar yadda ta sanar da Papa Abayomi a waya. Shida da rabi suna airport shi da Tauhidat a cikin sabuwar motar Haj. Manga Element. Basu wani jima ba kuwa suka sauka. Jamal ta fara hangowa ya taho a guje harda bude hannuwa.

"Oyoyo Tauhidat.." ya tafi kamar zai rungumeta Haj. Manga ta janyo kwalar rigarsa ta baya. Dariya ya saka yana kyakyatawa saboda yadda ta hade girar sama da kasa tana fada.

"Kwana biyu mun yi missing wannan Nannan ko?" Ya tambayi Tauhidat dake taya shi dariyar.

Girgiza kai tayi ta kama kunnuwansu tana cewa suna son mayar da ita kakarsu ta karfi da yaji. Baffa yana kallon yadda take fadan amma kana ganinta ka san cewa tana tattare da babban farinciki. Shi da su Papa Abayomi duka murmushi suke yi lokacin da take korafin wai Tauhidat tayi duhu kuma ta fada. Ba za ta kara turata Gombe ba tunda babu kulawa yadda ta dace.

Mota suka nufa Tauhidat ta daukar mata jakar hannunta sauran akwatunan kuma ana tura musu. Baffa motar Haji. Lawalli ya bi washegari zai wuce Maiduguri. Tun a gidan

Arqam ya riga ya baiwa Haj. Manga takardun da za ta karbi kudadenta dasu.

Anzo shiga mota tunda Jamal ya kyalla ido ya ga wadda aka zo da ita ya shiga rokon a bashi ya tuka. Magiya yake yi Tauhidat na taya shi Haj. Manga ta ce basu isa ba. Tunda bai gaji ba idan sun isa gida ya dauki tasa motar ya wuce Adamawa amma ba ta ta ba. Basu fasa rokon ba har Papa Abayomi ya taya su cewa a bashi dani. Ashe kaddara ke kiransu.

Ranar kwanan Mammalo daya a tasha ya rasa inda zai sa ransa yaji dadi. Shi dai ya fadawa direban motar da ya biyo cewa birnin tarayya zai je. Direba kuwa ya caje shi kudin zuwa Abuja. Duk lissafinsa Kaduna zasu je domin nan ne yaji ana cewa garin Gwamna. Sai ya zata nan din ne birnin tarayya. Da isarsu kowa ya sauka Mammalo ya shiga raba idanu ga yunwa. Kure aljihunsa ya yi ya sayi kosan hamsin aka zubo masa su a leda kamar ya hada ya tura duka lokaci guda. Ya ga tashin hankali muraran domin a iya saninsa kosan hamsin a garinsu duk yunwar cikinsa ya yi masa yawa. Tijara ya hau Mai kosan da ita ya ce ko ta kara masa ko a bashi kudinsa.

"Wake abin banza shi ne za ki zuba min wannan abu kamar za a baiwa dan yaye? Ni da Yaya Uwani dan talatin muke ci mu gyatse a garinmu"

"Nan Abuja ne ba garinku ba" wani a kusa ya bashi amsa.

Ita kuwa Mai kosan harara ta doka masa ta cigaba da juya wanda yake cikin mai. Mammalo ya kara harzuka kuwa yana ganin kamar rainin wayon 'yan birni ake neman yi masa. Wanda ta soma kwashewa ya dumbuza a hannu ga zafi ya kwasa a guje. Bai je ko ina ba wasu karti suka damko wuyansa. Nan aka nada masa na jaki ana kiransa barawo. Abu dau baiyi dadi ba. Da tsattsaman jiki ya kwana akan wani benci a tashar ga yunwa kamar ya ci babu.

Tunda garin Allah ya waye ya koma bakin titi yana jiran motar masu kudi tazo ta bige shi ko ya samu su daidaita da budurwar da wuri ya koma wurin Yaya Uwani. Da yake da wayonsa ya kula motocin nan sharo gudu suke yi, idan ya yi gangancin hawa titi mitstsike shi zasu yi tas a kasa gane shi a kan kwalta. Tafiya mai dan nisa ya yi zuwa bakin junction inda ya kula da mai bada hannu ga kuma wata fitila mai canja kala. Gaban motoci biyar ya sha daga safe zuwa yanzu amma duka bai ga

alamun nasara ba. Na farko fitowa ya yi ya zabga masa mari yana ta magana da yaren da bai ganewa. Na biyu sai da yellow fifa ya sa baki har aka ce ana kallon lokacin da ya kwanta a gaban motar don ya kulla musu sharri. Wahala idan ta auri mutum sai hakuri.

Isha ta kawo kai yanzu babu wata alamar sa'a a tare da shi. Hanyar tashar ya soma nema ya koma amma ya kasa ganewa. Kamar da wasa ya dan juya gefen titin kuwa ya hango wata bakar mota mai masifar kyau tana tahowa. Hasken fitilun titin sun sake kawata ta tana ta kyalli. Babu mai bada hannu yanzu kuma dai ba sanin kan fitilar nan mai canja kala ya yi ba. Haka ya yi shahadar kuda ya jefa kansa a tsakar titi daidai lokacin da Jamal ya taka wani mahaukacin burki. Haj. Manga da Tauhidat sai salati don sun saddakar ko waye an gama taka shi. Jikin Jamal na rawa Papa Abayomi ya fita da sauri. Mota dai bata taba Mammalo ba sai firgitar da ya yi. Ganin babban mutum a kansa sai ya ji tsoron kada a maimaita irin na dazu a mare shi. Tashi ya yi zai bar wurin salin alin sai ga Haj. Manga da Tauhidat sun fito daga motar suna tambayar ko yaji ciwo. Ai yana kyalla idanu akan Tauhidat sai ga shi ya fadi wanwar a kasa yana kiran bayansa ya karye tare da kifta mata idanu yana mata kallon notice me.

Haj. Manga ta soma yiwa Jamal fada shi kuwa duk ya rude yana tsoron ko da gaske ya ji masa ciwo sai ga wasu masu cin kasuwar bakin danja. Wani cikinsu ne ya gane Mammalo ya tona masa asiri cewa tun dazu yake shan gaban motoci. Suka tarar masa don son burge Hajiya mai alamun naira a jikinta ai kuwa sai gashi ya mike garau. Wannan abu ya batawa Haj. Manga rai kuwa.

"Idan kudi kake so ka nemi aiki mana. Kai ko bara ai ta fiye maka da wannan gangancin da kake da rayuwarka."

Idanu akan Tauhidat har lokacin Mammalo ya shiga bata hakuri tunda ya ji ance a kira 'yan sanda su tafi dashi.

"Ka wuce ka koma gida zaman yaro kamarka a nan da wannan sana'ar babu abinda zai ja maka sai wahala" cewar Papa Abayomi.

"Kwarankwatsa bani da wurin zuwa a garin nan. Birnin tarayya na ce a kaini can Kaduna shi ne aka kawoni nan. Aiki nazo nema in sami kudi in koma wurin Yaya Uwani."

Haj. Manga tace "daga ina kake?"

"Dakasoye, alkarya ce mai kyau a birnin Kano." Ya bata amsa yana dan hura hanci kada a raina shi. Ah to shi da zai zama surukinsu gara a fara mutunta juna tun wuri.

Murmushi tayi ta tambaya shi sunansa.

"Mammaloncy ne da turanci"

Jamal da Tauhidat me zasu yi in ba dariya ba. Mammalo zuciyarsa har wani shiga shauki take yi ganin ya fara samun kan budurwar da yake da yakinin idan har ba aurenta yazo yi ba to tabbas akwai wani al'amari tsakaninsu da ya kawo shi Habujan nan. Ita kanta sai lokacin ta dan kalle shi haka nan ta ji kamar jininsu zai hadu saboda yanayin barkwancinsa.

Bayan doguwar muhawara tsakanin Papa Abayomi da Haj. Manga akan rashin gaskiya na mutane da kuma tausayin yaron da ya mamaye zuciyarta a lokacin aka ce ya shiga gaba. Papa Abayomi ya karbi tukin su kuma suka koma baya su uku.

Yana zama a motar ya dan waiga baya "Hajiya nace ba, shin yarinyar nan taki kinyi mata miji ne?"

Wata muguwar harara da ya samu daga Papa Abayomi sai da hanjin cikinsa ya karkada. Jamal na dariya ita kuma Tauhidat ta hade rai.

Haj. Manga ta kalleta tana murmushi don zancensa ko kadan bai bata haushi ba "Tana da miji idan ma saboda ita ka biyomu tun wuri a tsaya ka sauka."

"Ai ba za ku rasa 'ya'yan 'yan uwa da abokan arziki ba. Mace dai indai ta birni ce kuma gidansu akwai get ina so."

Kafin su isa gida hatta Papa Abayomi sai da ya dara. Gaskiyar dalilin zuwansa birni ya fada musu abin tausayi abin dariya. Haj. Manga ta ce indai zai dan nutsu to za ta bashi aikin yi ya samu kudin sayawa Yaya Uwaninsa abinci.

Girman Karam Mansion ya matukar tsorata Mammalo har ya tuna da 'yan yankan kai da Yaya Uwani da fada masa akwai. Jikinsa a matukar sanyaye ya fito daga motar bayan kowa ya fito. Bakinsa yana rawa ya ce "kaddai har na cika?"

Jamal yana nunawa wani yaron gidan jakarsa da zai kai masa daki ya ce "Me ka cika?"

"Na cika da imani mana an kawoni aljanna. Idan kuma gidan yankan kai ne to na rantse fatalwa zanyi muku na hanaku rawar gaban hantsi."

Dariyarsu ce ta janyo hankalin Alh. Audi da Shamsu da suke ta magana cikin bacin rai tun dazu basu ji shigowarsu ba. Murmushin dole ya dauko ya yabawa fuskarsa ya karaso inda suke. Wata mummunar faduwar gaba yaji a lokacin da ya hada ido da Mammalo da Tauhidat da tafi kusa dashi. Bai san kuma ya akayi ba haka nan ya tuno da Arqam yaron da yake ta nema ruwa a jallo a boye.

Dauriya ya yi suka gaisa Haj. Manga tana ƙoƙarin sanar da shi baƙon da ta taho dashi ya kasa nutsuwa ya saurara. A zuciyarsa kuwa fargaba ce take masa kai kawo. A cikin shekaru sama da goma sai yau ya tuna cewa banda Arƙam da Tauhidat tabbas Oga ya faɗa masa mutum uku ne manyan ƙalubalensa a rayuwa. Abinda ya kwantar masa da hankali shi ne sanin da ya yi cewa Oga yana faɗa masa duk lokacin da suka tunkaro shi. Tunda bai sake jin gargaɗi ba daga gareshi tun wanda ya yi masa gabanin zuwan Tauhidat, ya tabbata wannan ragowar yunwar ba ya cikinsu. Sakin fuska ya yi ya nunawa Haj. Manga ta kyauta wurin tunanin taimakon mabuƙaci. Daga nan ta roƙi Papa Abayomi ya tafi dashi ɗakinsa kafin a bashi wani da safe.

Suna tafiya hanyar ɗakunan ma'aikatan daga ɓangaren dabbobi jimina ta yi kuka sai birrai daga nasu kejin suka soma. Mutuwar tsaye Mammalo ya yi jikinsa ya saki sai gumi kamar anyi masa feshin ruwa.

"Fafa" ya kira Papa Abayomi kamar yadda yaji Jamal da Tauhidat suna kiransa da murya can ƙasa.

"Taho mana mun kusa. Yanzu Hajiya za ta aiko da abinci sai kaci ka yi wanka da sallah."

Maƙalewa ya yi a wurin yaƙi ƙwaƙƙwaran motsi. Papa Abayomi sai ya dawo da baya ya riƙe hannunsa ya ji ya turje.

"Meye haka ne?"

Wani siririn hawaye ne ya silalowa Mammalo ya ce "Gidan zoo ku ka kawoni daga neman taimako?"

"Gidan zoo kuma?"

"Kada ka ce komai nima da kake ganina wayis ne. Gidan zoo ɗin Kano zuwana ɗai-ɗai har huɗu saboda haka na waye da kukan birai da damisa."

Sai da Papa Abayomi ya gama dariyarsa sannan ya kama hannunsa yana jansa tare da yi masa bayanin cewa wurin shaƙatawar masu gidan ne. Lallai ba don dai har yanzu yana jin tsamin jiki daga dukan da ya sha a tasha ba da ya yi rantsuwar cewa ya mutu ne. Yanzu a gidan duniya don tsabar jindaɗi mutum sai ya kewaye kansa da namun daji? Ba komai yake jiye musu ba sai ranar da dabbobin zasu tsinke. Watanda sunan wani abu. Indai aikin da za a bashi ya danganci zuwa zoo ɗin ne ya yanke shawarar kama gabansa a gobe goben nan. Da suka shiga ɗaki bayan ya gama santin wuri ya tambaye shi garinsu.

"Na ji hausar taka ba irin tamu bace."

"Bayerabe ne ni."

Mammalo ya riƙe baki, "kuma musulmi? Ikon Allah. Yasin in ka barni duk duniya daga mu Hausawa sai Larabawa ne kaɗai muke sallah."

"To yau ka haɗu da bayerabe wanda aka haifa cikin musulunci" Papa Abayomi ya ce da sakin fuska. Mammalo ya washe baki "ni kuma Badaƙasoye ne, ai ka ji lokacin da nace sunana Mammaloncy ko?"

Dariya bata barshi ya iya amsawa ba kuwa. Haka suka kasance, sunata wasa da dariya abinsu.

***

Kulsum da Aimana suna ta murnar dawowar Nanna. Yaro ba ruwansa da kishi balle kuma ga mai kyautata masa. Suna daga cikin dalilin da ke daƙile rashin kunyar Fanna yanzu gareta. Sun gaisa a mutunce suka wuce ɗaki Jamal shi ma ya nufi ɓangarensu. Ya fito daga wanka kenan Arƙam ya kira yana mitar rashin samunsu tun dazu bayan ya san sun sauka. Jamal ya zauna bashi labarin guntun hatsarinsu da Mammalo, hankalinsa kuwa ya tashi ya shiga kiran Haj. Manga ba ji ba gani. Sallah take yi ya kira ya kai sau biyar ya kuma kiran Jamal yace ya kai mata wayar. Ya kusa isa ɗakin ya ji ya ce,

"Ka bata wayar da na baka?"

"Wa kenan?" Ya tambaya duk da ya riga ya san da Tauhidat yake.

Dan sosa kai Arƙam ya yi sannan ya ce, "ƙanwarka."

"Kulsum ko Aimana?" Ya tambaya yana dariyar tsokana a ciki.

"The other one (ɗayar)"

"To ko autar Nanna kake nufi?"

"Jamal" Arƙam ya ce da alamun gargaɗi. Ya kuwa sa shi dariya hadda yi masa tsiyar ko har yanzu yana tsoron mata kamar yadda yake a da. Lokacin idan ka ga fushinsa a makaranta an haɗa shi yin wani abu da mace. A gida kuma idan suka fita indai gidan akwai mata da yawa kasa shiga yake yi. Ya ce da Haj. Manga wai tsoronsu yake ji. Sai su dinga kallon mutane suna jujjuya idanu baƙin kwayar yana shigewa sama. Ranar da ya faɗi haka ita da babansu sun sha dariya. Ashe wata yar ajinsu ke son shi da aka faɗa masa ya ce ba ya yi shi ne fa ta koma hararsa.

Ya gaisa da Nanna ya tabbatar da lafiyarta sannan hankalinsa ya kwanta. Da Jamal ya tambayeshi ko ya kaiwa Tauhidat ba musu ya amince. Yana mamakin yadda yake jindaɗin hira da ita duk da ba ta sake masa saboda rashin sabo.

Washegari da wuri Alh. Audi ya nemi Oga a waya ya tambayeshi ko mutum na uku cikin waɗanda ya gargaɗe shi a kansu ya tunkaro shi. Oga ya yi murmushi don ya tabbatar abin da ya sami labarin faruwarsa ya riga ya faru.

"Ka kwantar da hankalinka har yanzu ko waye mace ko namiji lokacin zuwansu gareka bai yi ba saboda babu wani canji da na gani."

Sai a lokacin hankalinsa ya kwanta ya ja gwauron numfashi.

"Ba ka ga yaron da Manga ta kwaso min bane jiya. Muna haɗa ido sai jin numfashina na yi yana neman tsayawa. Yadda ka san yana gani na tsirara haka na ji."

Sake kwantar masa da hankali Ogan ya yi suka yi sallama. Ko da wasa ba shi da niyyar sanar dashi hatsarin da yaron zai zame masa a nan gaba. Ba komai ya janyo hakan ba kuwa sai nasa ƙudirin da yake ɓoyewa game da Alh. Audin.

Tauhidat da shirin komawa makaranta sati mai zuwa ta tashi bayan ta gama duka aikace-aikacenta na ɓangaren Haj. Manga. Dama an riga an saya mata litattafai da sababbin kayan makaranta tun ranar hutu na shiga SS3. Zaune take a falon Haj. Manga tana rubuta sunanta a jikin litattafan ita kuma tana bata labarin Arƙam. Wani abin ta maimaita mata sau uku ko huɗu saboda tsabar farinciki ita kuma ko sau ɗaya bata nuna ƙosawa ba. Babban abu irin wannan ya faru na murna amma tsoro ya hana ta raba farincikinta da makusantan ta. A wannan yanayin Jamal ya shigo anyi abin arziƙi yau ya taje tulin gashinsa da gayu yasa ya barshi a cukurkuɗe babu kyawun gani. Manyan kaya ya saka, shadda anyi mata ɗinkin tazarce yana ta zuba ƙamshi.

"Sai ina wannan ƙure adaka don na tabbatar ba don zuwa gaisheni ka yi ba." Cewar Haj. Manga bayan ta amsa gaisuwarsa.

Dan sunkuyar da kai ya yi Tauhidat ta dinga leƙen idonsa shi kuma yana mata nuni da baki akan ta yi bayani.

"Uhmm Nanna tsaraba zai je kai mata." Ta ce kai a kasa saboda har ta fishi jin kunya.

"Ita wa? Kada kice min da wannan sheƙar ungulun gashin nasa akwai budurwar dake sauraronsa."

A take su biyun suka ɓata fuska. Tauhidat ce mai kare masa "akwai Nanna kuma yar islamiyyarmu ce. A wurin kaini suka haɗu kuma kyakkyawa ce sosai."

Murmushi ta yi. Ita dai haɗin kansu yana matuƙar burgeta bata fatan wani abu mara daɗi ya gifta tsakanin yayanta. Yadda Tauhidat ta ɓata fuska ne yasa ta cewa "Maida wuƙar ƙanwar Jamalu. Tunda bokon yaƙi idan auren yake so sai na yi masa ai."

Zai yi magana Tauhidat ta riga shi. "Nanna Jamal fa zai baki mamaki." Ta juya tana kallonsa yana zaune ya tallafi fuskarsa da tafin hannayensa yana kallonsu "kai kuma idan ka cigaba da bin su Mannirun nan ni ma ba ruwana da kai."

Da sauri ya soma bata haƙuri hadda alƙawuran maida hankali a karatu kamar gaske. A gaban Nanna ta yi masa a bayanta idonta ma haka. Shi fa idan za ka ƙure shi akan su wa yafi so a rayuwarsa daga Nannansa to tabbas Tauhidat sai ta zo a ta

biyu sannan Arƙam ya biyo baya. Shaƙuwa ce mai ƙarfi sosai a tsakaninsu tamkar da gaske cikinsu ɗaya. Yana fita sim ya fara saya ya saka mata a wayar da ko yau da safe Arƙam ya sake masa tuni da ya bata kuma ya tabbatar ya saka mata kuɗi. Katin dubu goma ya loda mata sannan ya wuce gidansu budurwa.

Haj. Manga gudun tone-tone tunda ta ce dubiya za ta je shi ya sa Kulsum da Aimana kaɗai ta sayawa riguna da takalma. Yarta kuwa akwati guda ne da kaya da tarkacen yan mata na kwalliya. Turarakan jiki da na kaya masu ɗan karen ƙaamshi kuma saƙon Arƙam ne a wata yar jaka mai kyau. Murnarta ba a cewa komai. Tun tana godiya ta koma ƙwalla. Sai da Haj. Manga ta soma faɗa ta dena kukan. Ko gama ganinsu bata yi ba ta tashi zuwa dakin mahaifinta ta faɗa masa tunda ido ba zai bari ta kinkimi akwatin ba.

Daga bakin bene tun kafin ta gama saukowa take jin sautin dariyar Fanna. Ta soma saukowa ta hango Papa da Mammalo ya taƙaƙare yana bayani. Takunta Fanna ta ji ta ɗago idanunta hadda hawaye don dariya ta ce mata ta kirawo Nanna baƙonta na jiranta. Komawa ta yi ba jimawa suka sauko tare. Papa Abayomi ne ya musu bayanin cewa daga fitowarsu zai nuna masa gidan ya rikice masa wai a saita shi gabas zai koma ƙauyensu. Girma da haɗuwar gidan sun matuƙar tsorata shi ya soma kokwonton ko cinikin kansa zasu yi da turanci tunda ba ji yake ba.

Sai da Haj. Manga ta yi da gaske wurin kwantar masa da hankali sannan ta ce daga yau Papa Abayomi ya soma koya masa abubuwan mota. Ya san sunan kowane bangare da amfaninsa sannan a kai shi makarantar koyon tuƙi. Tana so kuma duk inda aka aike shi su je tare saboda ya gane gari shi ma wata ran a aike shi.

Bayan ta gama duka bayananta Mammalo ya muskuta gaba a hankali sai ga shi a kusa da kujerar da Haj. Manga take. An gama magana bai ji an sako batun abinda ya kawo shi birni ba.

"Hajiya sai maganar albashi na ko."

Gyara zama ya yi saboda abinda zai faɗa ya ƙudurta a ransa yadda gidan yake da girma to fa ba zai musu lamuni wurin albashi ba. Da yatsun hannuwansa ya shiga lissafi.

"To da farko dai shinkafa kwana uku idan yar hausa ce, kwano biyu idan ta gwamnati ce. Sai wake da gero suma kwano bibbiyu. Kwantirola kwalaba ɗaya amma kwalabar seben o (seven up) don tafi girma. Sai gihiri da mai tauraro yan hansin-hansin. Da kuma kuɗin motar da zan kaiwa Yaya Uwani." Ya kare maganarsa da haɗe fuska don tun yana lissafin ya kula kamar suna mamaki. Shi kuwa ko yi ko bari ba zai rage ba.

"Yanzu Mammalo da wannan ka ke so a biyaka?" Fanna ta tambayeshi don har ga Allah ya bata tausayi. Duk a lissafinsa nan fa ya ƙure su kenan.

Ita kuwa Haj. Manga cewa ta yi yaushe yake son a kaishi wurin yayar tasa za ta so ganinta. A zatonsa ko so suke ita ma a taho da ita gidan. Nan ya fitittike musu ya ce shi yayarsa tafi ƙarfin aikatau.

"Ah to, irinsu Yaya Uwani fa sai Kansila ba don ƙaddarar auren matsiyacin nan ta gitta mata ba da yanzu ana kiranta Hajiya."

Haj. Manga ta sanar da shi cewa albashinsa na farko za ta biya shi saboda haka take son yaje gida ya kaiwa yar uwarsa nasa rabon. Daga jin haka Papa Abayomi ya riga ya san uwarɗakin nasu alkhairi take nufin Mammalo da shi. Godiya ya ta ya shi yi mata ta ce washegari sai a kaishi gida saboda ita ta fi gane duk wanda zama ya haɗasu to ta san asalinsa. Suna wannan tattaunawar Jamal ya dawo. Da hannu ya yafito Tauhidat suka hau sama zuwa falon Nanna. Wayarta ya nuna mata ƙirar Nokia mai matuƙar kyau daidai yan mata. Ta saki baki ta ma rasa abin cewa ya ɗauko tasa da zummar saka mata nambar Arƙam sai ya ga suna ya bayyana kafin ya kai ƙarshe an rubuta Karam 1 a jiki. Ɗan murmushi ya yi da ya ga tasa numbar da Karam 2 ya mata saving. Miƙa mata ya yi,

"Arƙam ne ya saya miki, ki kira shi yanzu don ya dameni akan na baki wayar. Da kuɗi a ciki na san zai isheki."

Sai da ta gama godiya ta koma yi masa mitar yadda ya hanata kiransa da Yaya ta kula haka yake kiran ɗan uwan nasa.

"A wurin wa na koya ni ma? Shi ne fa mai ƙorafin wai sunansa is too sweet bai yarda a ɓoye masa da wani Yaya ba. To ni ma nawa da daɗi ga gudun tsufa so kawai sammakal ki kiramu kai tsaye."

Kai ta gyaɗa kawai tana biye da shi, "muje na nunawa Nanna."

"Ta gani tun a can, please ki kira shi yanzu na huta da mitarsa."

Kitchen ɗin ɗakin ya shiga neman abinda zai ci ita kuma ta shige ɗakinta. Sunan ta ke ta kalla tana murmushi kafin ta tattaro ƙwarin gwiwa ta danna kira. Farar safiya ce a can ƙarfe shida da yan mintuna. Yana cikin cire scrubs ɗinsa (kayan aikin asibiti) bayan sun fito daga wata emergency theatre wayar ta shigo. A gajiye yake sosai idanunsa da ƙyar yake iya buɗeu saboda bacci. Gida yake son ya tafi ya kashe waya ya kwanta sai azahar. Baƙuwar number da ya gani kuma daga Nigeria sai kawai jikinsa ya bashi ita ce. Tana jin alamun ya ɗaga ta yi masa sallama a ladabce kuma ta kara da, "ina wuni?"

Earbud ne a kunnensa irin wanda ake amsa waya da kunne ɗaya mai dan girma saboda haka ya cigaba da balle maɓallan rigarsa yana mai jindaɗin muryarta.

"Bamu wuni ba Cuddles."

"Cuddles?" Tauhidat ta ce da mamaki.

"Yeah" ya amsa a lalace saboda wata muguwar gajiya da ta sake saukar masa.

"Me yake nufi?"

Sautin murmushinsa har kunnenta sannan ya fassara mata kalmar tana nufin mutum mai jiki irin wanda ake son rungumewa ko a kwanta a jikinsa. Kafin ya gama dogon turancin nasa ta buɗe baki yafi a ƙirga saboda kunya da mamaki. Yanzu ita ɗin ce za ta yi daɗin runguma sai kace wani pillow?

Tana can tana tunani har ya gama shiryawa ya rataya jakarsa bayan ya fito da mukullin motar daga ciki.

"Uhmm bari na kashe maybe yanzu ka tashi daga bacci."

"Zan tafi gida ne nayi call yau."

"To sai anjima" kit ta kashe wayar.

Kafin ta fita daga ɗakin ya sake kira. Hira ya buƙaci ta yi masa wai yana jin bacci sosai saboda haka yana buƙatar abinda zai ɗauke masa hankali har ya isa gida. A zahiri muryarta kawai yake son ya cigaba da ji ba wani abu ba. Shiru ta yi ita ma

saboda rashin sabo ta rasa abin cewa. So yake ta saki jiki da shi kamar Jamal.

"Bani labarin Nanna. Yanzu na manta things about her (abubuwa game da ita)."

"Faɗa min waɗanda ka tuna tukunna."

Tuƙi yake cikin nutsuwa yana ta murmushi. Wai shi za ta nunawa tana da wayo.

"Lokacin Abbanmu yana nan tana yin baki-baki da baka-baka."

Allah Ya sa ta taɓa jin wannan sunan a wurin Jamal ta soma dariya "burabusko da miyar kuka!"

Ɗan zaro idanu ya yi "don't tell me (kada ki ce min) har yanzu tana yi."

"Idan za ta zo wurinka zan tuna mata ta taho da tsakin da kuka ta yi maka." Ta tsokane shi.

Har ya hango abin a idonsa kuwa ya kyaɓe fuska da sauri "No, ba na ci fa! Amma ba tare za ku zo ba?"

Shiru ta yi. Ita fa yar direba ce kuma ba ta son zaƙewa akan matsayinta. Yanzu ma wayar nan a takure take jin kanta. Tana gudun ce masa ba tare zasu zo ba kada ya je ya yi wa Nanna magana a haɗa da ita ko ba niyya. Basu taɓa yi mata wani abu na ƙasƙanci ba amma kamar yadda babanta ke ja mata kunne a duk lokacin da suka keɓe, yana da kyau ta dinga sara tana duban bakin gatari.

"Kafin mu zo tare nake nufi."

"Kamar baki son ganina Tauhidah. Ni kuma ina son ganin yan uwana da yawa musamman ke."

"Ni kuma? Me yasa?"

"Honestly I don't know. I just want to know you (zancen gaskiya ban sani ba, kawai ina son saninki ne)."

Shiru suka yi har ya ajiye motar ya shiga gida. Sai da ya gama shirin wanka ya faɗa mata ta kife wayar ko sallama babu saboda nauyin da maganar tayi mata.

"What's her problem? (Meye matsalarta?)" Ya tambayi kansa. Tunda babu mai bashi amsa shi kaɗai ya ke ayyana ko don basu saba bane. Alƙawari ya ɗaukarwa kansa kafin su haɗu sai

ya sa sun saba ta sake dashi sosai. Bayan ya gama waya da Haj. Manga da daddare kuwa ya sake kiranta. Wayar tana ɗaki ta manta da ita saboda rashin sabo. Ta Nanna ya kira ba kunya yace ta faɗa mata ta ɗauki wayarsa. Murmushin manya ta yi tana fatan Allah Ya kai damo ga harawa. Duk duniya bata jin akwai wanda zai kaita farinciki. Haɗuwar waya da hoto kawai ɗan nata yana wasu abubuwa da ita kanta ta yi imanin bai san girmansu ba ga mace. Ta yarda da yarta, rashin samu ne kaɗai zai sa mutum kusheta don ya huce ɗacin rai ba don tana da makusar ba. Wa yafi cancanta da morar rainonta sama da jininta? Waye za ta iya haɗawa da yar da take jin ta har ranta ya riƙe mata ita amana sama da jinin nata dai? Kiranta ta yi tana falo ta ce ta ɗauki wayarta ana kira. Missed calls uku ta gani da ta duba. A take wani kiran ya sake shigowa. Sunan ɗazu ya kirata dashi ta zumɓura baki kamar yana ganinta.

"Na fa duba dictionary. Ashe mutum ɗan lukuti ake kira haka? Ni dai ba lukata bace."

"Lukuti fa yana nufin fat, ke kuma you are not fat, just chubby."

Buga hannu ta yi akan pillow ta ce "Ni dai gaskiya..."

"Cuddles"

"Na'am." Ta amsa ba shiri

Ya yi dariya "kina son sunan kenan, ni kuma ba zan canja ba."

Maganarsu da Jamal ta rana ta tuna "to kai kuma sunanka Yaya ko Brother."

A take ya faɗa mata yadda Jamal ɗin ya ce mata kuwa. Shi yana son sunansa sosai bai yarda ba. Ta ce wato nata sunan babu daɗi ya ce a'a yana son sunan amma ta yi haƙuri tunda dai gaba yake da ita babu canjawa. Alƙawari dai zai mata shi ne ba kullum zai kirata haka ba. Wani lokacin Tauhida zai ce. Sai da suka kwashe wurin awa guda a rigimar suna har ta fara hamma sannan ya ƙyaleta.

Kafin sati kuwa Fanna ma sai da ta fara zargin ko saurayi Tauhidat tayi. Daga waya sai text. Sai tana zaune ka ga ta tashi tana murmushi. A nasa ɓangaren da ya sami break a wurin aiki ko ya tashi ya koma gida bashi da aiki sai kiran gida. Daga ya gama da Nanna to kunnen Tauhidat bashi da sakat. Ba ta taba kiransa da kanta amma har tsumayin ya kira take yi.

Kwana tara da dawowarsu Haj. Manga ta yanke shawarar zuwa wurin Dada ta faɗa mata gaskiya game da jikanta. Lokacin Tauhidat sun koma makaranta Mammalo kuma an zama ɗan gida saboda bai iya baƙunta ba. Sati na gaba Shaheed zai dawo tuni an bashi wani ɗakin amma kullum yana jikin Papa Abayomi yana bashi dariya. Saboda a kaishi gida ta yanke shawarar tafiyar mota.

Mammalo ya fito lokacin sun shiga baya ita da Tauhidat. Yar jakar kayansa Papa ne ya saka a boot da kansa saboda haka duk tunaninsa bai wuce gida zasu mayar dashi ba batare da an biya shi ba ma. Zamansa ke da wuya a mota Fanna ta aiko Kulsum da envelop ta bawa Haj. Manga wai a ƙarawa Mammalo guzuri. Godiya ta yi mata sosai kuwa, ya baza kunnuwa yana jiran a ce ya miƙo hannu ya karɓa yaji shiru. Haka nan aka yi tafiyar jikinsa a saɓule. Yanzu haka zai koma gida bai samo komai ba yan garin ya san za su saka shi a gaba da surutu.

Hanyar gidansu ba ta mota ba ce saboda haka da yar tazara tsakanin gidan nasu da inda aka ajiye motar. Papa Abayomi ya ce masa ya samo masu taya shi kwashe kaya a boot.

"Fafa kenan, miƙo min jakata kawai na saba a kafaɗa. Me za a zo tayani ɗauka kamar wanda aka bawa kwanon shinkafa da wake bibbiyu kamar yadda na kwantas da kai na roƙa."

Da yake akwai zulumin yadda Dada za ta karɓi maganar Arƙam sam Haj. Manga ta kasa sakewa sosai. Tana cikin damuwa ta ki faɗa. Shi ya sa Tauhidat ta jefa wayarta a jaka yau taƙi biyewa hirar Arƙam sai janta take ta hanyar bata labarin makaranta da suka koma ranar litinin.

Bude boot ɗin Papa Abayomi ya yi Mammalo ya tafi da niyyar ɗaukar jaka ya yi arba da buhunhuna da kwalaye ga galan ɗin manja da na man gyaɗa. Dariyar farinciki ce ta mamaye fuskarsa da ta soma cikowa saboda cima mai kyau.

"Ha in ruga bakin titi na karɓo laidos a wurin Ɗanasabe mai kiyos. In haɗo da kwano ko kuna dahi?"

"Meye laidos kuma?" Inji Papa Abayomi.

Tafa hannuwa ya shiga yi yana kaɗa kai "ledoji da turanci. Ka san fa na soma firamari, da dan boko na ma na san idan gayu

yayi gayu ana kara cyyyyyy a ƙarshen suna." Ya fitar da kalmar tamkar sakin takurarrariyar tusa.

Sai ga Tauhidat da Haj. Manga suna dariya hadda hawaye. Balle da ya ce zai karɓo ledar ne su aunar masa komai kwano kwano aka ce masa duka na Yaya Uwani ne. Ya kusa suma ya shiga far-far da idanu yana neman faduwa. Irin addu'ar da ya jerowa Haj. Manga sai ta ji inama ta ƙara masa fiye da haka. Buhun shinkafa da na wake bibbiyu ne sai na gero karami. Ga kwalin taliya da macaroni da na maggi da gishiri. Mai kowanne galan guda da omon wanki, sabulun wanka da man shafawa. Kuɗin da Fanna ta bayar ya karɓa ya ƙirga sai ya zari biyu ya maida mata. Shi tsoron kuɗin ma yake ji. Dubu ashirin zuwait kamar wanda yaje fashi? Sai da ya gama yar diramar tasa ya ruga gida a guje.

Yaya Uwani hadda hawayen murnar dawowarsa. Da ƙyar take ɗaga ƙafa don ma ta roƙi wata Gwaggonsu ta dawo gidan saboda haihuwarta da ta matso. Haka ta daure zuwa inda aka ajiye motar ya gabatar dasu Haj. Manga da abin arziƙin da aka basu. Kuka hadda majina suna ta godiya ta roƙi Haj. Manga da ta dinga haƙuri da Mammalo. Shi kuma a gabansu ta rantse idan yaci amarsu kwarankwatsa sai ta kama shi. Da taimakon wani abokinsa suka kwashe kayan Haj. Manga ta bata sauran kuɗin sannan ta ce ya shirya ranar Lahadi zasu tsaya su ɗauke shi su wuce.

***

Dada bata ce komai ba har Haj. Manga ta gama yi mata bayanin komai. Su kaɗai ne a ɗakinta. Babu hawaye ko ɗigo a idanun baiwar Allahn nan sai murmushi cike da jindaɗi.

"Hafsatu ki sani cewa a tare da addu'a akan sami jinkirin ganin biyan buƙata amma tabbas a duk lokacin da ka ɗaga hannu kana tare da samu. Yanzun shi ne lokacin da Allah Yaso mu san inda Arƙam yake."

Wani hoto Haj. Manga ta ɗauko wanda tun bayan dawowarsu take fargabar kada ya faɗa hannun da zai tona asirinta a gidan. Saboda gudun tsautsayi ko Tauhidat bata bari ta san da zamansa ba. Miƙawa Dada ta yi wadda ta saka kuka a lokacin.

"Da gaske shagwaɓaɓban yaron nan likita ya zama." Ta ce tana shafa hoton. Yana tsaye sanye da kayan likitoci na asibitinsu ya ɗora labcoat ga stethoscope zagaye da wuyansa. Sun gama

jajantawa juna Dada ta ce ita ma bata yarda ya dawo ba. Idan mahajjata sun dawo zuwa ƙarshen shekara ya tafi umara su haɗu a Saudiyya. Haka ya yiwa Haj. Manga daɗi sosai. Haɗasu ta yi a waya, Allah Yaso yana gida ya sakankance yana gwada mata halinsa da ta san shi dashi tun ƙuruciya. Tsohuwar nan ta yi kuka ta yi dariya ta kuma tsinewa Alh. Audi sau babu adadi. Biye masa ta yi suka sha hira sosai.

Burinta ya cika. Su kaɗai suka rage mata tsani tsakaninta da Mal. Iro Karamci. Mahaifinsu ya rasu sune take gani su sanyaya zuciyata.

Tauhidat ta kira ta zo kwashe kwanukan da aka ajiye musu na abinci kamar daga sama ta ce "ni kuwa Hafsatu an raba gadon yaron nan kuwa? Ba wai don na damu da a bani wani abu ba, ko kaɗan. Kawai kinsan shi gado nauyi ne ga mamaci."

Shiru Haj. Manga tayi mamaki kamar ya danneta a wurin. Ashe fa duk tsayin shekarun nan ba a taɓa zama da sunan raba gadon mijinta ba. Zabura ta yi ta miƙe

"Tauhida ɗauko min wayata da sauri na kira Baffa." Bayan ta tafi falo har lokacin tana jiyo muryar Nanna tana faɗawa Dada cewa tunanin bai taba zuwa kanta ba. Kuma bata san inda komai yake na shaidar abinda ya bari ba. Dada ta ce ita ma sai a yan kwanakin nan abin ya faɗo mata.

Ta ɗauko mata wayar a cikin jaka ta kawo ta miƙa mata. Ko da ta karɓa sai ta hau dudduba sunaye ta rasa me take nema. Dada ta kalla ta ce "Dada zancen me muke yi ne ma?"

Yar tsohuwa ta murmusa "maganar zamu haɗu da Arƙam a Saudiyya mana. Ba don Hajji ba da gobe goben nan zan bar ƙasar nan."

Kan Haj. Manga sarawa ya soma yi da ta matsawa kanta da tunani saboda ta tabbatar cewa sunyi wata magana mai matuƙar mahimmanci amma kamar an shafe mata ƙwaƙwalwa. Wayar ta miƙawa Tauhida kana ganin yanayinta ka san bata ji daɗin wannan mantuwa ba.

"Jeki da ita na manta wa zan kira."

Jiki a sanyaye Tauhidat ta karɓi wayar ta fita. A bakin ƙofar ɗakin ta tsaya tsoro da fargaba na cika zuciyarta. Wannan wane irin abu ne haka? Yanzu suke zancen ba a raba musu gado ba amma cikin abinda bai fi ƙiftawar ido da buɗewa ba

duka sun manta. Ita kuma da bata manta ba ɗin wani irin tsoro ne na ban mamaki ya kama ta ta yadda take jin ko da wasa bazata iya faɗawa Nanna ba duk son da take mata. Damuwar da take gani a fuskar Nanna tasa ta yakice tsoron ta yi nufin tuna mata. Sai dai kuma da ta buɗe baki sai ta ji harshenta ya yi nauyi. Abin ya ɗaure mata kai fiye da zato da tsammani. Ga magana a saman harshenta amma taƙi fita. Hankalinta ya tashi matuƙa. Wayarta ta ɗauko za ta rubuta a ciki sai ta tura mata nan ma abu yaci tura. Tun tana daurewa kuwa sai ga hawaye. Ga abu yana cin ka a rai amma ka kasa faɗa.

Banɗaki ta shiga tasha kukanta son rai ta fito. Ranar bata iya bacci ba duk da gajiyar da suka kwaso ta hanya. Sau biyu tana tashin Haj. Manga idan ta gama karantawa zuciyarta dauriya. Tana farkawa sai ta kasa motsa bakin. Kafin asuba sai zazzaɓi mai zafi. Ko kaɗan zafin jikin ba shi yake damunta ba kamar wannan abu da ta laƙabawa tashin hankali. Kuka ta saka da abin yaci tura tana ta addu'a domin neman samun sauƙi.

Karfe tara a wani asibitin kuɗi ta yi musu aka zurkuɗa mata allurai da magunguna. Haj. Manga duk ta tashi hankalinta ganin tana share hawaye. Ta zata zafin zazzaɓi ne ita kuwa Tauhidat ba ta shi take yi ba. Bayan sun dawo tana ta lallaɓata ta ci abinci sai ga wayar Arƙam. Bayan sun gaisa ta faɗa masa Tauhidat ba lafiya. Ta san ko bata faɗa ba sai ya tambayi ina take tunda ya kira bata ɗauka ba.

"Nanna ki bata wayar."

"A kwance take ka bari ta huta."

Ya tabbatar ba zai iya bacci ba idan bai ji muryarta ba. "Please just a minute na ce ya jikinta."

Dada tana kallonta ta yi murmushi "ki bata mana su gaisa."

Ɗakin da suka kwana ta bita ta bata sannan ta fito. Dada ta ce tana fatan dai abinda take zargi ne tsakaninsu. Gara a haɗa shi da ta gida kafin ya ɗauko musu baturiya. Suna hira suka ji sallamar Alh. Audi. Tauhidat tana ɗaki idanunta jazur saboda hawaye ta ma kasa amsa ya jikin da Arkam yake mata kawai ta jiyo muryar da ta saka ta kusan sakin fitsari a kwancen. Wuntsilowa ta yi a firgice ta fito daga ɗakin. Tamkar ita yake jira kuwa tana fitowa suka haɗa ido. Irin kallon da ya yi mata sai da ya tsinka mata jini saboda tsabar firgici. Bata taɓa jin tsoronsa ba sai yau. Jikinta ke bata ya san me yake faruwa

shiyasa babu wani dogon lissafi don bata ma san ta yi ba ta maka masa wata uwar harara ta saki laluben ta juya. Gumi ya shiga tsatstsafo masa da ganin dahir game da abinda Oga ya faɗa masa a daren jiya cewa sirrinsa daya ya shiga kunnen Tauhidat. Bai san wanne bane cikin sirrukan amma ya kiɗime don gabaɗaya duk abinda ya kira sirri to ba ya fatan duniya ta taɓa ji.

Da yake babu wanda ya ga leƙowa da komawarta basu damu ba. Wayancewa ya yi da cewa yaso tahowa jiya tare da Haj. Manga gaishe da Dada aiki ya riƙe shi. Babu wata magana daya da yake faɗa wadda ta ƙara masa daraja a idanunsu sai dai a bishi da to. Tauhidat sai taji girmansa gabaɗaya ya zube a idanunta. Sai yanzu wasu abubuwan ke dawo mata kamar uban kudaɗen da yake bawa Jamal duk kuwa da an san me yake da kuɗi. Nanna ko ƙwandala bata bashi saboda shaye-shayen da yake amma saboda taya ɓera ɓari a irin kuɗin da Alh. Audi ke bashi har kyautar motarsa ya bawa wani abokinsa ya sayi sabuwa.

Wunin ranar a ɗaki ta yi shi, saboda rashin ƙwarin jikin da ya same ta. Babu yadda Haj Manga da Dada basu yi da ita ba, amma taƙi fitowa. Haka shi ma ya dinga zuba, yana daɗin baki. Har dai ya gaji da zaman munafurcin ya tafi. Washegari suka ɗunguma sai Abuja, tare da Mammalo da aka ɗauka a hanya. Rayuwa ta cigaba a inda Haj. Manga ta nemi contractors aka tsantsara mata zanen makarantar primary irin wadda ake haɗawa da karatun arabiya da Qur'ani sosai. Makarantar aji ɗaya zuwa shida ce, wadda take burin wadatawa da abubuwa na zamani. Sosai take burin ginata, domin taimakawa yara wajen jindaɗin karatunsu. Babu abinda ta faɗawa Alh. Audi don wannan karon taci alwashin ko me zai yi ya yi ƙarya ya rabata da abinda yake mallakinta.

Ana wannan tsarin a gefe ta gama da cinikin fili da komai, ranar wata Laraba sai ga Madam Zainaba ta shigo gidan lokaci ɗaya. Koda suka haɗa ido ta ji ba daɗi, domin wata guda da dawowarsu daga wurin Arƙam ko sau ɗaya bata nemeta ba. Bata yi tsammanin ma za ta dawo ba. Ɗauke kai ta yi ta shige gida. Madam Zainaba ta rame sosai saboda ciwo. Rashin ji daga Hajiyan ya sa ta kasa haƙura ta gama samun lafiya ta taho. Ɗakinta na ɓangaren ma'aikata taje ta fara ajiye kayanta sannan ta shiga cikin gidan. Tauhidat tana makaranta haka su Kulsum. Tunda bata da shamaki kai tsaye ta shiga falon Haj.

Manga wadda take ta safa da marwa tana jiran shigowarta. Yanayin fuskarta kaɗai ya ishi Madam Zainaba sanin cewa babu lafiya. Jikinta a sanyaye ta daure ta ƙarasa ciki sannan ta gaisheta.

Auna ƙarfin hali irin na Madam Zainaba ta yi kafin ta sake haɗe rai bayan ta zauna tana fuskantarta sosai.

"Zainaba wace irin zuciya ce a ƙirjinki da ta baki damar iya daurewa ganin hawayena tsayin shekarun nan amma baki taɓa tausaya min ba? Wace riba ki ka tsinta a sakamakon cin amanata?"

Bata gane kan maganar ba amma ta tabbatar cewa ran Haj. Manga ya ɓaci da ko ma mene ne.

"Hajiya me na yi?" Madam Zainaba ta tambaya a tsorace.

Haj. Manga tana son sanar da ita cewa haƙansu bai cimma ruwa ba amma tana tsoron abinda zai faru "ba zan ja magana dake ba ki kwashe kayanki kafin gari ya soma duhu ki koma wurin waɗanda ki ke yi wa aikin. Ki faɗa musu cewa Allah ba azzalumin Sarki bane inji ni."

Tashin hankalin Madam Zainaba ba zai faɗu ba. Haƙuri take son badawa amma babu ƙofa, domin irin maganganu masu zafi da take faɗa mata sun tsaya mata a zuci. Bata rabe ɗayan biyu, shiga tsakaninsu aka yi. Ta riga ta san halin Haj. Manga tunda take ganin kamar taci amanarta ne to fa sai ta yi da gaske za ta fidda kanta. Zaman shekara goma shaɗaya cikin rabin awa ya ƙare tsakaninsu.

Haj. Manga ta yi fushi sosai, babu kuma laifinta domin ko waye zai yi haka ko ma fiye. Arƙam da ya kama sunan Madam Zainaba ɗin shi ma abinda ya sani ya faɗa ga Tony ya bar ƙasar. Alh. Audi kansa ya gaji da nemansa ya ɗauki wani da Oga ya haɗasu ya maye gurbinsa.

Duk yadda ta roƙeta akan ta bari ta kwana abu yaci tura. Yadda ta shigo haka ta fita, ita ɗaya sai guzurin barazanar hawan jini bayan diabetes ɗin da take fama dashi. Tasha ta wuce kai tsaye don ba ta da wani wurin zuwa a garin kuma.

***

Yanzu da Mammalo ake kai Tauhidat makaranta a ɗaukota. Bayan dawowarsu daga Kano ta yi ƙoƙorin cire damuwar

maganar da taji daga ranta. Duk wanda taso faɗawa ta kasa, sai ya zamana ta sake saka ido sosai wurin ganin tana kula da Nanna yadda ya dace. Iya mafitar da wayonta ya hasko mata kenan tunda abin yafi ƙarfin tunaninta.

A yau suke shirin tarbar Shaheed. Haj. Manga ta tada hankalin masu aiki, sai ka rantse ɗan cikinta ne a hanya. Ba ta gajiya da cewa tana son zuri'ar Abayomi domin mutane ne na ƙwarai. Tana yawan jinsa yana yi wa Jamal faɗa akan shaye-shaye da rashin mayar da hankali akan karatu.

Abinci da snacks kala-kala tasa aka yi sannan aka gyara masa wani ɗakin don ta ce zamansa da mahaifinsa takura ne garesu. Shiri sosai ta yi ta tura direban gidan ɗauko shi daga airport tare da Tauhidat da Mammalo. Papa Abayomi ta umarta da ya zauna a gida ya tarbi ɗansa. Idan yaje da kansa tamkar yaje a bakin aiki ne kuma ba za ta so hakan ba. An jere duka kayan abincin a ɗakinsa, komai na mutum uku ta tsara wato su da babansu. Lokaci ne da zasu keɓe na taya juna farinciki. Da gudu Tauhidat ta isa gareshi, ta rungume shi tana murna. Shi ma ya rasa inda zai sa kansa don farinciki. Da yarbanci ya ce

"Tosin kece kuwa? Yaushe ki ka girma haka kin zama yan mata."

Kunya ya bata ta sunne kai a ƙirjinsa "Brother kaima ka yi kyau sosai kamar ba kai ba."

"Ina Papa?"

"Yana gida yana jiranka.

Mammalo an ga ɗan ƙasar waje, jiki na rawa ya dinga kinkimar akwatunansa yana sakawa a boot.

"Wannan fa? Ban san fuskarsa ba." Shaheed ya tambayeta.

"Mammaloncy kenan" ta amsa da murmushi.

Jin an ambaci sunansa ya taho da sauri "Allah e sa yayan naki iya jin hausa. Kin tuna na faɗa miki iyakata firamare ba wani nisa na yi ba a turanci."

Zancen kenan iyakarsa firamare. Daga ita har Shaheed dariya ya basu. Hannu Shaheed ɗin ya miƙa masa zasu gaisa idanunsa suka sauka akan wasu maza biyar yan ƙasar China. A iska ya barwa Shaheed hannunsa ya juya kallon ikon Allah.

Yarfe hannuwa kawai yake yi yana ɗaga kafafu ya dire kafin ya sandare a wurin.

Direban da ya kawosu dama ba hausa yake ji ba amma yanayin da ya ganshi ya bashi tsoro. Tauhidat da Shaheed ma sun zata wani abu ne ya same shi. Kaɗafarsa Shaheed ya ɗan doka ya kuwa saki ihun murna yana jijjiga Shaheed ɗin da ƙarfinsa.

"Wohohooo, eh na yarda inda rai da rabo. Yar gidan Nanna duba min ki gani Brut Li nake hangowa ko gizo yake min?"

Sai da ta toshe bakinta don dariya shi kuwa sai cewa yake "aka ce mana ya mutu ahe duk ƙarya ne Yasin." Cikin sauran mazan akwai wanda yafi gajarta ya nuno shi da hannu harda ɗan hawayensa na farinciki "kinga ga ƙaninsa can Jenti Li, na san cikin waɗancan da suka bada baya ba'a rasa Jaki Chan."

Shaheed dariya, Tauhidat dariya aka rasa mai gyara masa a cikinsu. Mammalo daɗin ya masa yawa ya kasa haƙuri su dai sai hango shi suka yi a gaban mutanen nan. Irin gaisuwar da akan yi a finafinan China, na zamanin da za ka ga mai koya faɗa da ɗalibansa suna bashi girma haka ya yi musu. Kansa a ƙasa ya dunƙule hannu ɗaya, ya saka cikin ɗan uwansa ya ce musu.

"Shan kwenkwen chizo fa."

"Kut...Brother ku sameni a mota, ba za ayi wannan abin kunyar dani ba."

Inji Tauhidat ta ruga ta shige mota tana dariya sosai. Ta tabbata cigaba da tsayuwarta tana kallonsa zai iya sawa a ɗauko musu yan sanda saboda dariyar da take yi. Mutanen birnin Sin sai suka hau yare suna tambayar juna ma'anar abinda yake cewa. Shi kuma sai ya zata amsa masa suke yi ya hau gyaɗa kai,

"yes yes shanwe shanwa."

Shaheed ya daure ya yi ta maza ya matsa gabansu, ya basu haƙuri da turanci. Sun amsa masa a sake ya nuna musu Mammalo mai son finafinan ƙasarsu ne shi ya sa. Ransa ne ya soma ɓaci da ya ga kamar ƙwacensu Shaheed zai yi masa ya ɓata rai "Me ku ke cewa? Ka barmu mu masu jin yaren muyi a junanmu ba sai kunyi turancin ba."

"Muje mota sun ce zasu kira security ne a tafi da kai wai ka dame su."

A guje ya bar wajen kafin Shaheed ya gama magana ya shige motar. Suna tafe a hanya ana maida zance da dariya Arƙam ya kira Tauhidat. Dama ta faɗa masa zasu je ɗauko yayanta yau. Kunyar ɗauka taji kada Shaheed ya ce meye tsakaninsu. Sai kuma ta tuna ita kaɗai ta san ko waye shi bisa amanar Nanna. Ya kuma kira sau biyu tana tonawa kanta asiri ta hanyar kallon wayar da ta kashewa fitar sautin kara. Kamar daga sama ta tsinci muryar Shaheed, ya matso kusa da ita "indai ni ki ke jin kunya ki ɗauki wayarki amma fa sai kin faɗa min ko waye idan na huta."

"Ba fa abinda ka ke tunani bane" ta furta maganar tana tura masa baki.

Ya yi murmushi "to ɗauki ki bani mu gaisa. Kinsan dole a kama ƙafa dani." Sai kuma ya kawar da zancen ganin da gaske kunyar ɗauka take ji.

"Wai ina amininki ne Jamal?"

Kafin ta bashi amsa da cewa yana makaranta, Mammalo ya juyo daga gaba yana rarraba idanu tsakaninsu.

"Nace ba, ko za ku yi firar da hausa yadda zan iya tofa albarkacin bakina nima? Da shike ina yawan faɗa ban yi nisa a boko ba. Iyakata firamare da munyi da turanci ko don mai tuƙa motar nan."

Ya ɗan kanne ido, "kunsan ba daɗi na kama sunansa bai san me nake cewa ba."

Shaheed ya fi kowa dariyar shirmen Mammalo. Hirar yan China ya sako musu motar ta kaure da dariya kuwa. Alamun shigar saƙo Tauhidat ta gani a wayarta ta duba. Murmushin da ta yi ne ya ƙara ƙarfin zargin da ɗan uwanta ya ke yi, na cewa ko waye yana da babban matsayi a wajenta. Saƙon text ne daga Arƙam da harshen turanci kamar haka.

(Hey Cuddles, yau na yi kewarki. Ki kirani idan kun isa gida. Nanna ta ce baku dawo daga airport ba. Ina gaishe da Brother Shaheed kuma ina fata ni ma idan na dawo dake za a zo ɗaukata?)

Kalamansa sun yi nasarar kashe mata jiki, ta yadda ta kasa rubuta masa amsa sai juya su da take yi a cikin zuciyarta. Sabonsu da Arƙam yana bata tsoro, saboda yanzu kusan komai na juna sun sani. Da wuya su kwana uku basu ji muryar juna ba. Tun yana hirar tana bashi amsar kurame har ta sake ta fito masa a Tauhidat ɗinta sak. Yarinya mai surutu da yawan abin dariya. Tuni ya waye da halinta na rashin saurin fushi da yawaita uzuri. Ya ɗokantu da haɗuwa da ita domin yadda suka shiga rayuwar juna yanzu shi kan sa ya san rabuwarsu ba abu bane mai sauƙi. Nanna idon manya ta saka musu suna bidirinsu tana addu'a a gefe. Fatanta yadda suke yanzu kada ya kama ƙafar yadda zasu kasance duk ranar da suka ɗora ido akan juna. Wani saƙon ya sake turowa wanda yasa ta bashi amsar dole.

(Ina fata dawowar Brother Shaheed ba za ta shafi Karam1 ba?)

Baya saka suna saboda gudun ɓacin rana kada wayar ta faɗa hannun da ba nata ba.

(Kanwar Jamal, Tosin ɗin Shaheed, Tauhidat ɗin Nanna, Cuddles ɗin Doctor. A ciki babu wanda ya taba ta kowa.)

Amsarta har ya kwanta a ranar ita zuciyarsa take karantawa. Cuddles ɗin Doctor. How he can't wait to cuddle her!

***

Bayan fitarsu daga gida Alh. Audi ya kira matansa ɗakinsa. Babu wadda ta san me yake ƙullawa tun jiya. Sun dai ga yana yawan waya da wani daga office ɗinsu wanda ya baiwa ragamar ganin kammaluwar shirin da ya yi wa yau ɗin. Dama yana ta addu'ar kada Haj. Manga ta yi shigen abinda ya yi niyya domin hakan zai ɓata masa wasa sai gashi kuwa ko kusa bai ga alama ba. Yau zai ƙara kusanto da iyalin Abayomi gareshi domin ya samu kan Tauhidat cikin sauƙi. Yana da yaƙini kan talaka da zuri'arsa babu abinda za ka yaƙe su dashi cikin sauƙi kamar kuɗi da kuma jansu a jiki. Ita ma Haj. Mangan ya fahimci kuɗinta ne ya ɗauresu gareta.

Kaya ne a leda ya miƙa musu. A ledar Fanna guda uku ne, ɗaya nata wani irin lace da bata taɓa gani ba a ɗinke sai na yaranta iri ɗaya shi ma mai matuƙar kyau. Iri ɗaya ne da na Haj. Manga da ta buɗe nata sannan kayan Tauhidat babu bambanci da na su Kulsum sai a mayafi da jaka da takalmi. A take tasha jinin jikinta da cewa akwai abinda zai biyu baya

mara daɗi. Alh. Audi bai bata kunya ba kuwa. Wani shegen murmushin ya yi kawai saboda jindaɗin yanayin da ya gani a fuskarta na fargabar me zai biyo baya. Sai da Papa Abayomi ya shigo ya miƙa masa tasa ledar sannan ya faɗa musu shirin nasa.

"Duk wani mazaunin gidan nan ba zai rasa jin labarin babban ɗan Hafsatu ba da na kai karatu UK ba." Ya ja gwauron numfashi kansa na yawo hagu da dama irin na masu alhini "to yaro dai tamkar ɓatan allura an neme shi an rasa ba amo ba labari. Saboda haka na kasa cewa zan kai Jamal. Idan na yi haka ma sai duniya ta zargeni da raba uwa da ɣaɣanta."

Fanna ta gyaɗa kai "Wannan gaskiya ne Alhaji. Ta wannan fannin ni kaina ina jinjinawa Hajiya. To amma Shamsu kuma fa?"

Karya ya yanko musu Haj. Manga tana kallonsa, ko kunya babu ya ce wai ba lafiya ce ta ishe shi ba. Fanna da bata shiru ta ware murya tana tambayar cutar da take damun Shamsun suna matsayin matansa basu da labari. Da yake ɗan duniya ne sai ya bagarar da zancen.

"Yanzu ba maganarsu ake yi ba. Shaheed ya dawo cikin ikon Allah da sakamako mai kyau. Domin taya mahaifinsa farinciki Hajiya sai kiyi haƙuri na muku karambani. Surprise party na shirya masa da ƙarfe bakwai na dare."

Yadda yake maganar duk mai hankali ya san ba da zuciya ɗaya bane. Sai nanatawa yake ai ɗa na kowa ne. Wannan magana ya yi ta lugwigwitawa kamar mangwaro a hannun yara, har zuwa lokacin da ya ji muryar Shaheed da Tauhidat suna sallama. Daga nan ga mamakin duka mazauna falon sai cewa ya yi,

"Abayomi na sani sarai tamkar bawa kake ga Hajiya sai abinda ta ce. Amma ka sani ba zaman kanta take yi ba. Saboda haka na gama magana kowa ya shirya ana sallah za mu wuce venue ɗin."

Fuskokin ɣaɣan mutumin da aka kira bawanta domin cin zarafi ta fara kallo, kafin ita da su duka su raka Alh. Audi da idanu. Jikinta ya yi mata nauyi da sanyi ganin irin kallon da Shaheed yake mata. Wane ɗa ne zai so a kira mahaifinsa bawa a zamanin da babu bauta? Ledar kayan da ya bata ta ɗauka ta yi sama batare da ta tankawa kowa ba. Tauhidat na ganin haka tabi bayanta da sauri. Fanna ma dai a saɓule ta tashi tana

kawo tunani barkatai a ƙwaƙwalwarta da zai sa maigidan nasu wannan furuci a gaɓar da bata dace ba.

Papa Abayomi da aka yi domin a nunawa yayansa cewa shi ɗin wulaƙantacce ne a gaban uwarɗakinsa, bai tsaya ba ya kama hannun Shaheed suka fita zuwa ɓangarensu. Muryarsa a kausashe saboda ya ga irin kallon da ɗan nasa ya yiwa Haj. Manga ya soma magana da yarbanci.

"Aderemi Shaheed Abayomi waye ya kawoka gidannan?"

Ɗan jim ya yi kafin ya ce,

"Nanna ce."

"Yauwa na ji daɗi da baka manta ba. Ina so ka riƙe a ranka cewa kuɗi ko wani ƙyale-ƙyale da wani zai nuna maka kada ya canja maka tunani a kanta. Mace ce mai matuƙar kirki da hangen nesa. Ban san meye tsakaninta da mijinta ba amma ban yarda ka canja mu'amalarka da ita ba akan abinda kaji ɗazu kana jina?"

Sakin fuska ya yi domin kwantarwa da mahaifinsa hankali duk da wasi-wasin da yake masa kai kawo a zuci ya ce,

"Na ji Papa kuma zan kiyaye."

Murmushi Abayomi ya yi shi ma ya rungume ɗansa, yana mai farinciki da dawowarsa. Tarin kayan abincin da ta aiko musu ya nuna masa da kuma kuɗi dubu ɗari wanda ta ce su tafi Abeokuta cikin dangi ayi walimar gama karatunsa lafiya. A ranar da ta bashi kuɗin tana ta nanata masa kada a wuce sati da Tauhidat tunda an koma makaranta. Dan abinda Shaheed ya riƙe a ransa sai ya nema ya rasa. Ba wai kuɗin bane ya sauya masa ra'ayi, ko kusa, mutuntawa ga mahaifinsa ya fiye masa komai.

Haj. Manga kuwa ɗaki ta shiga ta kwanta, zuciyarta tana tafarfasa. A yanzu da ta ga Arƙam shi ne daidai lokacin da ya kamata ta nemi Alh. Audi ya sahale mata wannan aure da suna kawai ya tara. Ya rabata da Madam Zainaba bata fatan ya yi nasara akan su Tauhidat. Tana cikin tunanin bata ji shigowarta ba sai kwanciya da ta yi a bayanta ta saƙala hannu ta rungumota yadda take yi da ƙuruciya. Tana ji lokacin da ta

kama hannuwan ta riƙe sosai a cikin nata masu ɗumi. Cikin ƙanƙanuwar murya ta ce,

"Nanna kada ki yi kuka. Idan ki ka yi kuka za a gane, idan aka gane kuma anyi nasara a kanki."

Da sauri Haj. Manga ta tashi zaune ta tambayeta dalilin faɗin haka.

"Saboda bana so kowa ya raina min uwa."

Ita ce amsar da Tauhidat ta bata Rungume juna kawai suka yi, wani abin ba sai an fada ba. Allah ne Ya amintar da zukatansu suka zama wani bangare mai mahimmanci ga juna.

***

Taro ya kasance fiye da zato da tsammaninsu. Alh. Audi amfani ya yi da dawowar Shaheed wurin ɗaga martabarsa a idanun al'umma. Ya aikawa yan uwan Abayomi da na matarsa ashe kwanansu ɗaya su goma sha uku a guest house ɗinsa bai sanar da kowa ba. Su ma kuma ya nuna musu ba ya son Abayomi ya sani ne saboda haka suka yi shiru. Wannan kirki nasa da suka gani yasa suka ɗaukake shi da girman daraja. Ga abokansa da Alh. Ari wanda ya bayar da shawarar yin wannan taro.

Yadda ya ɗinkawa kowa leshi domin dacewa da taron yarbawa shi ma haka ya saka nasa da babbar riga da hular kayan ya karkata. Gefe ɗaya kuma ga yan jaridar da Alh. Ari ya ɗebo ana ta ɗaukar hotuna da video an yiwa taron laƙabi da Karamcin Karam. Mutane suna ganin wane mai arziƙin ne zai yiwa ɗan direban matarsa abu irin wannan. Don gwaninta ya haɗa yayansa da na direba ya yi musu kaya iri ɗaya don ya nunawa duniya cewa babu bambanci tsakaninsu. Sun dai bi yarima sun sha kiɗa ko ba komai zuwan kawunnai da gwaggwanninsu ya faranta zuƙatansu. Haj. Manga sai ta shige cikin taron ta saki ranta sosai, abinda ya tunzura zuciyar Baba Audi. A can gefe Shamsu ya tsaya yana mai takaicin haɗa shi da wannan taron matsiyatan kamar yadda ya karantawa zuciyarsa. Da gayya Alh. Ari ke tambayar Alh. Audi wai ina Jamal shi kuma ya wani karkata kai yana cewa ayi sha'ani kawai. Waɗanda suka san mashayi ne ɗan ƙwaya suka dasa faifansa ana ta bawa yan rahoto kanun labarai a fakaice. Bayan taron ya watse sai su da yan uwansu Haj. Manga ta zauna cikinsu ana ta hira da raha. Alh. Audi bai daddara ba ya taho inda suke Fanna tana mara masa baya. Bayerabe akwai

girmama mai kyautata masa. Nan fa suka shiga yi masa godiya da fatan alkhairi akan ɗawainiya da ɗansu. Ya murmusa yana duban Abayomi,

"Duka yi wa kai ne saboda mun riga mun zama ɗaya. Na so Hajjin bana ma ayi da kai to amma sai na tuna yadda uwarɗakin naka ta ɓata rai lokacin da na ce zan tura Shaheed Turkey karatu."

Ba ɓata lokaci wurin ya kaure da ƙananun maganganu. Masu jin turancin cikinsu suna fassarawa sauran. Idanu suka yi caaa akan Haj. Manga. Tauhidat ta kalla wadda ta ɗage mata gira irin na muna da namu makamin, ta saki murmushi sannan ta ce,

"Alhaji mungode sosai amma kada ka damu. Maganar Hajji in sha Allahu ana fara ɗiban Alhazai za ka ji sunan Alhaji Abayomi."

Fanna bata iya ɓoye farincikinta na ganin wannan karon bai sami damar tozarta kishiyarta ba. Ba wai zaman dadi suke yi ba, amma ta gama gane cewa akwai ta inda Alhajin nasu yake tauye Haj. Manga wanda shi ne dalilin shigowarta gidan. Sauran mutanen hadda Shaheed aka shiga yi mata addu'a suna yaba kyautatawarta garesu. Kwafa Alh. Audi ya yi a zuci ya bar wurin da murmushin yaƙe. Yana isa gaban motarsa Haj. Manga tana isowa. Kallonsa take ido cikin ido.

"Ina roƙon Allah Yasa ba takalmin kaza ne tsakanina da kai ba, domin na ji daɗin rangaɗa guɗa ranar da za ka ciji yatsa."

A fusace ya ce,

"me kike nufi?"

"Ina nufin Allah Yana sane dani da yayana a duk inda suke. Mahaifinsu har ya koma ga Allah bai da abokin adawa balle ace ya cutar da wani. Nayi imani cewa da izinin Allah zuri'ar Ibrahim ba za ta wulaƙanta ba duniya da lahira."

***

A kwana a tashi rayuwa tana jujjuyawa da ɗan Adam. Yau fari gobe tsumma haka maikuɗi da talaka suke tashi. Papa Abayomi yaje Hajji tare da wasu cikin yan uwansa da suka tashi a wannan shekarar. Ta garinsu ta biya masa dama saboda tafiya irin wannan tafi daɗi da idon sani. A cikin lokacin

kamar yadda ta alƙawartawa Arƙam bayan wata biyu da yan kwanaki suka haɗu a England saboda kada Alh. Audi ya zargi komai. Hutu kawai ta ce masa za ta ya ce Allah Ya kiyaye hanya. Zaman nasu ya ƙara muni ya kuma dage akan ba zai saketa ba. Sai ta rabu dashi ta tattara hankalinta wurin aikin makarantar da za a soma gini.

Tafiyar Dada umara domin haɗuwa da jikanta bata yi wu ba, saboda jikin tsufa tana ta rashin lafiya. Haƙura suka yi sai lokacin azumi sannan ta je. Amma yana yawan kiranta su gaisa. A haka Tauhidat ta kammala jarabawar SSCE suka sha murnarsu ita da Nanna. Alƙawarin umara ta yi mata batare da ta faɗa mata Arƙam zai je ba idan ta yi ƙoƙari. Shi ma kuma bata faɗa masa ba, saboda sanin halinsa zai dameta ne ya kuma hana Tauhidat sakat. Yanzun ma sai da ta karɓe wayarta da tana jarabawar. Sai ya ce kira ya yi ya mata fatan alkhairi amma sai an shafe minti goma ko sama da haka ana kus-kus. Nanna kanta rasa me suke cewa take yi. Jamal tara shi kawai yake wai ya musu farraƙu shi da ƙanwarsa.

A can Kano aka sami guda cikin jikokin Dada ya je da dvd ɗin waƙar Arƙam gidansu. Mahaifiyarsa Anti Nana da ta kasance ita ce babba a cikin ƙannen Ibrahim tana ganin kwalin ta gane shi. Hankali a tashe ta kaiwa Dada tana zagin Haj. Manga. A dole ranar Dada ta feɗewa yayanta biri har wutsiya. Babu wanda baiyi Allah wadai da Alh. Audi ba. Suka taru wurin riƙe amanar ɗan uwansu. Biyu a ciki zasu bi Dada zuwa umarar da za ta je domin haɗuwa dashi. Gidan Baffa ma zasu je da Umma matarsa da duka yaysn nasu. Sun san halinsa, ya ja musu kunne sosai akan riƙon sirrin yar uwarsu. Hakama Dada, sun mata alƙawarin kame bakinsu tare da duƙufa wajen yin addu'ar kariya gareshi.

Rana bata ƙarya ance sai dai uwar ɗiya taji kunya. Ranar da aka kai azumi takwas Arƙam ya tashi daga Baltimore zuwa ƙasa mai tsarki. Kwanansa ɗaya da sauka, saboda nisan tafiya a hanya ya kusa kai azumi na tara sannan su Haj. Manga suka taso a ranar da aka ɗauki na goma. Ita da Jamal da Tauhidat da iyalan Baffa sun tashi ta Abuja. Su Dada kuma daga Kano amma duka rana ɗaya.

Alh. Audi yaso zuwa umara a shekarar, amma ƙyashin haɗuwa da zai dinga yi da Baffa Alƙali yasa shi fasawa. Fanna da ta ɗora rigimar son a barta taje da yaranta yasa babanta ya sille

masa ita. Wai sun kula Haj. Manga ta wanke ta bata ta sha. To koma dai mene ne su kam abin ya tafi musu a daidai. Zasu tafi cikin kwanciyar hankali.

Murna da ɗoki a wurin Tauhidat ba a cewa komai za ta ga dakin Allah. Ta sake zama yan mata kyawunta mai fisgar hankali ya kuma bayyana. Sirrukan gyaran jiki tun tana ƙwailarta Nanna take koyar da ita saboda Kanuri sun yarda da gyara sosai. Zaman awa biyu suka yi a airport ɗin Jidda har jirginsu Dada ya sauka sannan suka ɗunguma zuga guda zuwa Madinatul Munawwara. Madina garin Manzo SAW.

Gabanin asuba suka isa Coral Al-Madina Hotel inda Arƙam ya yi masauki shi ma. Babu nisa sosai tsakaninsa da Harami (masallacin Annabi SAW). Babban hotel ne mai tsada yaci karo da mutanen da kuɗi ba matsalarsu bane. Kawu Safiyanu shi ne ɗan Dada na uku kuma tare aka zo dashi da Anti Nana. Bai yarda ya shiga aljihun Baffa ko Haj. Manga ba ya kama musu ɗakuna biyu. Ɗaya Dada da Anti Nana sai nasa. Baffa kuma ya kama biyar. Shi da Umma, Haj. Manga da Tauhidat, Jamal tare da baffaninsa a sauran ukun. Sallah suka fara yi sannan aka yi wanka tunda sunyi sahur a hanya. Maimakon bin lafiyar gado haƙarƙari ya huta sai suka ɗunguma zuwa ɗakin Baffa gabaɗayansu banda Tauhidat. Ita dai Nanna ta ce mata za ta je wurinsu Baffa ta yi kwanciyarta sai la'asar zasu je masallaci. Ko motsin kirki bata iyawa saboda gajiya ta kwanta bacci mai nauyi ya ɗauketa.

Kowa na zaune Baffa ya kira Arƙam da lambar wayarsa da ya bashi tun ranar da ya iso. Bai daɗe da dawowa daga masallaci ba lokacin. Ya san ranar zasu iso amma bai san da sassafe ba, kuma bai san adadinsu ba. Yana ganin wayar gabansa ya faɗi, ya riga ya san ko waye. Jikinsa na rawa yau zai ga yan uwa ya fito daga ɗakin zuwa hawa biyu saman nasa inda Baffa ya faɗa masa ɗakinsa yake. A bude ya tarar da ƙofar suna tsatstsaye gabaɗayansu, sallamarsa ta ratsa kunnuwansu.

Dada ya fara nema da ido ya yi sa'ar ganinta a kusa da Umman Baffa. Allah Ya sani zuciyarsa ta karye fiye da yadda zai iya jurewa. Hawayen tsufaffin nan ya ishi Alh. Audi haƙƙi. Haka suka sa Arƙam a tsakiya ana kukan farinciki. Anti Nana da kawunansa babu sunan wanda ya kuskure. Sun ƙara girma akan sanin da ya yi musu kafin ya tafi. Su ma suna mamakin tsayinsa. Ya cika ɗan Haj. Manga duk inda ya gilma ya fi kowa

tsayi. Neman gajiya kowa ya yi ya rasa saboda farinciki. Ba su suka tashi ba sai da aka soma kiran azahar. Mazan suka ɗunguma zuwa Harami, matan suka yi sallolinsu a ɗakunansu. Suna dawowa Jamal ya gudu ɗakin Arƙam. Basu ɗauki lokaci ba kuwa sai bacci.

Uku da kwata Tauhidat ta farka, ta faɗa wanka a gaggauce saboda sallar azahar da ta kufce mata. Tana idarwa suka fara shirin tafiya harami saboda samun la'asar. Don ɗoki ta hana Nanna sukuni. Ta dameta sai da ta shirya lokacin uku da arba'in. Ƙaramin akwatinta da ta saka hijabai da laffaya ta nema ta rasa ashe yana wurin Jamal, saboda shi ya ɗauko mata. Arƙam ta kira tunda ta san suna tare ya bashi ta faɗa masa ya ɗauko mata sannan su shirya su ma su wuce tare. Tauhidat da ta gaji da jiran ta ce ita za ta je ƙofar ɗakin da yake ta ƙwanƙwasa ya bata. Ita so take hatta kiran sallah ayi tana wurin.

Haj. Manga bata hanata zuwa ba, tunda ta san kafin ta isa ɗakin ma ƙila ya ɗauko. Yadda take rawar jikin nan duk abinda zai hanasu fita da wuri zai iya sa ta kuka. Fuskarta babu wata kwalliya sama da hoda da ƙwalli amma ta yi fes da ita. Riga da skirt ne a jikinta na atampa da suka fiddo da yanayin jikinta. Ta ɗaura ɗankwalin sannan ta saka hijab mai hannu da ya zarta gwiwarta kaɗan ruwan ƙasa na wani irin yadi mai kyau mara nauyi. A sama take jin kanta yau gata a Madina. Ta fita ɗauke da murmushin nan nata Haj. Manga tana girgiza kai ita ma tana tayata. Arqam ne ya tafi dauko akwatin saboda Jamal lokacin yake shiryawa. Shirt mai gajeren hannu ce a jikinsa army green ya bar maballai biyun sama a bude ta yadda ake ganin ta ciki light green. Ya karbo akwatin yana bin lambobin sauran ɗakunan da kallo kada ya wuce na Nanna. Ita kuma Tauhidat ta karyo kwana daga bangaren dakin nasu za ta je inda a saninta nan Jamal yake. Duk tsirarun mutane masu wucewa ta wurin hankulansu gabadaya suna kan abinda ke gabansu. Kanta a kasa yake har lokacin da taji wani mayataccen kamshin turare mai dadi. Daurewa ta yi bata kalli mai fitar da ƙamshin ba lokacin da suka gilma juna. Arqam da bai da dabi'ar kallo sau daya ya kalleta ya dauke kansa. Sai dai yana dauke idanun ya dawo dasu da sauri ya bi bayanta zuciyarsa na wani irin bugu. Bata ankara ba ta ga mutum a gabanta. Dago dara-daran idanuwanta ta yi suka sauka a cikin

nasa. A hankali, cikin nutsuwa, kamar yana tsoron yin kuskure ya ce,

"Cuddles?"

Yadda idanunta suka ƙara girma akan idonsa, da hannun da ta ɗora akan bakinta don kada ta yi ihun mamaki da murna ne suka tabbatar masa da cewa ita ɗin ce.

"Kece da gaske? My God, I can't believe Nanna"

Wannan karon da ƙwarin gwiwarsa ya faɗa. Fuskarsa na fitar da annurin farincikin da yake lulluɓe a zuciyarsa. Ita dai tunda ta ƙare masa kallo sau ɗaya, ta haɗiyi wani yawu bata san lokacin da ta juya da sauri ta bar wurin ba. Yanzu wannan mutumin ne Arƙam ɗin da take waya dashi? Rashin sanin yadda za ta kwatanta haibarsa da cikar zatti ya sa taji ƙafafunta sun gagara ɗaukarta. A wurin ya bar akwatin Nanna yabi bayanta da sauri yana kiranta. Kafin ya taddota ta buɗe ƙofar da gudu ta shige bayan Nanna dake zaune akan kujerar ɓangaren da yake kamar falo a ɗakin ta ɓuya.

"Ke lafiyarki?" Ta tambayeta ganin tana faman cukwikuyeta.

Ɗago kai ta yi ta kafaɗarta tana mayar da numfashi da sauri,

"Nanna na ganshi?"

"Shi wa?" Ta yi kamar bata gane ba.

Daga bakin ƙofar ɗakin taji muryarsa,

"Arƙam, kuma ta gudu."

Sake ɓuyewa ta yi. Haj. Manga tana dariya za ta tashi taji ta riƙeta da kyau.

"Yanzu banda abinki Tauhida meye abin gudu? Mutumin da ku ke cika mana kunne da surutunku a waya ki ke ɓoyewa?"

Da ƙyar ta iya sauko da ƙafafunta kasa, amma taƙi dago kai ta kalle shi, "kunya naji ne wallahi."

'Kamar kin ga suruki? Ni ina akwatin ko babu wanda ya ɗauko cikinku?"

Sai lokacin Arƙam ya sake yin magana. Sauraron muryar Tauhidat daga kurkusa haka kuma yana kallonta ya ɗauke masa hankali.

"Shit" ya furta a hankali yana juyawa "Cud..."

Kafin ya ƙarasa ta ɗago da sauri ta danna masa wata harara. Ko ita dashi a waya kunyar sunan take yi balle a gaban mahaifiyarsa. Murmushi ya yi mai sauti, "ba kya so Nanna ta ji? To taso muje ki tayani neman akwatin."

Tafa hannuwa kawai Haj. Manga take yi tana cewa da alama dai sai sun rasa sallah. A ƙasan zuciyarta kuwa kamar sallar Idi. Fita suka yi hannuwan Tauhidat duka biyun ta rufe fuska dasu tana murmushi.

"Ki cire na ganki don Allah."

Hannu ɗaya ta cire ya zuba mata idanu an rasa mai magana a cikinsu suka ji muryar Jamal. Akwatin da suka fito nema ne a hannunsa ya rike haba da hannu ɗaya.

"A watan azumi da rana tsaka me nake gani ni Jamalu?"

Har lokacin idon Arƙam na kan ta ya ce masa, "ka gani kunyata take ji."

"Ba dole ba, wannan kallo da ka tsareta dashi sai kace budurwarka."

"Wai haka?"

Wayam ya gani tuni ta karɓe akwatin ta gudu. Su huɗu suka tafi masallacin. Dada da Umma sun ce sai washegari. Anti Nana kuma dole ta zauna saboda taimakawa Dadan. Mazan ne dai sun jima da tafiya su ma sai taxi suka nema gudun lattin. Karatu suka zauna yi bayan an idar da sallah. Tun a nan Tauhidat take ta kwararawa mahaifiyarta, Papa da Nanna addu'o'i. Ba su suka bar masallacin ba sai da aka idar da sallar magrib suka sha ruwa a masallacin. Daga nan suka fito zuwa hotel ɗinsu domin su ci abinci su koma lokacin isha da taraweeh. Ita da Nanna ɗakinsu suka wuce jiran Arƙam da Jamal su karɓo musu abinci a wani restaurant da yake gefen hotel ɗin. Snacks da abinci da abin sha suka siyo. Komai an jera a tsakiyar falon suka zauna zagaye kowa yaja nasa abincin. Tauhidat ta takure ta kasa ci saboda Arƙam ba dai takura ba. Kai tsaya yake abubuwa abinsa. Ya raba kazarsa biyu ya ɗora mata a plate ɗinta, yazo ya tura mata samosa da doughnut. Gajiya ya yi da ganin yadda take tsakura kamar bata so yace,

"Abincin babu daɗi ne? Na siyo miki wani?"

"La'ilaha illahu! Ta ina za ta ci abincin har ta gane ko da daɗi ka dameta. Ni ku tashi ku koma ɗakinku. Ina dalili ku zo har makwancinta ku hanata sakewa."

"Aahh Nanna ki ware mai laifi shi kaɗai banda jama'u." Cewar Jamal ya cika baki da shinkafa.

Kan Arqam ne ya ɗaure don bai ga ta inda ya kuskure ba ya marairaice fuska, "me nayi? Cu..."

"Ya isa zan ci, zan ci"

Tauhidat ta cika cokali ta danna a bakinta. Haj. Manga da Jamal suka fara cewa sai an faɗa musu me ake ƙoyewa. Ita dai abinci take turawa babu bakin magana. Su uku suka tashi Haj. Manga ta ce su je ɗakinsu Dada yi musu barka da shan ruwa. Idan ta gama cin abincin ta same su can sai su koma masallaci. Jamal ya ce ta taho da jaka sai ta sako sauran snacks ɗin zai ci idan yaji yunwa kafin su dawo. A can suka samu Umma ita ma tare dasu tasha ruwa. Sun zauna ana taƙa hira Arƙam ya miƙe.

"Dawo ka zauna" Haj. Manga ta ce fuska babu alamun wasa. Ta san inda zai je ko bai faɗa ba.

Anti Nana ce ta bata amsa da cewa, "Ki ka san uzurinsa za ki hana shi fita kamar wani yaro. Babban likita tashi abinka ka ji."

Ya miƙe kuwa kafin ma a kuma dawo da shi ya yi waje yana jiyo dariyar shaƙiyancin Jamal. A bakin ƙofar ɗakin ya tsaya, ta waje ya jingina bayansa da bango yana jiran fitowar Tauhidat. Ya kusa minti shabiyar kafin ya ji ta buɗe cikin nutsuwa ta fito. Ji ta yi kamar ta koma da suka haɗa ido ya rigata sake kulle ƙofar yana murza ɗan mukullin.

"Meye haka ne Cuddles duk kin takura min?"

"Ni ce ma na takura maka?" Ta ce tana dariyar hausarsa da kullum take a bauɗe.

"Eh mana. Ko magana kin kasa yi min." Yadda ta juya bakinta ya shagaltar da shi, wajen kallo tana magana yana lumshe idanu.

"Haka ne takura?"

Tafiya suka soma gefe da gefe ya karƀe abin sallar da ta ɗebo musu ita da Nanna guda biyu. Ya rataya a hannunsa,

"To me zan ce? Kin takura kanki saboda kin ganni kamar ba ki yi murna ba."

Sai da ta shagwaɓe fuska ba tare da niyya ba ta bashi amsa da cewa,

"Allah na yi."

"Ban ga alama ba. Nafi son Cuddles ɗina ta waya. Wannan ina jin ƙanwar Jamal ce."

Ta yi dariya,

"Kaci sa'a ba ƙanwar Tarantula bace da ka gudu da kanka"

"Amma me ya hanaki kula ni? Na ji haushi fa. Hmmm."

Rasa kalmar da za ta kwatanta shi ta yi, sai kawai ta yi wannan murmushin nata bai bayyana siririyar wushiryarta.

Dan tunani ya yi ya ce "How old are you?"

"Ba na faɗa maka ranar birthday ɗina ba?"

"Amma ki ka ɓoye shekarun ba."

Ya dage gira yana kallonta yar ƙarama a gefensa.

"18 zan yi fa."

"What? Cuddles you are such a baby. I can't believe am this crazy for..." bai ƙarasa ba suka ji muryar Haj. Manga tana cewa shanyar tasu ta bushe. Ta ga alama ishar ma a gurguje suke son su isa masallaci. Dole hirar ta katse ba don suna so ba. Tare da Anti Nana suka tafi wannan karon. Kafin su isa masallaci Arƙam da Tauhidat sun sake ɗinkewa. Jamal ne ya dawo da baya ya shiga tsakaninsu. Arƙam sai ya dawo gefen Tauhidat shi kuma Jamal ya sake rabasu. Tana ta yi musu dariya ta hanzarta komawa gaba gefen Nanna ta barsu.

Kwanakin da suka yi a Madina idan kowa zai manta dasu banda Arƙam, Tauhidat da Haj. Nanna. Duk wani motsinsu a kan idonta tana kallo tana jiran ranar da zasu fitowa da juna sirrin zukatansu. Arqam ba karamin so yake yiwa 'yar gaban goshin Nanna ba. Abin nasa ya hade da yanayin wurin da ya tashi sai ya zamana ba ya jin kunyar nuna mata kulawa a gaban iyayen nasu. A haka ma don Haj. Manga na taka masa burki ne da abin sai yafi haka. A ɓangaren Tauhidat yadda soyayyarsa ta mata shigar sauri haka sabo dashi ya yi mata.

Tare suke tafiya masallaci kullum su dawo tare. Babu wata hirar soyayya a tsakaninsu amma sun san komai game da juna. Ranar da ta bashi labarin ƙwan da Susu ta turata yi a ƙasan gado ya jima rai a ßace. Sai ta dawo bashi labarin Mammalo da mutan China. Da ƙyar ta kai ƙarshen labarin saboda dariyar da take yi. Motoci biyu suka yi bus zuwa Mikati domin ɗaukar haramar gabatar da Umra. Kowa ya fito cikin haraminsa suna ta talbiyya har suka isa Makka. Sun riga sun kama ɗakunan hotel ta yanar gizo saboda haka kaya kawai suka ajiye aka ɗunguma zuwa Masjidul Haram. Nan ma da addu'a suka shiga cikin wurin da yake ƙarshen ni'ima da haske a zuciyar mai imani. Tauhidat sai da ta zubar da ƙwalla saboda tsabar farinciki.

A tare ƙungiyarsu take, saboda akwai cunkuso kada wani ya ßata suka fara dawafi. Kowa yana kai kukansa wurin da za a share masa hawaye a ƙara masa da fiye da abinda ya roƙa. Bayan sun gama suka gabatar da nafila raka'a bibbiyu a bayan Mukam Ibrahim sannan aka wuce yin Sa'ayi (tafiya tsakanin Safa da Marwa). Cikin dare suka kammala kowa ya gaji aka koma masauki. Kafin su kwanta sai da aka cike ibadar da aski mazansu da matansu kowa ya yanke gwargwadon abinda shari'a ta lamunce masa.

Washegari sai ga Arƙam da Jamal da huluna irin wadanda ake kira tashi ka fiye naci. Kwalƙwalin da Baffa ya ce lallai shi zasu yi ba saisaye ba suke rufewa. Sun fito tafiya masallaci Tauhidat ta gansu. Maganar da tayi ce tasa su rige-rigen cire hular. Inda ta ce da ace mata an halatta musu buɗe kai da ta nunawa duniya nata kan don kowa ya san cewa Allah Ya albarkaceta da yin umra. Baffa da Kawu Safiyanu suna wurin sai duka suka ji ta matuƙar burgesu.

Azumi yana kwana ashirin da bakwai Arƙam ya gama tada hankalinsa akan yadda zai koma Baltimore shi kaɗai. Bashi da wata walwalar kirki sai ta zuwa masallaci. Tare yake tafiya da Tauhidat su wuni kowa na nasa bangaren yana ibada, sai lokacin tafiya su haɗu. Ita ma duk ta yi sukuku har tausayinsu Haj. Manga take ji. Sabo abu ne mai tsayuwa da cin rai. Daren jiya sai da ta yi kuka bayan ya fita daga ɗakinsu. Idanunsa jajur yake roƙon mahaifiyarsa akan ta barshi ya bisu sai ya zauna a Kano kafin hutunsa ya ƙare.

"Arƙam kafi kowa sanin cewa ni ma ba don daɗi na barka kai kaɗai ba. Kana kallo na rasa da yadda zan yi na raba kaina da auren mutumin nan. Ga Jamal ko ɗazu ka ga irin turarrukan da ya saya masa wai shi mai uba. So kake yi kai da Allah Ya tseratar na ɗauka na damƙa masa?"

Tashi Tauhidat ta yi za ta bar musu ɗakin saboda da farko hirar ba irin wannan bace. Yanzu kuwa ta fuskanci suna buƙatar ganawa cikin sirri. Ta kusa kaiwa bakin ƙofa ya daka mata tsawa, "koma ki zauna. Cuddles ba za ki iya tayani roƙonta ba shi ne zaki fita ko?"

A gigice ta fashe da kuka saboda dama yanayinsa ya bata tausayi ga kuma tsawar da ta tayar mata da hankali. Ya kuwa taɓowa kansa don Haj. Manga bata masa da daɗi ba. Faɗa ta hau shi dashi akan me zai saka mata ya kuka.

"Nanna ki dena masa faɗa ba don shi nake kukan ba. Kin gani na dena." Ta goge hawayen da sauri duk ta cabe gaban mayafin pashmina da ta yafa akan abayar jikinta.

"Ji min sakarci. Ya saka ki kuka kuma kina kare masa." Shi ma da kukan nata ya ɗaga masa hankali sai ya koma bata haƙuri.

"Zo na raka ki inda zaki je."

"Na fasa"

Ransa ƙara baci ya yi sai ka rantse kuka yake shirin yi ya ce, "Nanna kin ganta ko? Bata ma tunanin zamu daɗe bamu haɗu ba take min haka."

Tausayinsu duka taji ta saki fuska,

"Tashi kije ya saya miki ice cream kafin mu sauko. Ina son yin ɗawafi kafin a fara ƙiyamul laili da wuri zamu tafi yau. Kuma kada ki raga masa. Ki ɗauki duk abinda ki ke so."

Fita suka yi aka rasa mai kula ɗan uwansa. Jamal ya haɗu dasu a wurin lift, ya soma tsokanarsu ya ga babu fuska sai ya wuce yana cewa faɗan masoya hutu ne. Wurin Haj. Manga yaje ta faɗa masa dalilin rigimar.

"Ni fa idan ba Arƙam ba gaskiya ban ga wanda zan bawa ƙanwata ba. Tunda ni na amince ina ga kawai ayi komai a wuce wurin ni ma ki ji da ni."

Pillow ta jefa masa tana cewa waye zai aure shi yaƙi maida hankali akan komai sai shiririta. Bacci taso yi kafin lokacin zuwansu masallaci amma ya addabeta da zance dole ta haƙura.

Arƙam da Tauhidat na tsaye suna jiran a miƙo ice cream ɗin da ya saya mata na roba har lokacin sun ƙi kula juna. Godiyar da ta yi masa da ya miƙa mata ce ta kawo ƙarshen shirun.

"Dazu kinyi magana da Papa?"

"Eh"

"Baki jin komai ace har za ki koma ko sau ɗaya bai taɓa sanin kina tare dani ba?"

Zama suka yi a lobby ɗin hotel ɗinsu sannan ta soma magana tana share hawaye. Tunawa ta yi da abinda ta sani game da gadonsu wanda har yau koda takarda ta kasa rubutawa saboda bala'in asirin dake zagaye da rufuwar wannan sirrin.

"Duk abinda Nanna take yi saboda ta kareka ne. Ni ma ba zan so mu koma wani abu ya sameka ba. Ka manta jiya ta ce next zuwa wurinka dani za ta zo?"

Kwantar da kansa ya yi a jikin kujerar da yake zaune ya miƙe ƙafafunsa tare da ɗora hannu akan goshinsa. Sun kasa fahimtarsa. Ba wai saboda ya matsu da zuwa Nigeria bane. Damuwarsa yadda zai rasa ganin Tauhidat da ta mamaye ko ina a ruhinsa. Tana fara jami'a fa shikenan za ayi ta bashi uzurin tana makaranta aƙi zuwa da ita. Yanzu kuma kamar ta yi ƙanƙanta da aure. Kai anya kuwa?

"Arƙam" ta ambaci sunansa karo na farko a cikin kunnuwansa. Da sauri ya buɗe ido ya gyara zamansa, hadda murmushin da ya yi masa ƙaura kwana biyu,

"uhmm."

"Me kake so Nanna ta yi sai na tayaka roƙonta."

'Ta bani ke', ya ce a zuci yana mai jin nauyin faɗa mata kalmar a zahiri, ba dan komai ba sai dan kada ya ɓata abinda ke tsakaninsu. Dole ya nema musu mafita kafin zuciyarsa da bata taɓa sanin soyayya ba ta buga akan ta.

Washegari Jamal ya ƙara tunzura shi. Dama yaya lafiyar kura? Ya san damuwar yayan nasa da Tauhidat. Abinda ya fuskanta shi ne kamar Arƙam bai wani goge ta fannin wayewa da sanin

soyayya ba. Abu na cin sa a rai amma ya kasa fitar dashi ya ji sauƙi. Ita kuma Tauhidat ya tabbatar ko zai sammata codein ba za ta taɓa fara cewa tana son Arƙam ba. Dawowarsu kenan gida zasu dan kwanta kafin su tafi masallaci ya taɓo ɗan uwan nasa.

"Bana za a kwashi Jambitos. Fatana dai na makarantarmu su zama kyawawa. Yan Gwags kam zasu more da su Tauhidat."

Babu wata kalma da Arƙam ya fahimta a zancen don jinsa yake kamar baƙon yare.

"Meye Jambitos kuma?"

Jamal ya ware idona kamar gaske, "kai fa baka san komai ba a ƙasarmu. Jambito na nufin fresh babes daga secondary school masu shiga level one."

Ba shiri Arƙam ya tashi zaune, "matan kawai banda maza?"

"Eh to hadda mazan amma ka san mu yan matan muke jira."

"Kuyi musu me?" Arqam ya tambaya hankalinsa ya fara komawa kan Tauhidat. Yanayin fuskarsa sai da ya kusa sa Jamal dariya. Ya dai daure don ya fuskanci idan bai ɗora shi a hanya ba haka zai ta zama ciwon so na nuƙurƙusarsa.

"Ka ga kamar ni da friends ɗina 'yan level one na shigowa muke sake yan mata. Ni dai iyakata na kashewa yarinya kuɗi amma irinsu Manniru kuwa ba a cewa komai."

An taɓo maza, a fusace Arƙam ya ce, "indirectly you are trying to say wani zai yi Jambitos da Cuddles ko?"

"Yes! Maganar gaskiya irinsu Tauhidat ne masu haɗa goslow ayi ta rigima tsakanin malamai da ɗalibai."

"Allah Ya kiyaye. Ayi da wasu dai ba ita ba" ya tashi ya bar ɗakin a fusace. Jamal ya gyara kwanciyarsa yana cewa idan an haihu ayi masa takwara.

***

Wajen shaɗaya na safe washegari Arƙam ya je ya gaishe da kakaninsa da iyaye. A ɗakin su Dada ya tarar da Haj. Manga ya tambayeta Tauhidat ta ce masa ta tafi masallaci yi wa mahaifiyarta ɗawafi. Tare suka saba tafiya sai yaji ya damu yana kokwonton kada taƙi soyayyarsa. Zama ya yi a ɗakin har

Haj. Manga ta tashi komawa nata. Suna shiga ya ɗauko maganar da ko kusa bata yi mamaki ba.

"Nanna don Allah ki bani Tauhida." Ya ce cikin yanayin tashin hankali da ban tausayi. Maganar Jamal ta jiya ko sahur bata barshi ya yi ba saboda damuwa. Zama tayi a kusa dashi ta riƙe hannunsa.

"Arƙam Tauhida ba kaya bace, idan kana son yata ka nemi soyayyarta."

"Idan taƙi amincewa fa?"

"Sai ka haƙura."

"I can't. To ki faɗa mata idan ta dawo." Ya soma yi mata magiya.

"Kana nan da tsoron mata ashe. Ka yi ƙoƙari ka faɗa mata kafin mu bar ƙasar nan. In sha Allahu za ta amince."

Yadda ya ga ta nuna masa farincikinta, ya ƙara masa ƙwarin gwuiwa sosai. Alƙawari ta yi masa cewa idan sun daidaita kansu tana komawa za ta turo masa takardunta ya nema mata admission a garin da yake. Su Baffa da kawunnansa na wurin uba zasu nema masa aurenta a wurin mahaifinta. Bai bar ɗakin ba suna ta shawarar yadda zasu gabatar da komai. Sharaɗi dai ta bashi cewa babu abinda za ta yi masa ba tare da amincewar Tauhida ba. Ranar da aka kai azumi ashirin da tara watan shawwal ya bayyana. Washegari ranar sallah ta zama babbar rana ga Haj. Manga da yayanta da duk mai ƙaunarsu. Sallah ce irin wadda suka daɗe rabonsu da ita. Yawo suka fice zaga wuraren tarihi a ƙasar har dare. Hotuna kuwa anyi ba iyaka.

Sallah da kwana biyu Arƙam zai koma su kuma sai da kwana huɗu. Ana gobe zai tafi kusan babu wanda ya yi bacci. Suna tare family gabaɗaya ana ta hira. Tauhidat ce kawai ta fake da gajiya don ta basu damar kaɗaicewa. Bayan fitarta Baffa ya ce da Haj. Manga,

"Hafsatu yarinyar nan kinyi mata kyakkyawar tarbiya. Wallahi ɗabi'unta suna burgeni sosai."

"Baffa ɗorawa na yi, Allah Ya jiƙan mahaifiyarta ita ta ɗora yayanta akan kyakkyawar turba."

Anti Nana ta murmusa "ina ta zuba ido ko za ayi yar gida da yar nan taki naji shiru. Shaƙuwarsu ta yi yawan da nake tausayin rabuwarsu."

Umma ta karɓe da cewa yau kukan Tauhidat ya kai huɗu, saboda tsokanarsu da Jamal yake yi. Shikenan fa hira ta koma kan Arƙam da Tauhidat. Iyaye da suka shiga bashi ƙwarin gwuiwa akan kada ya bari gobe ta wuce bai nemi sun daidaita ba. Kunya ta sa shi barin ɗakin. Har mamaki suke yadda mawaƙi kamarsa mai mu'amala da mutane daban-daban ya gagara sanar da yarinyar da ko ba a faɗa ba an san tana son shi ita ma. Sai ƙarfe biyar zasu tafi raka shi Jidda washegari saboda jirgin dare zai bi. Tun da Tauhidat ta tashi fuskarta babu fara'a. Motsi kaɗan sai kuka har ya shigo ɗakin tare da Jamal. Ganin yana ta jan ta da tsokana taƙi biyewa yasa Jamal tambayar me yake damunta. Bata iya cewa komai ba sai wasu sababbin hawayen. Kan ta ta ɗora a cinyar Nanna tana kuka sosai.

"Tauhida don Allah ki faɗa min abinda ke damunki. Ko baki da lafiya ne?" Haj. Manga ta tambayeta.

"Zazzaɓi nake da ciwon kai" ta ce tana fashewa da wani kukan. Arƙam kallonta kawai yake yi yana jin kamar ya janyota jikinsa.

"Ke da ki ke da likita a hannu har kya yi kukan ciwo? Dr. Arƙam Jambito is sick." Inji Jamal.

Murmushin dole ya yi ba don yaso ba. Jamal ba ya rabo da neman tsokana. Sai da ya je bakin ƙofa sannan ya ce, "Cuddles zo."

"Wannan suna wai ina ina aka raɗa shi?" Haj. Manga ta ce tana kallon bayan Arƙam.

"Kashhh, Nanna shiru ake yi. Wannan suna baya buƙatar fassara."

"Au to, ke Cuddles tashi kafin ya dawo don yau ko gyambo bai kai shi zafi ba." Ta ɗago mata kai daga cinyarta tana murmushi, "maza jeki ku yi sallama."

A bakin ƙofar ɗakin suka haɗu ya yi gaba ta bishi suka shiga lift. Da suka sauko ƙasa taxi ya nema tana baya yana gaba. Sunyi tafiya mai ɗan nisa ya juyo, "me ki ke so na saya miki?"

"Babu komai, kace ya juya mu koma." Ta share hawaye da bayan hannu. Zuciyarsa na kusa dama "Ya kike so nayi miki ne? Ba hadda ke ake supporting kada na biku Nigeria ba. Kukan na meye kuma?"

Ta kwaɓe masa fuska kuwa tare da fashewa da kuka, "ba kaine ka ke min faɗa ba."

Direban Taxi ɗin ya nunawa wani babban shopping mall a tsallaken titi ya ce ya saukesu a nan. Ɓangaren wurin wasu kujera ya kaita suka zauna.

"Kina so na tayaki kukan ne?" Ta girgiza kai.

"To ki dena kinji. Na dena faɗan. Ban san meye yake damuna ba. Gani nake kamar idan kun tafi ba zan sake ganinki ba."

"Zan zo, Nanna ta ce za ta zo dani." Ta bashi amsa da sauri cike da kafin gwiwa.

Gashi dai kuka take masa amma wani irin son ta yake ji yana ƙara yiwa zuciyarsa kyakkyawan kamu. Kallon cikin idanunta ya yi ya saki maganar da yake ta dako a ransa.

"I love you so much Tauhidah. I don’t even want to imagine life without you (bama na son yin tunanin rayuwa babu ke)."

Sai ga ƙayataccen murmushi mai haɗe da tsantsar jin kunya ya mamaye fuskarta. Bai iya yin shiru ba tunda ya faɗi kalmar farkon ya cigaba da fallasa mata zuciyarsa.

"Idan kin amince min muna komawa zan faɗawa Baffa."

Kai ta cusa a tsakanin cinyoyinta yana ta magana tana jinsa taƙi ɗagowa. Sai da ya ce ko bata amince masa bane sannan ta ɗago a hankali.

"Ni ka maidani wurin Nanna."

"Is that a yes?" Ya kafeta da idanu.

Runtse idanunta ta yi ta gyaɗa kai. Arƙam ji ya yi kamar an yaye masa wani duhu daga zuciyarsa. Inama zai samu a ɗaura masa aure da ita daga nan ya tafi da ita. Sun fi awa biyu a mall ɗin yana ta mata siyayya kamar bai san zafin nema ba. Warewa ya yi abinsa yana mata hirar soyayya ita kuma kunya duk ta hanata sakewa. Sai ƙarfe uku suka koma bayan ya

matsa mata sun ci abinci. Jamal ya kira ya hau mata da kayan shi kuma ya ce ɗawafi zai je ya yi idan anyi la'asar ya dawo ya shirya. Tauhidat na jin haka ita ma taƙi sauka daga motar. Jamal ya shiga tsokanarsu don ya ga alamun komai sammakal an daidaita.

Ɗaya daga cikin rigunan da ya saya mata ta saka da zasu tafi airport Jidda. Su Dada an sha kuka tana ta cewa ko da rabon ta sake ganinsa ko babu. Anti Nana ce kaɗai ta bisu da Uncle Kashim autan Baffa. Bayan tafiyarsa Haj. Manga ta shiga ɗaki taci kukanta ta more. Bata jin za ta taɓa yafewa Alh. Audi wannan halin da ya jefa mata iyali.

Da don Arƙam ya sa ta alƙawarin ba za ta yi kuka ba idan zai tafi da Allah kaɗai Ya san irin kukan da Tauhidat za ta yi. Bare da ta ga ya gama checking-in zai wuce wurin boarding. Hawaye take gogewa wani na bin wani. Anti Nana kuwa ta ce kada ya yarda ya wuce sai ya tabbatar ta ga murmushin yar amanar Nanna. Mp3 player ya zaro daga jakar hannunsa suka koma gefe ya bata "saka a kunnenki."

Ta saka earpiece ɗaya za ta saka na biyun ya yi saurin cewa, "wait!...” sannan da mafi dadin muryarsa ya kara da “I love you."

Lumshi ido ta yi da murmushi ya ce, "is that all?"

Ta sunkuyar da kai, "me too."

Ya sake matsowa kusa da ita yana girgiza kai, "is that all?"

Sai da ta kalli gefenta hagu da dama da sauri ta ce, "I love you Arqam."

Kyakkyawan murmushi suka sakarwa juna ya ce "Missing you already"

Sabuwar kwalla ce ta sake cika mata ido ta ce “ Nanna ta ce zata zo dani.”

“Baffa zai yi Magana da Papa, Allah Yasa ya yarda a daura aurenmu kafin lokacin. Zan tura miki text kafin mu tashi, ki yi min reply da wuri kinji.”

Kai ta gyada ya nuna mp3 ɗin "ina fata wakar ta yi miki daɗi. Ke na yi wa sai na koma zan yi a studio. My last song possibly."

Hawaye ta soma yi ya bar wurin ko juyawa bai sake ba saboda raunin da zuciyarsa ta yi. Haka suka rabu zuƙata na begen juna. Kafin jirginsu ya tashi ya kira Nanna ya faɗa mata ta fara shiri. Yadda ta nuna masa tamkar ta fishi murna ya ƙara kwantar masa da hankali. Text din da ya rubuta tun safe ya turawa Tauhidat kafin a fara sanarwar kasha waya wanda fassararsa take kamar haka.

(Me kike so na fara yi miki idan na zo daukarku daga airport a matsayin mata ta?)

Don ta san yana jiran amsa ne kuma ga yanayin rabuwar tasu amma da a fili ya yi tambayar sai dai ya nemi wani bakin ya bashi amsa.

(Duk abinda ka ga ya dace da Cuddles.)

Dama ya san za a rina, bai hakura ba ya sake tura wani (kina so duk wand kuke tare suce bani da kunya Kenan.)

Kusan tuntube taci wurin kallon wayar a tsorace ta rubuta (me zaka yi?)

(Abinda ya dace da Cuddles mana.) Ya tura yana murmushi ya kasha wayar.

***

Kamar yadda suka zo a tafiya ma sai bayan awa biyu da tashin su Dada nasu jirgin ya tashi. Saɓanin yadda suka zo Tauhidat da Jamal na ta zuba surutu yau bata komai sai sauraron waƙar da Arƙam ya yi mata. Baitin da yafi kowanne tsaya mata take son haddacewa sai baya take da shi. Suna sauka su Baffa suka sake bin jirgi zuwa Maiduguri. Papa Abayomi suke sa ran gani yazo ɗaukarsu sai suka ga baƙuwar fuska. Tare da Mammalo suka zo yana ta murnar ganinsu.

"Hajiya hannu da zuwa. Umara Tauhida da Umari Jamal duk hahhannunku."

Babu wanda ya iya amsa masa saboda rashin ganin baban Tauhidat. Jamal ne ya tambaye shi bayan sun fara tafiya, "Ina Papa Abayomi?"

"Iya gida sun fita da Alhaji ne. Da suka dawo ya ɗauko mukulli shi Alhajin sai ya ce ya huta"

"Ka tabbata lafiya yake ko?" Inji Haj. Manga.

"Sumul ƙalau Hajiya." Ya juyo baya yana murmushi "an fa kirani daga Daƙasoye. Yaya Uwani ta sauka an sami Muhammadu. Takwara ta yi min. Ina ta jira ki dawo he in tafi."

Barka suka yi masa amma Haj. Manga jikinta duk wani iri yake yi mata. Da ta ga Tauhidat ta ɗan sake ne ma ta biye musu suna hira har suka isa gida. Suna zuwa Mammalo ya ce su wuce zai shigo da kayan falo sai masu aiki su hau musu dasu. Kananun jakankunansu Tauhidat ta ɗauko tana biye da Nanna har falon ƙasa. Mai gyaran ɓangaren Fanna ce ta tarbesu sannan ta faɗawa Haj. Manga cewa Alhaji yana kiranta a falonsa.

"Jeki ki yi wanka kafin na hawo." Ta ce da Tauhidat.

"Tare ya ce ku je babanta yana ciki hadda kai Jamal."

Nan fa cikinsu duk su biyun ya tsirga da tsoro. Jikin mahaifinta ta tafi da sauri da suka shiga tana mai jin tsoron ko wani abu aka yi masa. Ganin ƙalau yake sai ta juya a kunyace ta gaishe da Alh. Audi da Alh. Ari. Alh. Ari ya washe baki kamar gonar auduga,

"Haj. Manga barkanku da dawowa. Allah Yasa maƙabuliya ce."

"Amin" ta ce fuska a gimtse tana neman wurin zama.

Ya miƙa hannu, "Kafin ki zauna fara bani tukwicina."

"Tukwici kuma? Me aka yi?" Gabanta yana tsananta faɗuwa. Alh. Audi ya kalli yadda jikinta ya yi sanyi ya sakar mata murmushi, "kinga Hafsatu ungo wannan" ya miƙa mata bandir din yan ɗari bibbiyu guda biyu.

"Na meye?"

"Sadakin yarki ne."

Yawu mai ɗaci ne ya tokare mata wuya da ƙyar ta iya cewa, "wacce?"

"Tauhidat mana hahah hahh" ya bata amsa yana dariya kamar ƙosasahen kwaɗo.

"Da wa??" Haj. Manga ta tambaya baki na rawa.

"Shamsu."

Zabura Tauhidat ta yi daga jikin mahaifinta a gigice ta nufi Haj. Manga tana wani irin ƙuntataccen kuka da sautinsa yaƙi

fitowa. Haj. Manga bata san lokacin da ta isa gabansa ta tsaya ba tana nuna shi da yatsa cikin ƙaraji ta ce, "baka isa ba Audi, kana jina? Idan ka isa …."

Kallon rashin damuwa ya bita dashi, "kada ki tsinewa kanki don aikin gama ya gama. Duk wani abin kirki da zan yi wa mutumin nan da iyalinsa sai kin nuna ɓacin rai. To wannan dai an gama!"

Ɗaga hannu tayi kamar ta mare shi Jamal ya riƙeta yana nuna mata Tauhidat dake kokawa da numfashi a jikin Abayomi. A gigice ta taho ita ma Tauhidat ɗin ta tashi da ƙyar daga jikinsa ta nufeta da sauri.

"Oluwatosin!" Abayomi ya daka mata tsawar da ta dakatar dasu su biyun, "idan ki ka ƙara taku ɗaya zuwa wajenta daga yau sai dai ki nemi wani uban bani ba."

"Papa?" Ta ce zuciyarta na harbawa kamar ta ballo mata ƙirji. Haj. Manga da ta ware hannuwa ta rungumeta sai ta yi turus hannuwan suka sauka a jikinta. Tunda take a duniya bata taɓa ganin abinda ya kona mata rai na cin amana makamancin wannan ba. Kunnuwanta neman toshewa suke ga ƙafafunta sunyi mata mugun nauyi. Tana tsaye a wurin wasu zafafan hawaye suka shiga gudu a kumatunta. Idanun Tauhidat na sauka cikin nata kuwa Tauhidat ɗin ta sulale a wurin. Jamal cikin zafin nama ya fincikota daga jikin Papa Abayomi yana ihun kiran sunanta. Kirjinta ya mata nauyi tana jin kamar za ta fita hayyacinta amma a haka ta daka masa tsawa "Jamaluddeen! Sakar masa yarsa."

Ya juyo shi ma kansa hawayen yake yi, "Nanna suma fa ta yi."

"Na ce ka saketa."

Ta juya a hankali cikin ƙunar rai tana tafiya. Bata fita daga falon ba ita ma ta yanke jiki ta faɗi. Jamal ya yi wa Tauhidat kallo ɗaya tana jikin babanta shi ma yana kuka ya isa wurin mahaifiyarsa da sauri. Juyawa ya yi neman taimako ya kula ashe babu kowa a falon sai su kaɗai. Ciccibarta yake son yi amma ko shi ta fi shi tsayi bare kuma jiki. Jijjigata kawai yake yana kiran sunanta cike da tashin hankali.

Alhamdulillah

Mu haɗu a kashi na biyu domin jin yadda za ta kaya.

Taku

BATUL MAMMAN.